JERANGIYAR DAGA HUƊUBOBIN MASALLACIN ANNABI 5



# LITTAFI KAN HALAYE

## DAGA HUƊUBOBIN MASALLACIN ANNABI

**WALLAFAR:**

**Dr. Abdulmuhsin Ɗan Muhammad Alƙasim**
**Liman kuma mai huɗuba a masallacin Annabi**

مترجم بلغة الهوسا

Za'a iya bincika da sauke dukkan littafan babban malamin a wannan linki:

**a-alqasim.com**

# LITTAFI KAN HALAYE DAGA HUƊUBOBIN MASALLACIN ANNABI

**WALLAFAR:**

Dr. Abdulmuhsin Ɗan Muhammad Alƙasim

Liman kuma mai huɗuba a masallacin Annabi

**DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JIN ƘAI**

# GABATARWA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai, yabo da Aminci su tabbata ga Annabin mu Muhammad, da kuma Iyalansa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Amma Ba'adu[1]:**

Yana daga cikin falalolin Allah ga bayinSa, Ya basu nau'o'in ayyukka; domin su samu ƙololuwar Gidajen Aljannah saboda su, kuma daga cikin waɗannan Ibadodin akwai; Ibadar dake tsakanin Bãwa da UbangijinSa, ta: Bauta da Ƙanƙan da kai a gare Shi, da kaɗaita Shi da Bauta, da tabbatar maSa da cikar kamala ta kowacce fuska; ta hanyar tabbatar da SunayenSa da SiffofinSa.

Daga cikin Ibadun akwai waɗanda suke tsakanin Bawa da Hallittu, kuma abunda ya dunƙulesu shine: kyakykyawan hali; ta hanyar kyautatawa, da kamewa daga cutarwa da kuma sakin Fuska.

Kuma domin fito da sashen Ibadar Halaye kyawawa, yasa nayi Huɗubobi akan haka a Massallacin Annabi, sa'annan kuma na waresu na tsara su a cikin wannan Littafin, sai adadinsu ya kai Huɗuba Goma sha uku (13), kuma na saka masa suna: «**Halaye –Kyawawa da munana-; daga Huɗubobin Masallacin Annabi**».

---

(1) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

Allah nake roko Ya amfanar da wannan Littafi, kuma Yasa shi domin neman Fuskarsa ne Mai Karamci kawai.

Yabon Allah da Aminci ya tabbata ga Annabin mu Muhammad da Iyalansa da Sahabbansa baki ɗaya.

**Dr. Abdulmuhsin bin Muhammad Alqãsim**

Limami mai Huɗuba a Massallacin Annabi mai Alfarma.

# HALAYE ABUN YABO

# KIYAYE HARSHE[1]

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrin kawunan mu da kuma munanan ayyukkan mu, wanda Allah Ya shiryar dashi babu mai ɓatar dashi, kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaidawa cewa babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa: lallai Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi Yabo da Aminci mai yawa a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Amma Ba'adu[2]:**

Kuji tsoron Allah –ya ku bayin Allah- haƙiƙanin jin tsoro; domin duk wanda yaji tsoron UbangijinSa lallai ya tsira, kuma duk wanda ya kawar da kai daga ambatonSa lallai ya halaka.

**Ayyuhal Muslimun[3]:**

Ni'imomin Allah ga BayinSa basa ƙirguwa:

---

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a Huɗu ga watan Rajab, Shekara ta Dubu Ɗaya da Ɗari Huɗu da Arba'in da Ɗaya bayan Hijira.

(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

(3) Ya ku musulmai.

﴿ وَمَا بِكُم مِّن نِّعْمَةٍ فَمِنَ ٱللَّهِ ﴾

((**Kuma duk wata Ni'ima dakuke da ita, lallai daga Allah take**)). [Suratul Nahl: 53].

kuma Harshe yana daga cikin Ni'imomi masu girma kuma yana daga cikin tausasan hallittar Allah masu ban-mamaki, Allah Ya gorantawa Bayi Ni'imar Harshe, Yace:

﴿أَلَمْ نَجْعَل لَّهُۥ عَيْنَيْنِ ۝ وَلِسَانًا وَشَفَتَيْنِ﴾

((**Ashe bumu saka masa Idanu guda biyu ba** ⁕ **kuma da Harshe da Leɓuna guda biyu**)). [Suratul Balad: 8-9].

Da Harshe ne ake samun Ilimi, Bayani da Karramawa ga ɗan Adam; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ ٱلرَّحْمَٰنُ ۝ عَلَّمَ ٱلْقُرْءَانَ ۝ خَلَقَ ٱلْإِنسَٰنَ ۝ عَلَّمَهُ ٱلْبَيَانَ﴾

**((Mai Rahama** –Allah- ⁕ **Ya sanar da Alqur'ani** ⁕ **Ya hallicci Mutum** ⁕ **Ya sanar dashi Bayani** –Magana**-)).** [Suratur-Rahmãn: 1-4].

Kuma duk abunda Bawa yake faɗi abun kiyayewa ne a cikin Littafinsa, kuma zai haɗu da UbangijinSa tare dashi; Allah mai Tsarki Ya ce:

﴿ مَّا يَلْفِظُ مِن قَوْلٍ إِلَّا لَدَيْهِ رَقِيبٌ عَتِيدٌ﴾

**((Kuma ba wata Magana da zai furta face a tare dashi akwai** -Mala'iki- **Mai tsaro kuma wanda yake**

**halarce)).** [Suratul Qãf: 18].

Don haka ne, Allah Ya umurci bayinSa da faɗin zance Madai-daici Yace:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَقُولُواْ قَوۡلٗا سَدِيدٗا ﴾

**((Yaku waɗanda sukayi Imani kuji tsoron Allah kuma ku faɗi Magana Madai-daiciya)).** [Suratul Ahzãb:70].

kamar yadda Ya umurce su da faɗin zance mafi daɗi da kyau:

﴿وَقُل لِّعِبَادِي يَقُولُواْ ٱلَّتِي هِيَ أَحۡسَنُۚ﴾

**((Kuma kace da BayiNa su faɗi** –magana- **mafi kyau)).** [Suratul Isrã: 53].

Kuma yana daga cikin wajiban Imani: Kiyaye Harshe sai a wurin faɗin Alkhairi; Annabi -Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- ya ce: «**Duk wanda yayi Imani da Allah da ranar ƙarshe, ya faɗi Alkhairi ko yayi shiru**». [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma Allah Ya yabi bayinSa Muminai saboda kawar da kansu daga yasashiyar Magana [marar amfani] da kuma aiki; Allah Yace:

﴿وَٱلَّذِينَ هُمۡ عَنِ ٱللَّغۡوِ مُعۡرِضُونَ﴾

((**Kuma da waɗanda suke kawar da kai daga yasashiyar magana**)) [Suratul Mu’Minŭn: 3]

Kuma Musulmi shine wanda ya kiyaye Harshensa, kuma kiyaye Harshe yana daga cikin ababen dake banbancewa tsakanin Matsayin bãyi, an tambayi Annabi

–Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- «Shin wane Musulmi ne yafi Alkhairi? Sai yace: **wanda Musulmi suka kuɓuta daga Harshensa da Hannayensa**». [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]. Kuma Aljannah itace sakamakon wanda ya kiyaye Harshensa; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Waye zai bani Lamunin kiyaye abunda yake tsakanin Kuncinsa guda biyu** –Harshensa- **da kuma wanda yake tsakanin Ƙafafunsa guda biyu** -Al'aurarsa-; **ni kuma ina bashi tabbacin Aljannah**». [Bukhari ya ruwaito shi].

Harshe yar ƙaramar Hallitta ce, mai yawan amfani, kuma yakan iya zama mai tsananin cutarwa; wannan yasa Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya nemi tsari daga sharrinsa yace: «**Ya Allah ina neman tsarinKa daga sharrin Harshena**» [Abu dawud ya ruwaito shi].

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yajiyewa Sahabbansa da Al'ummarsa tsoron illar Harshe; Sufyãnu ɗan Abdullahi Al-thaqafi –Allah Ya yarda dashi- yace: «Ya Manzon Allah! meye ne abunda kafi jiye min tsoro akaina? Sai ya riƙi Harshensa, sa'annan yace: **Wannan**» [Tirmizi ne ya ruwaito shi].

Kuma ahaka Sahabbai –Allah Ya yarda dasu- suka kasance suna tsoron sharrin Harshe; wata rana Abubakar –Allah Ya yarda da shi- ya fitar da Harshensa sai yace: «Wannan shine wanda ya jefani wuraren Halak», kuma Ibn Abbas –Allah Ya yarda dasu- ya kasance yana riƙe Harshensa yana cewa: «Kaiconka! Ka faɗi Alkhairi; sai

kasamu Ganima [Riba], ko kayi shiru daga mugun abu; sai kasamu tsira, idan kuma bakayi haka ba, to, lallai kasani cewa zakayi Nadama».

Haɗarin Harshe mai girma ne a Duniya da Lahira; sau nawa ne wata Kalma ta lalatawa wasu mutane Rayuwarsu, Ibn Mas'ud –Allah Ya yarda da shi- ya ce: «Babu abunda yafi buƙatar zama a tsare tsawon lokaci kamar Harshe».

Kuma Magana takan iya halakar da Ma'abocinta har ya haɗu da Allah bashida komai na aiki; Annabi –Tsira da Amincin su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Shin ko kun san waye Matsiyaci?** Sai Sahabbai suka ce: Matsiyaci a cikin mu shine wanda bashida Dirhami kuma bashida wasu kaya –Dukiya-, sai yace: **Haƙiƙanin Matsiyaci daga cikin Al'ummata shine wanda zai zo ranar Ƙiyama da Sallah da Azumi da Zakkah, amma zai zo alhali ya Zagi wannan, yayiwa wannan Ƙazafi, yaci Dukiyar wannan, ya zubar da Jinin wannan, ya Daki wannan; sai a biya wannan daga Ayukkansa na ƙwarai, shima wannan a bashi daga Ayukkansa na ƙwarai, idan Ayukkansa na ƙwarai suka ƙare kafin a gama biyan haƙƙoƙan dake a kansa; sai a ɗauko Ayykkansu na Laifi a ɗora masa, sa'annan sai a jefa shi a cikin Wuta**». [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma «An tambayi Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- akan abunda yake yawan shigar da Mutane cikin Wuta, sai yace: **Baki da Al'aur**». [Tirmizi ya ruwaito shi], kuma yace: «**Lallai Bawa zai iya furta wata Kalma wadda baaiyi tunani akan Matsayinta ba; amma sai ta jefa shi a cikin Wuta zurfin da yafi**

**nisan tsakanin Mafitar Rana da Mafaɗarta**». [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Mafi girman illar Harshe shine: kiran wanin Allah, da kuma sakawa Allah Mai Tsarki Kishiya; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَمَنْ أَضَلُّ مِمَّن يَدْعُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَن لَّا يَسْتَجِيبُ لَهُۥٓ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ وَهُمْ عَن دُعَآئِهِمْ غَٰفِلُونَ﴾

((**Waye yafi ɓacewa sama da wanda yake kiran wanin Allah wanda baya iya karɓa masa har zuwa ranar Alƙiyama kuma alhali su** –ababen kiran- **sun kasance masu gafala daga kiran nasu**)) [Suratul Ahƙãf: 5].

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Duk wanda ya mutu alhali yana kiran wani abun kishiya koma bayan Allah; lallai ya shiga Wuta**» [Bukhari ya ruwaito shi].

Kuma Allah Shine mai yin Ni'ima Shi kaɗai, kuma yana daga cikin Shirka: jingina Ni'imomi zuwa ga waninSa; a cikin Hadisin Qudsiy, Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Allah Ya ce: Wasu daga cikin BayiNa sun wayi gari suna masu Imani daNi wasu kuma suna masu Kafircewa daNi; amma waɗanda suka ce: Anyi mana Ruwa cikin Falalar Allah da RahamarSa; waɗannan sune sukayi Imani daNi kuma suka kafirce da Taurari, amma kuma waɗanda suka ce: Anyi mana Ruwa da nau'i kaza da kaza** –na Taurari-; **waɗannan sun kafirce dani kuma sunyi Imani da Taurari**» [Bukhari da Muslim

suka ruwaito shi].

Kuma neman tsari daga wurin wanin Allah baya ƙarawa Ma'abocinsa komai sai Tsoro da Rauni; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَأَنَّهُۥ كَانَ رِجَالٌ مِّنَ ٱلْإِنسِ يَعُوذُونَ بِرِجَالٍ مِّنَ ٱلْجِنِّ فَزَادُوهُمْ رَهَقًا ﴾

((**Kuma lallai wasu Maza daga cikin Mutane sun kasance suna neman tsari daga wasu Maza daga cikin Aljanu sai suka ƙara masu girman kai**)). [Suratul-Jinn: 6].

Kuma yana daga cikin Shirka a cikin Magana: Yin Rantsuwa da wanin Allah; Annabi –Tsira da Aminci su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Duk wanda yayi Rantsuwa da wanin Allah; haƙiƙa ya kafirta ko yayi Shirka**» [Ahmad ya ruwaito shi], kuma yace: «**Duk wanda yayi Rantsuwa da wani Addini wanda ba Musulunci ba akan Ƙarya kuma da Gangan; lallai shi yana nan kamar yadda ya faɗa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]. Kuma yace: **«Duk wanda yayi Rantsuwa da Amana; lallai baya tare damu**» [Abu dawud ya ruwaito shi].

Kuma Shi Allah Mai Tsarki yanada Kamala sake -ta kowace Fuska-, kuma duk wanda ya raɗawa kansa Sunayen Allah waɗanda Ya kaɗaitu dasu; lallai Allah zai ƙasƙantar dashi; Annabi –Tsira da Aminci su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Lallai mafi ƙasƙancin Suna a wurin Allah shine: Mutumin da zai saka sunan: Sarkin Sarakuna; kuma ba wani Sarki sai Allah**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma dukkan lamari na Allah ne Shi kaɗai, kuma ba'a haɗa ganin damar wani da ganin damar Allah Mai Tsarki ta fuskar dai-daito a cikin Lafazi ko Ma'ana; Annabi –Tsira da Aminci su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Kada kuce: Idan Allah Ya so kuma wane ya so; sai dai kuce: idan Allah Ya so, sa'annan wane ya so**» [Ahmad ya ruwaito shi].

Kuma ita ƙaddara ikon Allah ce, kuma Imani da ita Rukuni ne daga cikin Imani, ba'a cewa: «**Da nayi kaza da kaza da kaza ya faru;... domin ita kalmar danayi tana buɗe ƙofar Shaiɗan**» [Muslim ya ruwaito shi], kuma yin Fushi akan ababen da Allah Ya ƙaddara ta hanyar Magana yana daga cikin al'amuran Jahiliyya, Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Mai yin kururuwa idan akayi Mutuwa idan bata tuba kafin Mutuwarta ba; za'a tasheta a ranar ƙiyama tanada wani Wando mai zafin ƙuna da kuma Rigar ƙazuwa**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma lallai Allah Shi ne yake juyar da Dare da Yini, kuma Yake gudanar dasu, kuma zagin Zamani yana war-ware Imani ko yana raunana shi, Annabi –Tsira da Aminci su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Allah Mai Buwaya da Ɗaukaka Ya ce: Ɗan Adam yana cutar daNi; yana zagin Zamani, kuma Ni ne Zamani; ina juyar da Dare da Yini**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma duk wanda ya munana Zato ga Allah kuma ya yanke ƙauna daga RahamarSa; tabbas ya bijiro da kansa ga Azabar Allah; wani mai yawan Ibada daga cikin Bani

Isrã’ila yace da wani mai Saɓo daga cikinsu: «**Na Rantse da Allah, Allah ba zai gafartawa wane ba! Sai Allah Maɗaukaki Yace: Waye yake yi Mini Shi-shigi yana faɗin cewa bazan taɓa yafewa wane ba, to lallai Ni na yafewa wane, kuma na rusa Aikinka**» [Muslim ya ruwaito shi] Abu Hurairah –Allah Ya yarda dashi- yace: «Ya furta Kalmar data halakar da duniyarsa da lahirarsa» kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Idan Mutum yace: Mutane sun Halaka; lallai shi ne wanda yafi su Halaka**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma Allah Mai Tsarki Ya keɓanta da sanin Ilimin Gaibi –abunda yake ɓoye-; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿قُل لَّا يَعۡلَمُ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ ٱلۡغَيۡبَ إِلَّا ٱللَّهُۚ﴾

((**Kace babu wanda yasan Gaibi a cikin Sammai da Ƙasa, face Allah**)) [Suratul Naml: 65].

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Duk wanda yaje wurin Mai Tsibbu ya tambaye shi wani abu; ba za’a karɓi Sallarsa ba ta Kwana Arba’in**» [Muslim ya ruwaito shi], kuma yace: «**Duk wanda yaje wurin Boka ko Mai Tsibbu kuma ya gaskata abunda yake faɗi; Tabbas ya kafircewa abunda aka saukarwa Muhammad Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi**» [Ahmad ya ruwaito shi].

Kuma daga cikin mafi girman ababen da aka haramta akwai: Yin Magana a cikin abunda ya shafi Allah ba tare da Ilimi ba; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿قُلۡ إِنَّمَا حَرَّمَ رَبِّيَ ٱلۡفَوَٰحِشَ مَا ظَهَرَ مِنۡهَا وَمَا بَطَنَ وَٱلۡإِثۡمَ وَٱلۡبَغۡيَ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَأَن تُشۡرِكُواْ بِٱللَّهِ مَا لَمۡ يُنَزِّلۡ بِهِۦ سُلۡطَٰنٗا وَأَن تَقُولُواْ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ﴾

((**Kace abunda Ubangijina Ya haramta kawai shine Alfasha: abunda ya bayyana nata da wanda ya ɓoyu, da Zunubi da Zalunci batareda haƙƙi ba kuma da kuyi Shirka da Allah ga abunda bai sauko da wani dalili ba akansa kuma da ku faɗi abunda baku sani ba gameda Allah**)). [Suratul Al'a'arãf: 33].

Kuma yin Izgili da Addini yana fitar da Ma'abocinsa daga cikin Addinin;

Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَلَئِن سَأَلۡتَهُمۡ لَيَقُولُنَّ إِنَّمَا كُنَّا نَخُوضُ وَنَلۡعَبُۚ قُلۡ أَبِٱللَّهِ وَءَايَٰتِهِۦ وَرَسُولِهِۦ كُنتُمۡ تَسۡتَهۡزِءُونَ ❁ لَا تَعۡتَذِرُواْ قَدۡ كَفَرۡتُم بَعۡدَ إِيمَٰنِكُمۡ﴾

((**Kace yanzu da Allah da AyoyinSa da ManzonSa kuke yin Izigili ❁ kada ku kawo wani Uzuri, tabbas kun kafirta bayan Imaninku**)). [Suratut Taubah: 65-66].

Kuma Ƙarya tana daga cikin Zunubai masu muni da Miyagun Aibobi, kuma itace asalin kowane Sharri, kuma Alama ce daga cikin Alamomin Munafurci, Annabi – Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Kuma lallai ita Ƙarya tana shiryarwa zuwa ga Fajirci, kuma lallai shi Fajirci yana shiriyarwa zuwa ga Wuta, kuma Mutum ba zai gushe yana Ƙarya ba yana kirdadon yin Ƙarya har sai an rubuta shi**

**Maƙaryaci a wurin Allah**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

kuma mafi munin Ƙarya itace wacce akayi akan Allah da ManzonSa; Allah Mai Tsarki Ya ce:

﴿وَيَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ تَرَى ٱلَّذِينَ كَذَبُوا۟ عَلَى ٱللَّهِ وُجُوهُهُم مُّسْوَدَّةٌ ۚ أَلَيْسَ فِى جَهَنَّمَ مَثْوًى لِّلْمُتَكَبِّرِينَ﴾

((**Kuma a ranar Ƙiyama zakaga waɗanda sukayiwa Allah Ƙarya Fuskokinsu sunyi Baƙi, ashe babu Mazauni a cikin Jahannama ga masu girman kai** !?)). [Suratul Zumar: 60].

kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Duk wanda yayi min Ƙarya da gan-gan; to ya tanadi Mazauninsa a cikin Wuta**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma duk wanda yayi Rantsuwa akan Ƙarya alhali kuma yana sane game da wani abu wanda ya faru; lallai Rantsuwarsa mai nutsarwa ce, tana nutsar da Ma'abocinta a cikin Wuta, Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Duk wanda yayi Rantsuwa akan Dukiyar wani Mutum Musulmi ba tareda Haƙƙi ba; zai haɗu da Allah alhali Yana mai Fushi dashi**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma daga cikin Ƙarya akwai: Ƙarya a cikin Nasaba; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Babu wani Mutum da zai jingina zuwa ga wanda ba Mahaifinsa ba alhali yana sane da hakan, face sai ya kafirta, kuma duk wanda ya jingina zuwa ga wasu Mutane alhali bashida wata Nasaba zuwa**

**garesu; to ya tanadi Mazauninsa a cikin Wuta**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma daga cikin Manyan Zunubai akwai: Shaidar Zur; Annabi –Tsira da Aminci su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Ashe bana baku labarin mafi girman manyan Zunubai ba**? –ya tambayesu har sau uku-, sai sukace: Eh, ka bamu labari ya Manzon Allah! sai yace: **Shirka da Allah, da Saɓawa iyaye,** sai ya zauna alhali ya kasance a kishingiɗe, sai yace: **Ku saurara, da Maganar Zur**, bai gushe yana mai-maita ta ba har sai da mukace: da yayi saurara haka» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yace: «**Komai na Musulmi akan Musulmi Haramun ne; Jininsa da Dukiyarsa da Mutuncinsa**» [Muslim ya ruwaito shi], kuma yace: «**Yana daga cikin Manyan Zunubai Mutum ya zagi Mahaifansa**, sai Sahabbai suka ce: ya Manzon Allah! ashe Mutum zai iya zagin Mahaifansa? Sai yace: **Na'am, Mutum ya zagi Mahifin wani Mutum, sai shima ya zagi Mahaifinsa, kuma ya zagi Mahaifiyarsa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma daga cikin ababe masu halakarwa akwai: yin Ƙazafi ga Mata masu kamun kai, masu kawar da kai daga alfasha kuma Muminai; Allah mai Buwaya da Ɗaukaka Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ يَرۡمُونَ ٱلۡمُحۡصَنَٰتِ ٱلۡغَٰفِلَٰتِ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ لُعِنُواْ فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِ وَلَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ﴾

**((Lallai waɗannan da suke jifar Mata masu kamun kai masu kawar da kai daga alfasha, Muminai, an tsine masu a cikin Duniya da Lahira kuma sunada wata Azaba mai Girma)).** [Suratu Al-Nŭr: 23].

Kuma Ƙiren Ƙarya: shine jifar wanda yake wankakke ne da abunda bai yi ba; Allah mai Buwaya da Ɗaukaka Ya ce:

﴿وَمَن يَكۡسِبۡ خَطِيٓـَٔةً أَوۡ إِثۡمٗا ثُمَّ يَرۡمِ بِهِۦ بَرِيٓـٔٗا فَقَدِ ٱحۡتَمَلَ بُهۡتَٰنٗا وَإِثۡمٗا مُّبِينٗا﴾

((**Kuma duk wanda ya aikata Laifi ko Zunubi sa'annan kuma ya jefi wanda bai aikata ba dashi, haƙiƙa ya ɗauki ƙiren-ƙarya da Zunubi bayyananne**)). [Suratu Al-Nisa'i: 112].

Kuma Giba itace: «**Ambatar ɗan uwanka da abunda baya so**» [Muslim ya ruwaito shi], kuma tana daga cikin manyan Zunubai; Allah Maɗaukaki ya ce:

﴿ وَلَا يَغۡتَب بَّعۡضُكُم بَعۡضًاۚ أَيُحِبُّ أَحَدُكُمۡ أَن يَأۡكُلَ لَحۡمَ أَخِيهِ مَيۡتٗا ﴾

**((Kuma kada sashenku yayi Gibar sashe, shin ɗayanku yana son yaci naman ɗan uwansa yana matacce)).** [Suratul Hujurãt: 12].

Ibn Abbas –Allah Ya yarda da su- ya ce: «Allah Ya haramta Giba kamar yadda Ya haramta Mushe».

Kuma daga cikin illar Harshe akwai: yawo da Gulma tsakanin Hallittu: Allah Ya ce:

﴿وَلَا تُطِعۡ كُلَّ حَلَّافٖ مَّهِينٍ ۞ هَمَّازٖ مَّشَّآءِۭ بِنَمِيمٖ﴾

**((Kuma kada kabi kowane mai yawan Rantsuwa**

**wulaƙantacce ⁕ mai Zunɗe mai yawo da Gulma))**. [Suratul Qalam: 10-11].

kuma Annabi –Tsira da Aminci su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Magulmaci baya shiga Aljannah**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Yahya bin Abi Katheer –Allah ya jiƙansa- yace: «A cikin Sa’a ɗaya Magulmaci yana ɓata abunda mai Sihiri bai ɓata ba a cikin Shekara ɗaya».

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Zagin Musulmi Fasiƙanci ne**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi] kuma yace: «**Mutum ba zai jefi wani Mutum da Fasiƙanci ba, kuma ba zai jefe shi da Kafirci ba; face sai ya dawo akansa idan abokinsa** -wanda ya jefa- **ba haka yake ba**» [Bukhari ya ruwaito shi]. Kuma yace: «**Tsinewa Mumini kamar kashe shi ne**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma duk wanda ya tsinewa wani abu wanda bai cancanta a tsine masa ba, tsinuwar zata dawo akansa; kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Mumini ba mai yawan suka ne ba, kuma ba mai yawan tsinuwa ne ba**» [Ahmad ya ruwaito shi]; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Lallai masu yawan tsinuwa basa zama Shaidu, kuma basa zama masu ceto ranar Ƙiyama**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma yin Izgili da Hallittun Allah yana daga cikin nau’in girman kai, kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Ya ishi Mutum**

**daga Sharri ya wulaƙanta ɗan uwansa Musulmi**» [Muslim ya ruwaito shi].

Allah Mai Tsarki Ya ce:

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا يَسۡخَرۡ قَوۡمٞ مِّن قَوۡمٍ عَسَىٰٓ أَن يَكُونُواْ خَيۡرٗا مِّنۡهُمۡ وَلَا نِسَآءٞ مِّن نِّسَآءٍ عَسَىٰٓ أَن يَكُنَّ خَيۡرٗا مِّنۡهُنَّۖ وَلَا تَلۡمِزُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ وَلَا تَنَابَزُواْ بِٱلۡأَلۡقَٰبِۖ بِئۡسَ ٱلِٱسۡمُ ٱلۡفُسُوقُ بَعۡدَ ٱلۡإِيمَٰنِۚ وَمَن لَّمۡ يَتُبۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴾

**((Yaku waɗanda sukayi Imani kada wasu Mutane su yiwa wasu Mutane Izgili, mai yiyuwa ne** –waɗanda akeyiwa Izgilin- **su kasance mafi Alkhairi akansu** –masu Izgilin-**, kuma kada wasu Mata suyi Izgili ga wasu Mata mai yiyuwa ne su kasance sunfi su Alkhairi, kuma kada ku aibata kanku kuma kada ku jefi juna da miyagun Laƙubba, Tir da sunan Fasiƙanci bayan Imani, kuma duk wanda bai tuba ba lallai waɗannan sune Azzalumai)). [Suratul Hujurãt: 11].**

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Yana daga cikin al'amrin Jahiliya: Alfahari da dangantaka, da kuma suka a cikin Nasaba**» [Ɗhabarãni ya ruwaito shi].

kuma kamar yadda Musulunci yayi hani daga zagin Rayayyu; haka nan kuma ya haramta zagin Matattu; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Kada ku zagi Matattu; domin tabbas su sun gabata ga abunda suka aikata**». [Bukhari ya ruwaito shi], Musulunci yayi hani daga zagin Iska, da Zazzaɓi da Dabbobi.

Kuma duk wanda ya bayyanar da mugun abu, lallai ya bijiro ga yaye suturtawar da Allah yayi masa; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Dukkan Al'ummata abar yiwa Afuwa ce sai masu Bayyanawa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Musulmi yana neman yardar Allah ne da ciyarwar da yake yi, kuma yin gorin Sadaka yana ɓata ta, kuma Allah baya yiwa mai yawan Gori Magana, kuma baya kallonsa kuma baya tsarkake shi ranar Ƙiyama.

Kuma an hana roƙon Hallittu; Annabi –Tsira da Aminci su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Roƙo ba zai gushe tareda ɗayanku ba har sai ya haɗu da Allah babu tsokar nama a Fuskarsa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma duk wanda yayi jayayya akan ɓarna Allah zai ƙishi; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yace: «**Mafi ƙin Mutane a wurin Allah shine: Mai tsananin Husuma da dogewa akai**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma gidaje suna samun Aminci ne idan aka ɓoye Sirrinsu; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Lallai daga cikin mafi sharrin matsayi daga cikin Mutane a wurin Allah ranar Ƙiyama akwai: Mutunen da zai kusanci Matarsa kuma itama ta kusance shi, sa'annan kuma yaje yana yaɗa Sirrinta**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma yawan surutu marar Amfani yana jawo zamewar ƙafa, kuma Allah Yaƙi a garemu: «**Ance, Yace**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi] kuma

«**Daga cikin kyawun Musuluncin Mutum akwai: barinsa ga abunda bai shafe shi ba**» [Ahmad ya ruwaito shi], Sahal bin Abdullahi –Allah Ya jiƙansa- yace: «Wanda yayi Magana a cikin abunda bai shafe shi ba; za'a haramta masa Gaskiya», Al-Nawawe –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Yana da kyau ga kowane Baligi mai hankali ya kiyaye Harshensa daga kowace Magana; sai Maganar da Mas'laharta take bayyanne».

**Waba'adu Ayyuhal Muslimŭn(1):**

Lallai kiyaye Harshe da kula dashi shine asalin Alkhairi dukkan sa, kuma duk wanda ya mallaki Harshensa haƙiƙa ya mallaki al'amarinsa kuma ya dai-daita shi, kuma «**Duk wanda yayi shiru; ya tsira**» [Ahmad ya ruwaito shi], kuma Bawa ba zai gushe yana cikin Aminci ba idan yayi shiru, amma yana yin Magana za'a rubuta Lada a gare shi ko Laifi akansa. Kuma duk wanda ya ƙirga Maganarsa daga cikin aikinsa; lallai zai taƙaita Magana a cikin abunda bai shafe shi ba.

**Ina neman tsarin Allah daga Shaiɗan Jefaffe.**

﴿لَّا خَيْرَ فِي كَثِيرٍ مِّن نَّجْوَاهُمْ إِلَّا مَنْ أَمَرَ بِصَدَقَةٍ أَوْ مَعْرُوفٍ أَوْ إِصْلَاحٍ بَيْنَ ٱلنَّاسِ ۚ وَمَن يَفْعَلْ ذَٰلِكَ ٱبْتِغَآءَ مَرْضَاتِ ٱللَّهِ فَسَوْفَ نُؤْتِيهِ أَجْرًا عَظِيمًا﴾

((**Babu Alkhairi a cikin mafi yawan tattaunawarsu**)) wato: Maganarsu ((**sai wanda yayi umurni da yin Sadaka ko Aiki mai kyau ko Sulhu tskanin Mutane, kuma duk wanda yayi haka don**

---

(1) Bayan haka, Yaku Musulmi.

**neman yardar Allah, da sannu zamu bashi sakamako mai girma**)). [Suratul-Nisa'i: 114].

Allah Yayi min Albarka tare daku a cikin Alqur'ani mai Girma..

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarSa da kuma Ni'imominSa, kuma ina shaida cewa lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya; don girmamawa ga Sha'aninSa, kuma ina shaida cewa lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, yabon Allah ya tabbata a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa tareda Aminci mai ƙaruwa.

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Ƙofofin Alkhairi sunada yawa, kuma duk wanda ya mallaki Harshensa lallai ya mallakesu baki ɗaya; Annabi –Tsira da Aminci su tabbatta a gare shi- ya ce da Mu'az –Allah Ya yarda dashi-: «**Ashe bana baka labarin abunda yake mallakar wannan dukansa ba?** Mu'az yace: Eh, Ya Annabin Allah! sai ya riƙi Harshensa yace: **Ka kame wannan daga kanka,** sai nace: Ya Annabin Allah! ashe za'a kama mu da abunda muke Magana dashi, sai yace: **Mahaifiyarka tayi ɓarinka! Shin akwai abunda yake jefa mutane a cikin Wuta ta fuskarsu** ko yace: **akan karan Hancinsu- face abunda Harsunansu suka girba!** [Ahmad ya ruwaito shi].

Kuma matsayin Mutum yana bayyana ne da ƙananan Hallittu biyu a jikinsa: Zuciyarsa da Harshensa, kuma da gyaruwarsu ko lalacewarsu ne Mutm yake kasancewa na gari ko lalatacce, kuma Imanin Bawa ba zai tsayu ba har sai Zuciyarsa ta dai-daita, kuma Zuciyarsa bazata dai-

(1) Yaku Musulmi.

daita ba sai idan Harshensa ya dai-daita.

Kuma Zukata kamar Tukwane ne; suna tafasa ne da abunda yake a cikin su, kuma Harsunansu sune suke ɗebo abunda yake cikinsu –Zukata-, idan Mutum yayi Magana lallai Harshensa zai bayyana maka abunda yake cikin Zuciyarsa; don haka, ba ƙudirce Alkhairi a ɓoye sai Harshenka ya fitar da Alkhairi.

Sa'annan kuma kusani, lallai Allah Ya umurce ku da yin Salati da Sallama ga AnnabinSa...

# GASKIYA[1]

Godiya ta tabbata ga Allah wanda Ya hallicci Mutum daga Lãka, kuma a cikin ikonSa Ya saka shi a cikin wani Mazauni mai Natsuwa, ina godewa Allah Maɗaukaki da irin godiyar masu godewa kan Ni'imomi.

Kuma ina shaida lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, Shine Sarkin gaskiya Bayyananne.

Kuma ina shaida lallai Annabin mu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, mai gaskiya Amintacce, mafi gaskiyar Mutane a cikin Magana, kuma mafi tsarkake Niyya a cikin Aiki, kuma wanda yafisu cika Alƙawari, Allah Yayi yabo a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa waɗanda sune Fitilun Shiriya kuma Jagororin Addini.

**Ammab Ba'adu[2]:**

Kuji tsoron Allah -yaku bayin Allah- haƙiƙanin jin tsoro; domin lallai tsoron Allah shine Igiya mafi ƙwari, kuma shine Wasiyar Allah ga Mutanen Farko dana Ƙarshe, kuma itace Hanyar Tsira ranar Sakamako.

---

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a goma sha shida ga Rabi'ul Awwal, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da goma sha tara bayan Hijira.

(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Haƙiƙa Allah Ya hallicci Mutum daga Rauni, kuma Ya samar dashi daga rashi, kuma Ya sanar dashi bayan Jahilici, kuma Ya girmama shi tsakanin Hallittu, Ya keɓance shi da Magana da Bayani, da Lafazi ne Mutum yake bayyana buƙatarsa, kuma dashi ne yake fito da abunda Zuciyarsa ta ɓoye, kuma dashi ne Ɗaukaka, ƙasƙanci da Himma da girma suke bayyana, duk wanda yayi maganar gaskiya dashi zai samu ɗaukaka da tsira, kuma duk wanda yayi lalatartar Magana dashi zai halaka kuma zai taɓe.

Wannan kenan, Kuma Haƙiƙa, daga cikin mafi karamcin siffoffin Mutumtaka da mafi girman falalolin halaye akwai: abunda Mutum yake magana dashi na gaskiya; wannan shine ginshiƙin rayuwa mai karamci, kuma shine mafi muhimmancin ginshiƙai a gina Al'umma da samun cin nasarar Jama'a.

Allah Yayi umurni da yin ƙawa da ita [gaskiya], kuma Ya sanyata hali ne na waɗanda suke ɗauke da WahayinSa kuma masu isar da ManzancinSa; Allah Yana cewa gameda BadaɗayinSa Ibrahim Amincin ya tabbatta a gare shi:

﴿وَٱذۡكُرۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ إِبۡرَٰهِيمَۚ إِنَّهُۥ كَانَ صِدِّيقٗا نَّبِيًّا﴾

((**Kuma ka ambato Ibrahim a cikin Littafi, lallai shi ya kasance Mai gaskatawa kuma Annabi**)) [Suratu Maryam: 41].

---

(1) Yaku Musulmi.

kuma Allah Yana cewa gameda Isma’el -Aminci ya tabbatta a gare shi-:

﴿ وَٱذۡكُرۡ فِي ٱلۡكِتَٰبِ إِسۡمَٰعِيلَۚ إِنَّهُۥ كَانَ صَادِقَ ٱلۡوَعۡدِ وَكَانَ رَسُولٗا نَّبِيّٗا ﴾

((**Kuma ka ambato Isma’el a cikin Littafi, lallai shi ya kasance mai gaskata Alƙawari kuma ya kasance Manzo Annabi**)). [Suratu Maryam: 54].

Mazaje abun koyi suna yin ƙawa da Gaskiya, haka nan kuma masu cika Alƙawari daga cikin Muminai waɗanda Ruhinsu ya tsaftata daga gurɓata, kuma Zukatansu suka tsarkaka daga tsatsa, kuma Rayukansu suka ɗaukaka daga kowane ƙasƙantaccen abu wulaƙantacce.

Gaskiya Alama ce dake nuni zuwa ga cin nasarar Al’umma da tsaftar abunda take ɗauke dashi a ɓoye, kuma Maɓuɓɓugar Alkhairi ce gareta -Al’umma-; Abin Zaɓi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yana cewa: «**Na umurceku da Gaskiya; domin ita Gaskiya tana shiriyarwa zuwa ga Ayukkan Ɗã’a, kuma su Ayukkan dã’a suna shiryarwa zuwa Aljannah, kuma Bawa ba zai gushe ba yana Gaskiya kuma yana kirdadon yin Gaskiya ba har sai an rubuta shi a wurin Allah mai Gaskiya**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Gaskiya itace mai rarrabewa idan masu Husuma sukayi tsanani, kuma itace mai shaida idan Haƙƙoƙi suka tozarta, kuma itace Fitila idan Al’ammura suka yi Duhu kuma aka kasa gane dai-dai.

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Lallai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya kwaɗaitar akan Gaskiya; domin itace farkon ɗabi'u, kuma itace mai kira zuwa gare su, kuma ita Alama ce mai nuni zuwa ga ɗaukakar wanda ya siffantu da ita, da gaskiya ce Bawa yake kaiwa zuwa ga Matakan Mutanen ƙwarai, kuma da itace ake samun tsira daga dukkan Sharrori, kamar yadda Albarka take tare da ita a koyaushe.

Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yana cewa «**Masu saye da sayarwa biyu sunada zaɓi kafin su rabu, idan suka yi Gaskiya kuma suka bayyana komai; za'a saka masu Albarka a cikin cinikinsu, idan kuma sukayi Ƙarya kuma suka ɓoye; za'a cire Albarkar kasuwancin su**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]; don haka ne, bazaka samu mai yin Gaskiya a cikin Mu'amalarsa ba face sai kasamu Arzikinsa mai yawa ne, kuma Rayuwarsa mai daɗi ce, kuma zaka same shi ya taka Matsayin ɗaukaka da Girma.

Maƙiyi da Aboki suna samun Natsuwa ga Maganar Mai Gaskiya, kuma abun amicewa ne akan Dukiyoyi da Haƙƙoƙi da Sirrori, kuma duk lokacin daya samu Tuntuɓe ko Kuskure, gaskiyarsa mai Ceto ce karɓaɓɓe, amma Maƙaryaci ba'a amince masa koda akan ƙwayar Zarrah ce, kuma koda wani lokaci za'a iya tsammanin yin gaskiyarsa baza'a saurara ba!

Ashe baka ga Maganar Allah Mai Buwaya da

(1) Yaku Musulmi.

Ɗaukaka ba gameda ƴan uwan Annabi Yusuf a lokacin da suka cema Mahaifinsu:

﴿ ٱرْجِعُوٓا۟ إِلَىٰٓ أَبِيكُمْ فَقُولُوا۟ يَٰٓأَبَانَآ إِنَّ ٱبْنَكَ سَرَقَ وَمَا شَهِدْنَآ إِلَّا بِمَا عَلِمْنَا وَمَا كُنَّا لِلْغَيْبِ حَٰفِظِينَ ❁ وَسْـَٔلِ ٱلْقَرْيَةَ ٱلَّتِى كُنَّا فِيهَا وَٱلْعِيرَ ٱلَّتِىٓ أَقْبَلْنَا فِيهَا ۖ وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَ ❁ قَالَ بَلْ سَوَّلَتْ لَكُمْ أَنفُسُكُمْ أَمْرًا ۖ فَصَبْرٌ جَمِيلٌ ۖ عَسَى ٱللَّهُ أَن يَأْتِيَنِى بِهِمْ جَمِيعًا ﴾

**((Ku koma ga Mahaifinku kuce: Ya Baban mu lallai ɗanka yayi Sata, kuma mu bama shaida sai akan abunda muka sani kuma mu bamu kasance masanan Gaibi ba ❁ kuma ka tambayi Alƙaryar damuka kasance a cikinta da Ãyarin damuka zo a cikinsa, kuma lalle mu tabbas masu Gaskiya ne ❁ Ya ce: Ã'a, Zukatanku sun ƙawãta muku wani al'amari. Sai dai Haƙuri mai kyawu, akwai tsammanin Allah yazo min da su baki ɗaya** –Yusuf da ɗan uwansa-**))** [Suratu Yusuf 81-83].

Wannan gaskiyar tasu Ƙaryarsu ta farko ta ɓata ta, a lokacin dasuka ce game da Yusuf:

﴿فَأَكَلَهُ ٱلذِّئْبُ ۖ﴾

((**Sai Ker-keci ya cinye shi**)) [Suratu Yusuf: 17].

Wajibi ne Musulmi yasan matsayinsa a Rayuwa, kuma ya gane matsayinsa a Duniya, kuma yayi Halayen Ma'abota Girma; ya faɗi gaskiya idan ya bada Labari, ya zamo na ƙwarai idan yayi Mu'amala , kuma ya mayar da

Amana idan aka amince masa, kuma ya cika Alƙawari idan ya ɗauka.

Kuma lallai ƙarancin Gaskiya da yawan Ƙarya cuta ce, idan ta yaɗu tsakanin Mutane zata ƙarya ginshiƙan Amincinsa, kuma ta rushe asalin kafuwarsa, kuma zata canza Amincin ɗaya-ɗayan Mutanensa zuwa tsoro, kuma ta canza nasararsu zuwa taɓewa.

Kuma Rayuwa a cikin Jama'ar da ɗaya-ɗayan jama'ar suke mu'amala da Ƙarya lallai Rayuwa ce mai cike da Damuwa.

Lallai samun ci-gaban Jama'ar Musulmi, da walwalarsa da Amincinsa da Natsuwar ɗaya-ɗayan Mutanensa; dukan wannan ya jingina ne ga yadda gaskiya ta yaɗu tsakanin ɗaya-ɗayan Mutanen.

Tabbas, Imani da zallar Rayuwa mai duhu ya rinjayi wasu sashen Musulmi a yau, har ya manta matsayinsa a cikin wannan rayuwar, kuma suka nisantar da kansu daga Hikimar da aka hallicce su don ita, ya doge akan Rayuwa abar ƙi, kuma ya ɗabi'anta da kansa da ɗabi'a mai Muni; don kwaɗayin wasu Buruka dasuke tunani ne na Ƙarya.

Tabbas, Alƙur'ani mai girma yayi inkari ga wasu Mutane binsu bayan tsammani [zato] na Ƙarya wanda ya cika hankalinsu da tastuniyoyin ƙarya, wanda kuma ya lalata Rayuwarsu ta yanzu data gaba da ƙare-rayi; Allah Maɗaukai Ya ce:

﴿وَمَا لَهُم بِهِۦ مِنْ عِلْمٍۖ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّۖ وَإِنَّ ٱلظَّنَّ لَا يُغْنِي مِنَ ٱلْحَقِّ شَيْـًٔا﴾

**((Kuma basu da wani ilimi game da shi, basa bin**

**komai sai zato kuma lallai zato baya amfanar da komai daga gaskiya**)). [Suratul Najm: 28].

Lallai shaidar mai gaskiya ɗã'a ce, kuma Hukuncinsa Adalci ne, kuma Mu'amalarsa Amfani ce, duk wanda yayi Gaskiya a cikin aikinsa zai nisanci Riya da Jiyarwa acikin; Sallarsa da Zakkarsa da Azuminsa da Hajjinsa da Iliminsa da kiransa ga Allah Shi kaɗai bashida abokin tarayya, baya nufin Cuta ko Yaudara a cikin kyautatawarsa, kuma baya neman Sakamako ko Godiya daga wani ɗaya daga cikin Hallittu, Gaskiyarsa a cikin Magan-ganunsa da Ayukkansa yana dai-dai da Zahirinsa da abunda yake faɗa, kuma Ayukansa suna gaskata Maganganunsa.

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Lallai Allah Ya umurci dukkan tawagun dake cikin Jama'a da yin gaskiya tareda banabancin Sanayyarsu da Iliminsu; Malamai –Magadan Annabawa ne a cikin isar da Addini- sune abun koyi na ƙwarai a cikin kirdadon gaskiya a cikin Magan-ganunsu da Ayyukansu, suna aiki da abunda suke ɗauke dashi na Ilimi da abunda suke ciratowa daga addini:

﴿وَلَٰكِن كُونُواْ رَبَّٰنِيِّـۧنَ بِمَا كُنتُمۡ تُعَلِّمُونَ ٱلۡكِتَٰبَ وَبِمَا كُنتُمۡ تَدۡرُسُونَ﴾

((**Sai dai ku sakance Malamai masu renon mutane da ƙananan Ilimi kafin Manya saboda abunda kuka kasance kuna karantarwa na Littafi da kuma abunda kuka kasance kuna koyo**)). [Suratu Ãli Imrãn: 79].

---

(1) Yaku Musulmi

Kuma Ɗan kasuwa mai fatan samun Rîba mai Albarka a cikin kasuwancinsa; ya zama dole akansa yayi ƙoƙarin yin gaskiya, kada ya tallatta Hajarsa da Ƙarya da Rantsuwowin Fajirci [na Ƙarya]; domin yin hakan yana ɓãta nema kuma yana tafiyar da Albarka Rîba, Annabi – Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yana cewa: «**Lallai za'a tada ƴan kasuwa a ranar Alƙiyama a matsayin Fajirai; sai wanda yaji tsoron Allah yayi Ɗã'a kuma yayi Gaskiya**» [Ibn Mãjah ya ruwaito shi], Fajircinsu ya samo Asali ne daga yawan Ƙaryarsu «**Kuma ita ƙarya tana shiriyarwa zuwa ga Fajirci, kuma lallai Fajirci yana shiriyarwa zuwa ga Wuta**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma ƴan jinga [Ma'aikata] tareda banbancin mastayinsu da nau'o'in ayukkansu da muƙamansu; wajibi ne su yi ƙoƙarin kirdadon Gaskiya, kada su ƙiyas'ta abunda Zahiri yana ƙaryata shi kuma yanayi baya gaskata shi; kuma duk lokacin da Himma ta ɗaukaka, tasiri ya Faɗaɗa kuma nauyi ya yawaita, a wannan lokacin girman wajibcin yin Gaskiya yana ƙara ƙarfi «**Ku saurara! dukkan ku masu kiwo ne, kuma dukkan ku abun tambaya ne akan abunda aka bashi kiyo**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Lallai riƙo da Gaskiya a cikin kowane Sha'ani, da kuma ƙoƙarin yinta a cikin kowane Al'amari, da komawa zuwa gareta a cikin kowane Hukunci; ginshiƙi ne matabbaci a cikin halayyar Musulmi; domin gaskiya itace ginshiƙin Imani, kuma Ƙarya itace ginshiƙin Munafurci, kuma tabbas, Allah Mai Tsarki Ya bada labari cewa ba abunda zai amfani Bawa kuma ba abunda

zai tsiratar dashi daga Azabar Allah a ranar Ƙiyama sai gaskiyarsa; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ هَٰذَا يَوۡمُ يَنفَعُ ٱلصَّٰدِقِينَ صِدۡقُهُمۡۚ ﴾

((**Wannan shine yinin da gaskiyar masu Gaskiya take amfanin su**). [Suratul Mã'idah: 119].

Gaskiya a cikin Magana, Gaskiya a cikin Nufi da Niyyah, da Gaskiya a cikin Aiki, da Gaskiya a cikin Mu'amaloli.

**Ayyuhal Muslimŭn(1):**

Haƙiƙa, Allah Ya umurci ManzonSa –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- da ya roƙe Shi Ya saka Mashigarsa da Mafitarsa akan Gaskiya Allah Ya ce:

﴿ وَقُل رَّبِّ أَدۡخِلۡنِي مُدۡخَلَ صِدۡقٖ وَأَخۡرِجۡنِي مُخۡرَجَ صِدۡقٖ وَٱجۡعَل لِّي مِن لَّدُنكَ سُلۡطَٰنٗا نَّصِيرٗا ﴾

((**Kace Ya Ubangiji Ka shigar dani Mashiga ta Gaskiya kuma Ka fitar dani Mafita ta Gaskiya kuma Ka sanya min wata Hujja mai taimako daga wurinKa**)). [Suratu Al-Isarã'i: 80].

Kuma Allah Ya bada labarin BadaɗayinSa: Ibrahim -Aminci ya tabbata a gare shi-:

﴿ وَٱجۡعَل لِّي لِسَانَ صِدۡقٖ فِي ٱلۡأٓخِرِينَ ﴾

((**Kuma Kasa a gareni yabo mai kyau** -na Gaskiya- **a cikin Mutanen Ƙarshe**)) [Suratul

(1) Yaku Musulmi.

Shu’arã’i: 84].

Kuma Allah Ya yiwa BayinSa Bushara da faɗarSa:

﴿ وَبَشِّرِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَنَّ لَهُمۡ قَدَمَ صِدۡقٍ عِندَ رَبِّهِمۡۗ ﴾

((**Kuma kayi Bushara ga waɗanda sukayi Imani lallai sunada abin gabatarwa na Gaskiya a wurin Ubangijinsu**)) [Suratu Yunus: 2].

Kuma Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ فِي جَنَّٰتٖ وَنَهَرٖ ۞ فِي مَقۡعَدِ صِدۡقٍ عِندَ مَلِيكٖ مُّقۡتَدِرِۭ﴾

((**Lallai masu tsoron Allah suna cikin Aljannah da koguna ۞ a cikin Mazauni na gaskiya, wurin Sarki Mamallakin komai Mai ikon yin komai**)) [Suratul Qamar: 55].

Waɗannan ababe ne guda biyar: Mashiga, Mafita, Harshe, abunda aka gabatar, da kuma Mazaunin gaskiya; kuma haƙiƙanin waɗannan ababe baki ɗaya itace; Gakiya tabbatacciya wacce take sade da Allah, kuma mai kaiwa zuwa ga Allah, shine abunda yake na Allah kuma don Allah ne daga cikin Maganganu da Ayukka.

Kuma akan wannan Misalin Madai-daici ne Jama’ar farko da Magabatan ƙwarai –Allah Ya yarda dasu baki ɗaya- suka kasance akai, kuma suka haskaka Duhu da gaskiyarsu, kuma suka kasance jagorori ga Al’umma.

Ga Sahabi Ka’ab ɗan Mãlik –Allah Ya yarda dashi- a lokacin da yayi gaskiya gameda sababin dayasa bai fita yaƙin Tabuk ba, kuma ya kasance cikin Mutane guda uku da aka jinkirta karɓar Tubar su, har saida Ƙasa tayi

musu ƙunci duk faɗinta, kuma Rayukansu suka musu ƙunci, amma daga ƙarshe sai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yace masa: «**Kayi Bushara da mafi girman rana mai Alkhairi a gareka tun lokacin da Mahifiyarka ta haife ka!** Sai yace: Daga wurinka ne Ya Manzon Allah ko daga wurin Allah? sai Annabi yace: **A'a, daga dai wurin Allah,** sai Ka'ab yace: Nace Ya Manzon Allah! Lallai Allah Ya tseratar dani ne saboda Gaskiya, kuma lallai yana daga cikin Tubata ba zan taɓa bada wani labari ba face sai na Gaskiya har idan ina raye, -kuma Ka'ab Allah Ya yarda dashi yace-: Na rantse da Allah, ban taɓa yin Ƙarya da gangan ba tunda na faɗawa Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- hakan har zuwa wannan rana tawa, kuma ina fatan Allah Ya kiyaye ni a cikin abunda yayi saura -na rayuwata-» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

## Ina neman tsarin Allah daga Shaiɗan jefaffe

﴿ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَكُونُواْ مَعَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴾

((**Yaku waɗanda kukayi Imani da Allah, kuji tsoron Allah kuma ku kasance tareda masu Gaskiya**)). [Suratul Al-Taubah: 119).

Allah Yayi min Albarka tare daku a cikin Alqur'ani mai girma...

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Hallittu, Masanin abubuwan dake ɓoye, wanda Yake tsinkayar abunda ke cikin Zukata da Niyyoyi, ina godemaSa –Allah Mai Tsarki- don abunda Ya keɓance mu dashi na manyan Ni'imomi, kuma ina gode maSa Maɗaukaki akan abunda Yayi mana kyauta dashi na kyautuka da Karamci kala-kala.

Kuma ina shaida cewa babu Abun bauta da gaskiya sai Allah Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, Shine Sarki abun tsarkakewa Mai Aminci.

Kuma ina shaida cewa lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, shine mafi Alkhairin wanda aka aiko kuma mafi cikar kamalar jagora, Allah Yayi Salati da Aminci a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa Aminci mai yawa dawwamamme.

**Amma Ba'adu[1]:**

Kuji tsoron Allah, -yaku bayin Allah- kuma ku sani cewa lallai mafi Alkhairin Magana itace Maganar Allah, kuma mafi Alkhairin Shiriya itace Shiriyar Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi-, kuma kashedinku da ƙirƙirarrun abubuwa; domin duk abunda aka ƙirƙira Bidi'a ne kuma kowace Bidi'a Ɓata ce kuma kowace Ɓata tana cikin Wuta, kuma ku lazimci Jama'ar Musulmi; domin Hannun Allah yana tare da

(1) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

Jama’ar Musulmi kuma duk wanda ya ɓangare daga gare su zai ɓangare a cikin Wuta.

**Yaku bayin Allah:**

Lallai ɗabi’u Maɗaukaka da ababen da ake godewa da Musulunci yake dasawa cikin rayuka, ta hanyar Nagarta da kawo gyara kuma a gefe guda akwai ɗabi’u na tawaya dana ƙyama waɗanda Musulunci ya yaƙa; domin kasancewarsu ɗabi’u masu kaiwa ga talalaɓiya, kuma sabubba ne na rushe ɗabi’ar rai, kuma Ƙarya itace karin farko a cikin waɗannan miyagun ɗabi’un; lallai Ƙarya tana cikin mafi munin ɗabi’u masu tawaya kuma tana cikin ɗabi’u ƙasƙantattu masu halakarwa:

﴿إِنَّمَا يَفْتَرِي ٱلْكَذِبَ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ ۖ وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْكَٰذِبُونَ﴾

((**Abun sani kawai, waɗanda basu yi imani da Ayoyin Allah ba sune suke ƙirƙira Ƙarya, kuma waɗannan sune Maƙaryata**)) (Suratul Nahl: 105).

Kuma Allah Ya gwama tsakanin Ƙarya da bautar Gumaka; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿فَٱجْتَنِبُوا۟ ٱلرِّجْسَ مِنَ ٱلْأَوْثَٰنِ وَٱجْتَنِبُوا۟ قَوْلَ ٱلزُّورِ﴾

((**Don haka, ku nisanci ƙazanta daga Gumaka kuma ku nisanci ƙazanta daga Shaidar Zur** –ta Ƙarya-)) [Suratul Hajj: 30].

Akwai wasu kalar Mutane, suna ganin cewa Ƙarya wani launi ne na cikar Hankali, da kaifin basira da ƙwarewa a cikin Al’amura; harma suna ganin cewa tana daga cikin baiwar Mutum mai iya zartar da ababe, amma ta yaya zata kasance hakan?! Bayan kasancewarta

ƙasƙantattar ɗabi'a ce zalla! ginshiƙinta Zunubai ne da kuma asalin Sharrori, wanda yake nuni ga shigar ɓarna a cikin Ran Ma'abocinta, kuma Ƙarya tana daga cikin Alamomin Tsoro da Rauni, kuma Alama ce daga cikin Alamomin Munafurci; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- Yana cewa: «**Ababe guda Huɗu, duk wanda suka kasance a cikin shi ya kasance tsantsar Munafiki, kuma duk wanda yake da wata ɗabi'a daga cikin su, akwai wata ɗabi'a ta Munafurci tare dashi har sai ya barta, idan aka amince masa sai yayi Ha'inci, kuma idan ya bada labari sai yayi Ƙarya, kuma idan yayi Alƙawari sai yayi Yaudara, kuma idan yayi Husuma sai yayi Fajirci**». [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]. Muslim ya ƙara a cikin Riwayarsa «**kuma koda yayi Azumi yayi Sallah, kuma ya raya cewa shi Musulmi ne**».

Allahu Akbar! Haƙƙoƙa nawa ne suka tozarta saboda Ƙarya, kuma aka ci Mutunci saboda ita?! Sau nawa ne Ƙarya tazama sanadin yanke Zumunta da kawo Adawa?!

Lallai Maƙaryaci yana rarraba kan Jama'a da Ƙaryarsa, kuma yana raba haɗuwar Mutane saboda abunda yake ƙirƙirawa na Al'amura marasa tabbas da Zato na Ƙarya.

Ƙarya sanadi ce wanda yake kaiwa ga lalacewar Ayukka da kuma tozartar Haƙƙoƙa; Ƙarya tana wulaƙantar da Martabar Mutum, kuma tana zubar da girman Mazaje, kuma tana daga cikin Munanan Zunubai da miyagun Aibobi, Ƙarya ɗabi'a ce wulaƙantatta kuma Hali ne lalatacce, kuma raunin Addini ce, abunda yake

haka, ta yaya za'a siffanta Ma'abucinsa da cikar Hankali?!

Abunda ya dace da Maƙaryaci shine, a saɓa masa idan yayi umurni, a saɓa masa idan yayi hani; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ فَلَا تُطِعِ ٱلْمُكَذِّبِينَ ﴾

((**don haka, kada kabi Masu ƙaryatawa**)). [Suratul Qalam: 8].

A nisance shi idan ya kusanto, kuma a tsoratar daga gare shi idan ya nisanta, Nunfashinsa Guba ne, Zuciyarsa mai ciwo ce, kuma duk wanda ya nisanci Gaskiya zai faɗa ramin Ƙarya da Ɓata.

Don haka, Kuji tsoron Allah -yaku bayin Allah-, ku lazimci Gaskiya a Magana da aiki, sai ku rabauta da Alkhairin Duniya da Lahira.

Sa'annan kuma ku sani, lallai Allah Ya umurce ku da yin Salati da Sallama ga AnnabinSa ...

## GODIYA AKAN NI'IMOMI[1]

Godiya ta tabbata ga Allah, muna godema maSa kuma muna neman taimakonSa, kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrorin kawunan mu da miyagun Ayukkan mu, duk wanda Allah Ya shiryar dashi babu mai ɓatar dashi, kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa lallai Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi Salati da Aminci mai yawa a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Ammab Ba'adu[2]:**

Kuji tsoron Allah -yaku bayin Allah- haƙiƙanin tsoro; domin tsoron Allah Haske ne a cikin Zuciya, kuma tanadi ne a Makoma.

**Ayyuhal Muslimŭn[3]:**

Haƙiƙa, Allah Ya yawaita Ni'imominSa masu girma ga bayinSa, kuma Ya cikasu da Ni'imominSa manya manya «Damar Allah a cike take, ciyarwa bata rageta, Mai yawan kyauta ne Safe da Yamma» [Bukhari da

---

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a Ashirin da Uku ga watan Shawwal, Shekara ta Dubu Ɗaya da Ɗari Huɗu da Ashrin da Uku bayan Hijira.

(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

(3) Yaku Musulmi.

Muslim Suka ruwaito shi], Allah Yana rarraba Arzukka, Yana yawan bada Kyautuka, kuma Yana arzurta wanda Yaso batare da kidanyawa ba, Yana jarabtar bayinSa da Ni’imomi kamar yadda Yake jarabtarsu da Musibobi:

﴿ وَنَبْلُوكُم بِٱلشَّرِّ وَٱلْخَيْرِ فِتْنَةً ۖ وَإِلَيْنَا تُرْجَعُونَ ﴾

((**Kuma Muna Jarabtarku da Sharri da Alkhairi domin Fitina, kuma zuwa gareMu ne zaku dawo**)). [Suratul Ambiyã: 35].

Allah Shine Mai yin Ni’ima da wannan baki ɗayansa, kuma Fitinar Jin daɗi tafi girma akan Fitinar Cutarwa, kuma Ma’abocinta yana buƙatar Haƙuri da Godiya.

kuma Talauci da Wadata sune kashin bayan Jarabta da Fitina, kuma Haƙuri da Godiya suna lizimtar bawa a cikin Umurnin Ubangiji da HaninSa, da tsarawarSa da ƘaddarawarSa, kuma an gina tsoron Allah ne akan su. Kuma lallai Allah Mai tsarki Ya gwama tsakanin Godiya da Imani da Shi; sai Ya ce:

﴿ مَّا يَفْعَلُ ٱللَّهُ بِعَذَابِكُمْ إِن شَكَرْتُمْ وَءَامَنتُمْ ۚ ﴾

((**Meye Allah zai yi da azabtar daku idan kukayi Godiya kuma kukayi Imani**)). [Suratu Al-Nisa’i: 147].

Kuma Allah Mai tsarki Ya bada labari cewa Godiya ita ce manufa a cikin HallitarSa da UmurninSa sai Ya ce:

﴿ وَٱللَّهُ أَخْرَجَكُم مِّنۢ بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمْ لَا تَعْلَمُونَ شَيْـًٔا وَجَعَلَ لَكُمُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ وَٱلْأَفْـِٔدَةَ ۙ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ﴾

((**Kuma Allah Ya fito daku daga cikun-kunan Mahaifanku baku san komai ba, kuma Ya saka muku**

**Ji da Gani da Zukata domin kuyi Godiya**)). [Suratul Nahl: 78].

Kuma Allah Mai tsarki Ya sanya samun yardarSa a cikin gode maSa:

﴿وَإِن تَشۡكُرُواْ يَرۡضَهُ لَكُمۡۗ﴾

((**Kuma idan kuka yi godiya zai yardar maku hakan**)) [Suratul Zumar: 7].

Kuma Allah Ya hallicci Dare da Yini; domin ayi tunani kuma ayi godiya:

﴿وَهُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ خِلۡفَةً لِّمَنۡ أَرَادَ أَن يَذَّكَّرَ أَوۡ أَرَادَ شُكُورًا﴾

((**Kuma Shi ne wanda Ya sanya Dare da Yini suna maye juna; domin wanda yayi nufin yayi tunani ko yayi nufin Godiya**)). [Suratul Furqãn: 62].

Kuma Allah bayinSa sun rarrabu zuwa ga masu Gode masa da masu Kafirce maSa, Ya ce:

﴿إِنَّا هَدَيۡنَٰهُ ٱلسَّبِيلَ إِمَّا شَاكِرًا وَإِمَّا كَفُورًا﴾

((**Lallai ne Mu Mun shiryar dashi hanyar ƙwarai, ko ya kasance mai Godiya ko kuma mai Kafirci**)). [Suratul Insãn: 3].

Kuma Allah Mai Tsarki Ya bada labari cewa masu bauta masa kaɗai sune waɗanda suka gode maSa, don haka duk wanda bai gode maSa ba, bai kasance daga cikin masu bauta maSa ba, kuma haƙiƙa Allah Ya yi yabo ga farkon Manzo wanda Ya aika zuwa ban ƙasa saboda godiya; Ya ce:

﴿ ذُرِّيَّةَ مَنۡ حَمَلۡنَا مَعَ نُوحٍۚ إِنَّهُۥ كَانَ عَبۡدٗا شَكُورٗا ﴾ [الإسراء: 3].

**((Zuriyar waɗanda muka ɗauka tareda Nuhu, lallai shi ya kasance wani bawa ne mai yawan godiya)) [Suratul Isrã: 3].**

Kuma Ya umurci bawanSa Musa –Aminci ya tabbata a gare shi- da ya karɓi abunda Ya bashi na Annabta, da Manzanci da Magana dashi da Godiya; Allah Mai Buwaya da ɗaukaka Ya ce:

﴿قَالَ يَٰمُوسَىٰٓ إِنِّي ٱصۡطَفَيۡتُكَ عَلَى ٱلنَّاسِ بِرِسَٰلَٰتِي وَبِكَلَٰمِي فَخُذۡ مَآ ءَاتَيۡتُكَ وَكُن مِّنَ ٱلشَّٰكِرِينَ﴾

**((Yace ya Musa lallai Ni na zaɓeka akan Mutane da ManzanciNa da MaganaTa, don haka, kayi riƙo da abunda Na baka kuma ka kasance daga cikin masu Godiya**)) [Suratul A'arãf: 144].

Kuma Yayi yabo ga BadaɗayinSa Ibrahim –Aminci ya tabbata a gare shi- saboda godema Ni'imominSa, Allah Ya ce:

﴿إِنَّ إِبۡرَٰهِيمَ كَانَ أُمَّةٗ قَانِتٗا لِّلَّهِ حَنِيفٗا وَلَمۡ يَكُ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ❋ شَاكِرٗا لِّأَنۡعُمِهِۚ﴾

**((Lallai Ibrahim ya kasance wata Al'umma** –Jagora- **mai ƙasƙantar da kai ga Allah, mai karkata daga kowace hanya zuwa ga Allah kuma bai kasance daga cikin Mushrikai ba ❋ ya kasance mai godiya ga Ni'imominSa)) [Suratul Nahl: 120-121].**

Kuma Allah Ya umurci iyalan Da'wud –Aminci ya tabbata a gare shi- da godiya, Allah Ya ce:

﴿ ٱعۡمَلُوٓاْ ءَالَ دَاوُۥدَ شُكۡرٗاۚ ﴾

((**Yaku iyalan Dawud Ku yi; don godiya**)) [Suratu Saba'i: 13].

Kuma Sulaiman -Aminci ya tabbata a gare shi- ya roƙi UbangijinSa don ya kasance daga cikin masu godiya ga Ni'momi:

﴿ رَبِّ أَوۡزِعۡنِيٓ أَنۡ أَشۡكُرَ نِعۡمَتَكَ ٱلَّتِيٓ أَنۡعَمۡتَ عَلَيَّ وَعَلَىٰ وَٰلِدَيَّ ﴾

((**Ya Ubangijina Ka cusa min in godewa Ni'imarka wadda kayi a gare ni da kuma Mahaifana**)) [Suratu Naml: 19].

Kuma Allah Ya umurci ManzonSa Muhammad -Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- da yin godiya akan Ni'imomi; Allah Ya ce:

﴿بَلِ ٱللَّهَ فَٱعۡبُدۡ وَكُن مِّنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ﴾

((**A'aha, kai dai ka bautawa Allah kuma ka kasance daga cikin masu godiya**)). [Suratul Zumar: 66].

Kuma Allah Ya umurci Luƙmãn da yin godiya; sai Allah Ya ce:

﴿ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا لُقۡمَٰنَ ٱلۡحِكۡمَةَ أَنِ ٱشۡكُرۡ لِلَّهِۚ ﴾

((**Kuma haƙiƙa, Mun baiwa Luqmãn Hikima** – Muka ce masa- **ka godewa Allah**)). [Suratu Luqmãn: 12].

Kuma farkon Wasiyya da Ubangijin mu Yayiwa

Mutum shine yayi godiya ga Ni’imomi a gare Shi da Mahaifansa; sai Allah Ya ce:

﴿أَنِ ٱشْكُرْ لِى وَلِوَٰلِدَيْكَ إِلَىَّ ٱلْمَصِيرُ﴾

((**Ka gode maNi da Mahaifanka biyu, Makoma zuwa gareNi take**)) [Suratu Luqmãn: 14].

Kuma Annabwa sun umurci Mutanensu da yin godiya ga Ni’imomi; Ibrahim -Aminci ya tabbata a gare shi- yace ga Mutanensa:

﴿فَٱبْتَغُوا۟ عِندَ ٱللَّهِ ٱلرِّزْقَ وَٱعْبُدُوهُ وَٱشْكُرُوا۟ لَهُۥٓ﴾

((**Ku nemi Arziki a wurin Allah kuma ku bauta maSa kuma ku gode maSa**)). [Suratul Ankabũt: 17].

Kuma babu mai wa’azantuwa da Ayyoyi da ababen lura sai mai godewa Ni’imomi; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿كَذَٰلِكَ نُصَرِّفُ ٱلْءَايَٰتِ لِقَوْمٍ يَشْكُرُونَ﴾

((**Haka nan, Muke jujjuya Ayyoyi ga Mutane masu godiya**)). [Suratul A’arãf: 58].

Kuma Allah Ya cikamu da Ni’imomi domin muyi yabo a gare Shi akanta; Allah Mai Buwaya da Ɗaukaka Ya ce:

﴿وَرَزَقَكُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ لَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ﴾

((**Kuma Ya arzutaku daga ababe masu dãɗi; saboda kuyi godiya**)) [Suratul Amfãl: 26].

Kuma yin godiya itace Wasiyar Annabi -Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- ga Sahabbansa; haƙiƙa ya ce: «**Ya Mu’az! Wallahi ni ina sonka, ina maka**

**Wasici ya kai Mu'az: a bayan kowace Sallah kada kabar faɗin: Ya Allah Ka taimake ni akan AmbatonKa, da gode maKa, da kuma kyautata IbadarKa**». [Abu dawud ya ruwaito shi].

Kuma roƙon bawa ga Ubangijinsa ya samu damar cika godiyar Allah akan Ni'imominSa tana daga cikin mafi falalar Addu'a, Shaikhul Islam ɗan Taimiyya –Allah Ya jiƙansa yana cewa-: «Nayi nazari akan mafi falalar Addu'a sai nasamu itace: (Ya Allah Ka taimake ni akan AmbatonKa da gode maKa da kyautata IbadarKa)», kuma Masu godiya ga Ni'imomi sune waɗanda aka keɓance da Ni'imominSa a tsakanin BayinSa, kuma sune waɗanda basa girgizuwa a lokacin Fitintinu:

﴿وَمَن يَنقَلِبْ عَلَىٰ عَقِبَيْهِ فَلَن يَضُرَّ ٱللَّهَ شَيْـًٔا ۗ وَسَيَجْزِى ٱللَّهُ ٱلشَّـٰكِرِينَ﴾

((**Kuma duk wanda ya juya bayansa lallai ba zai cutar da Allah da komai ba, kuma da sannu Allah zai sakawa masu Godiya**)). [Suratu Ãli Imrãn: 144].

Kuma da maƙiyin Allah Iblis yasan darajar matsayin godiya, kuma yasan cewa tana daga cikin Ibadu mafi ɗaukaka kuma mafi girma; sai yasanya babban Burinsa shine yin ƙoƙarin yanke Mutane daga gareta, sai yace:

﴿ثُمَّ لَـَٔاتِيَنَّهُم مِّنۢ بَيْنِ أَيْدِيهِمْ وَمِنْ خَلْفِهِمْ وَعَنْ أَيْمَـٰنِهِمْ وَعَن شَمَآئِلِهِمْ ۖ وَلَا تَجِدُ أَكْثَرَهُمْ شَـٰكِرِينَ﴾

((**Sa'nnan lallai zan zo masu ta gabansu data bayansu, data damansu data hagunsu, kuma bazaka samu mafi yawa daga cikinsu masu godiya ba**)). [Suratul A'arãf: 17].

Kuma Annabin mu Muhammad -Tsira da Aminci su

tabbata a gare shi- shine mafi godiyar halittu ga UbangijinSa, -ya bar Duniya bai taɓa ƙoshi daga wainar Sha'ir ba, kuma saboda Yinwa ya kai ga ɗaura dutsi a cikinsa, kuma an gafarta masa abunda ya gabata na Zunubinsa da abunda ya jinkirta-, yana yin tsayuwar dare har sai da ƙafafunsa suka tsage, kuma yana cewa «**Ashe bazan kasance Bawa mai godiya ba?!**». [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Dawud -Aminci ya tabbata a gare shi- «**Ya kasance yana yin bacci rabin dare, kuma yayi tsawuya a cikin ɗaya bisa uku na dare, kuma yana bacci ɗaya bisa shida na daren, kuma yana Azumin rana ɗaya kuma ya ajiye rana ɗaya**». [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]; kuma Allah Mai Buwaya da Ɗaukaka yace masa:

﴿ ٱعۡمَلُوٓاْ ءَالَ دَاوُۥدَ شُكۡرٗاۚ ﴾

((**Yaku iyalan Dawud Kuyi aiki don godiya**)) [Suratu Saba'i: 13].

Kuma godiya ga Ni'imomi tsari ne daga Azaba; Allah Mai Buwaya da Ɗaukaka Ya ce:

﴿ مَّا يَفۡعَلُ ٱللَّهُ بِعَذَابِكُمۡ إِن شَكَرۡتُمۡ وَءَامَنتُمۡۚ ﴾

((**Meye Allah zai yi da azabtar daku idan kukayi Godiya kuma kukayi Imani**)). [Suratu Al-Nisa'i: 147].

Kuma Allah Ya tseratar da Luɗ -Aminci ya tabbata a gare shi- daga Azaba saboda godiya ga Ni'imomi:

﴿إِنَّآ أَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمۡ حَاصِبًا إِلَّآ ءَالَ لُوطٍۖ نَّجَّيۡنَٰهُم بِسَحَرٍ ❋ نِّعۡمَةً مِّنۡ عِندِنَاۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي مَن شَكَرَ﴾

**((Lallai Mu Mun aika masu da Iskar tsakuwa akansu, face kawai Mabiyan Luɗ, Mun tseratar dasu a lokacin Sahur ❋ Saboda wata Ni'ima daga wurin mu, kuma haka ne Muke sakawa wanda yayi godiya))** [Suratul Qamar: 34-35].

Kuma a lokacinda Mutanen Saba'i sukayi Butulci ga Ni'imomin Allah kuma sukayi musantata kuma suka fuskanci Ni'imomin da Saɓo; sai Allah Ya yaye Ni'imomin daga gare su kuma Ya ɗanɗana masu Azaba kala-kala; Allah Yace gameda Sha'anin su:

﴿فَأَعۡرَضُواْ فَأَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمۡ سَيۡلَ ٱلۡعَرِمِ وَبَدَّلۡنَٰهُم بِجَنَّتَيۡهِمۡ جَنَّتَيۡنِ ذَوَاتَيۡ أُكُلٍ خَمۡطٖ وَأَثۡلٖ وَشَيۡءٖ مِّن سِدۡرٖ قَلِيلٖ ❋ ذَٰلِكَ جَزَيۡنَٰهُم بِمَا كَفَرُواْۖ وَهَلۡ نُجَٰزِيٓ إِلَّا ٱلۡكَفُورَ﴾

**((Sai suka bijire, Saboda haka sai Muka saki Mãlãlar madatsar ruwa a kansu, kuma muka musanya musu gonakinsu biyu da waɗansu gonaki biyu masu ƴaƴan itace kaɗan: talakiya da Goriba da wani abu na Magarya kaɗan ❋ Munyi masu sakamako da wannan ne saboda Kafircewar su, kuma lallai bamu yiwa kowa irin wannan sakamakon sai Kafiri)).** [Suratu Saba': 16-17].

Kuma Masu Gonan nan –kamar yadda labarin su yazo a cikin Suratul Qalam- sun fuskanci Ni'imar Allah da Butulci da rowa ga Miskinai; sai wani Mai kewayawa ya

kewaya ga amfanin gonarsu sai gonar ta wayi gari ƙura, kamar duhun dare, Fuɗhail ɗan Iyadh -Allah Ya jiƙansa- yana cewa: «Na umurce ku da lizimtar godiya akan Ni'imomi; domin da wuya wata Ni'ima data gushe daga Mutane ta dawo gare su».

Kuma masu godewa ga Ni'imomin Allah ƴan kaɗan ne; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَقَلِيلٌ مِّنْ عِبَادِيَ ٱلشَّكُورُ﴾

((**Kuma kaɗan ne daga cikin bayiNa suke godiya**)) [Surattu Sa'aba'i: 13].

kuma duk Ni'imar da bata kusantar da bawa zuwa ga Allah ba lallai Azaba ce, kuma godiya itace take tsare N'imomin da ake dasu yanzu kuma ta jawo wasu Ni'imomin da babu su, Aliyyu ɗan Abi Ɗalib –Allah Ya yarda dashi- Yana cewa: «Ni'ima tana sade da Godiya, kuma Godiya tana rataye da samun ƙari, kuma ƙari daga wurin Allah ba zai yanke ba har sai Godiya ta yanke».

Kuma idan Bawa yanada Matsayi a wurin Allah sai ya kiyaye shi, kuma ya tabbata akan sa, sa'annan kuma ya godewaa Allah akan abunda Ya bashi; lallai Allah zai bashi abinda yake sama da shi, kuma idan ya tozarta godiya, Allah zai masa tãlãla, Hassanul Basriy –Allah Ya jiƙansa- yana cewa: «Lallai Allah Yana jiyar da daɗi da wata Ni'ima kamar yadda yaso, idan ba'a gode maSa akanta ba sai Ya juyata zuwa Azaba», kuma idan kaga Ubangijinka Yanata baka Ni'imominSa wata-bayan-wata alhali kana saɓa maSa, lallai ka kiyaye Shi; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿سَنَسْتَدْرِجُهُم مِّنْ حَيْثُ لَا يَعْلَمُونَ﴾

**((Da sannu zaMuyi masu Is'tidiraji ta inda basu sani ba))** [Suratu Qalam: 44].

Sufyãn –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Ya cika Ni'imomi a gare su kuma sai Ya hanasu Godiya».

Kuma duk wanda akayi masa arzikin godiya lallai anyi masa arziki samun ƙari:

﴿وَإِذْ تَأَذَّنَ رَبُّكُمْ لَئِن شَكَرْتُمْ لَأَزِيدَنَّكُمْ وَلَئِن كَفَرْتُمْ إِنَّ عَذَابِي لَشَدِيدٌ﴾

((**Kuma a lokacinda Ubangijinka Yayi sanarwa, lallai idan kukayi godiya tabbas Zan ƙara muku kuma idan kuka kafirce lallai AzabaTa mai tsanani ce**)). [Suratu Ibrahim: 7].

Abu Ƙilãba -Allah ya jiƙansa- yana cewa: «Duniyar da kuka yi godiyarta bazata cutar daku ba».

Kuma haƙiƙa Allah Mai tsarki Ya soki Butulu daga cikin BayinSa –wanda baya gode maSa akan Ni'imominSa-; sai Allah Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلْإِنسَٰنَ لِرَبِّهِۦ لَكَنُودٌ﴾

((**Lallai Mutum mai tsananin Butulci ne ga UbangijinSa**)). [Suratul Ãdiyãt: 6].

**Ayyuhal Muslimũn[1]:**

Da godiyar Allah da yi maSa biyayya ne ƙofofin Duniya dana Lahira suke buɗewa ga Bawa; Allah Mai

[1] Yã ku Musulmai.

tsarki Ya ce:

﴿وَلَوْ أَنَّ أَهْلَ ٱلْقُرَىٰٓ ءَامَنُوا۟ وَٱتَّقَوْا۟ لَفَتَحْنَا عَلَيْهِم بَرَكَـٰتٍ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ﴾

((**Kuma lallai da Mutanen Alƙaryu sunyi Imani kuma sukayi Taƙawa da Mun buɗe Albarkoki a garesu ta Sama da Ƙasa**)). [Suratul A’arãf: 97].

Kuma godiyar Allah tana kasancewa ne da Zuciya da Harshe da Gaɓoɓin jiki; tana kasancewa ne da Zuciya ta hanyar jingina Ni’imomin ga Mahalliccin su; Allah Mai tsarki ace:

﴿وَمَا بِكُم مِّن نِّعْمَةٍ فَمِنَ ٱللَّهِ﴾

((**Kuma duk wata Ni’ima dakuke da ita, lallai daga Allah take**)) [Suratul Nahl: 53].

Kuma tana kasancewa da Harshe ne da yawan yin godiya ga wanda Ya bada ta; Annabi -Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Kuma Alhamdulillah; tana cika Ma’auni**» [Muslim ya ruwaito shi].

Don haka, Alhamdulillah itace ƙololuwar Godiya kuma itace farkonta, kuma itace Aya ta farko a cikin Littafin Allah Mai girma:

﴿ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَـٰلَمِينَ﴾

((**Dukkan godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin Talikai**)). [Suratul Fãtiha: 1].

Kuma lallai Allah Ya umurci AnnabinSa -Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- da ya bada labarin Ni’imomin Allah; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ وَأَمَّا بِنِعْمَةِ رَبِّكَ فَحَدِّثْ ﴾

**((Amma kuma ka bada labari gameda Ni'imomin Ubangijinka))** [Suratul Duhã: 11]

Kuma godiya da Gaɓɓai: tana kasancewa ne a cikin amfani da Ni'imar a cikin neman yardar Allah, da kuma ƙin amfani da ita a cikin abunda yake Fusata Shi da kuma Saɓa maSa; Godiyar Ni'imar Ido itace kada ya kalli abunda Allah Ya haramta da shi, kuma kada Mutum ya saki ganinsa zuwa ga ababen da Allah Ya haramta, kuma godiyar Ni'imar Harshe shine kada Mutum ya bada labari dashi sai gaskiya, kuma kada yayi magana dashi face sai da Gaskiya, kuma godiyar Ni'imar Kunnuwa itace kada Mutum ya saurari Giba da Ƙiren karya da Haram dasu.

Haƙiƙa Allah Yayi umurni da godewa Mahaifa a cikin FaɗinSa:

﴿ أَنِ ٱشْكُرْ لِي وَلِوَٰلِدَيْكَ ﴾

((**Ka gode maNi da Mahaifanka biyu**)) [Suratu Luqmãn: 14].

Kuma yana daga cikin gode masu, yi musu biyayya da kyautatawa zuwa gare su, da yi musu Addu'a da ƙaunarsu da neman yardarsu, da saukar da kai a garesu, kuma daga cikin Saɓo akwai: bijire musu, da yin Tir dasu da ƙin bin Umurnin su, da sanyin jiki a cikin yi masu ɗa'a.

Kuma mafi arzikin Mutane shine wanda ya saka Ni'imomi matsayin hanyoyin kaiwa ga Allah da ranar

Lahira, kuma mafi taɓewarsu shine wanda yayi amfani da Ni'imominsa zuwa ga bin son Zuciya da samun jin daɗinsa.

**Ina neman tsarin Allah daga Shaiɗan jefaffe**

﴿إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضۡلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَشۡكُرُونَ﴾

((**Lallai Allah Mai yawan falala ne ga Mutane sai dai mafi yawan Mutane basa godewa**)). [Suratul Baqara: 243].

Allah yayi min Albarka tare daku a cikin Alƙur'ani mai Girma...

## HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarSa da kuma Ni’imominSa, kuma ina Shaida lallai babu abun bauta da Gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya; don girmamawa ga sha’aninSa, kuma ina shaida lallai Annabin mu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi Salati da Aminci mai yawa da ƙari a gareshi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Amma ba'adu Ayyuhal Muslimŭn(1):**

Ubangijimu Ya siffantu da godiya, kuma mafi soyuwar hallittunSa a gare shi shine wanda ya siffantu da siffar godiya, kamar yadda mafi ƙyamar hallittarSa a gareShi shine wanda ya ɓata wannan sifar ta godiya kuma ya siffantu da kishiyarta, Shi Allah Mai tsarki Mai yawan godiya ne kuma Yana son masu godewa, kuma godewa wanda yayi maka Alkhairi daga cikin hallitun Allah yana daga cikin godewa Allah, Annabi -Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Wanda baya godewa Mutane, baya godewa Allah**» [Ahamd ya ruwaito shi].

Kuma idan kayi wani Alkhairi ga wani, kada ka kama jiran godiya daga gare shi, ka nemi Lada daga Allah, kuma ka kasance mai wadatuwa da abunda Allah ya arzutaka dashi sai ka kasance daga cikin mafiya godiya, kuma ka yawaita godiya ga Allah da yabo a gare Shi;

(1) Bayan haka, Yaku Musulmi

domin wannan Ibada ce daga cikin Manyan Ibadu; Annabi -Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Mai cin abinci mai godiya ga Ni'ima kamar mai Azumi ne mai Haƙuri**» [Hãkim ya ruwaito shi].

Kuma duk wanda bai godewa kaɗan ba, ba zai godewa mai yawa ba, kuma Abu Mugirah –Allah Ya jiƙansa- ya kasance idan aka ce masa: Ya ka wayi gari? Sai yace: «Mun wayi gari muna masu nutso a cikin Ni'imomi, kuma muna masu kasawa daga godiya».

﴿وَإِن تَعُدُّواْ نِعۡمَةَ ٱللَّهِ لَا تُحۡصُوهَآۗ﴾

((**Kuma idan zaku ƙirga Ni'imomin Allah bazaku iya kewayewa dasu ba**)). [Nahl: 18].

Kuma babu wani daga cikin Mutane face sai an jarabce shi da Lafiya; domin aga yadda zai gode, ko kuma a jarabce shi da wani Bala'i; domin aga yadda zai yi Haƙuri.

Wajibi ne akanku –yaku bayin Allah- da haɗawa tsakanin Haƙuri da Godiya tareda Taƙawa; sai su kasance daga cikin mafiya bautar Mutane.

Sa'anna kusani lallai Allah Ya umurceku da yin Salati da Sallama ga AnnabinSa ...

# KYAWAWAN ƊABI'U[1]

Godiya ta tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrorin kawunan mu da miyagun Ayukkan mu, duk wanda Allah Ya shiryar babu mai ɓatar dashi kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida lallai Annabin mu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi Salati da aminci mai yawa a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Amma Ba'adu[2]:**

Kuji tsoron Allah yaku bayin Allah haƙiƙanin tsoro, kuma kuyi riƙo da Musulunci da Igiya mai Ƙarfi.

**Ayyuhal Muslimŭn[3]:**

Allah Ya shar'antawa bayinSa nau'o'in ayukan ɗã'a da neman kusanci, kuma Ya umurce mu da Al'ummomin dasuke gabanin mu da yin Ibadah wadda take kusantar da bawa ga UbangijinSa, kuma take nauyaya Ma'auninsa ranar Ƙiyama; Annabi –Tsira da Amincin Allah su

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a goma sha uku ga watan Jumãda Ulã, Shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da talatin da huɗu bayan Hijira.
(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.
(3) Yaku Musulmi.

tabbatta a gare shi- ya ce: «**Ba wani abu dayafi nauyin kyawawan ɗabi'u a cikin Mizani a ranar Ƙiyama**» [Tirmizi ya ruwaito shi], kuma kyawawan ɗabi'u suna ɗaga darajarsa kuma suna ƙara yawan ladansa; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Lallai Mutum zai iya kaiwa ga darajar mai Azumi mai tsayuwar dare; saboda kyawawan halaye**» [Ahmad ya ruwaito shi], kuma ladar kyawawan ɗabi'u yana nunkawa koda kuwa wani abu ne ɗan kaɗan daga ciki; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Kada ka rena komai daga aikin Alkhairi, koda ka haɗu da ɗan uwanka ne da fuska a sake**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma mafi Alkhairin Halittu shine wanda ya kasance Mumini ne kuma ya siffantu da kyawawan ɗabi'u; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Lallai na daga cikin zaɓaɓɓunku, mafiya kyawawan ɗabi'unku**». [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma kyawawan ɗabi'u sune mafi yawan abunda yake shigar da Mutane Aljannah; «An tambayi Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- gameda abunda yake yawan shigar da Mutane Aljannah, sai ya ce: **Tsoron Allah, da kyawawan ɗabi'u**» [Tirmizi ya ruwaito shi], kuma dasu ne Imanin bawa yake cika; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Mafi cikar Imani daga cikin Muminai shine; wanda yafi su kyawun ɗabi'u**» [Ahmad ya ruwaito shi] kuma mafi girman darajoji a ranar Lahira tana kasancewa ne ga wanda ya aikata su; Annabi –Tsira

da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Ni nayi lamunin wani gida a mafi ƙololuwar Aljannah ga wanda ya kyautata halayensa**» (Abu dawud ya ruwaito shi].

Ibnul Qayyim –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Addini shine: Halaye, duk wanda ya wuce ka a cikin Halaye; ya wuceka a cikin Addini», kuma haƙiƙa Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya kasance a cikin Sallarsa yana roƙon Ubangijinsa samun kyawawan Halaye; sai ya kasance yana cewa: «**Kuma Ka shiryar dani ga mafi kyawon Halaye, ba mai shiryarwa ga mafi kyawonsu sai Kai, kuma ba ka kawar daga gare ni Munanan su, ba mai kawar da munanan su daga gare ni sai Kai**». [Muslim ya ruwaito shi], kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya kasance yana cewa: «**Ya Allah Ka kyautata Hallita ta; Ka kyautata Halayena**» (Ahmad ya ruwaito shi), Ibn Rajab –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Taƙawa bata cika sai da kyawawan Halaye».

Kuma mafi kusancin matsayi ga Annabawa daga cikin Mutane a ranar Ƙiyama shine wanda yafi su kyawun Halaye, Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Lallai daga cikin mafi soyuwar ku a wurina kuma mafi kusancin ku ga Mazaunina a ranar Ƙiyama shine; wanda yafi ku kyawon halaye**». [Tirmizi ya uwaito shi], kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya kasance yana yiwa Sahabbansa Wasici da kyawawan Halaye; yace ga Mu'az –Allah Ya yarda dashi-: «**Kaji tsoron Allah a duk inda ka kasance, kuma kabi mummunan aiki dana ƙwarai**

**sai ya shafe shi, kuma kayi Mu'amala da Mutane da Halaye na ƙwarai**» [Tirmizi ya uwaito shi], kuma kyawawan ɗabi'u da Rahamar Allah suna tseratarwa daga Wuta «**Ku nemi tsari daga Wuta koda da tsagin Dabino ne, idan baka samu ba, koda da Kalma mai daɗi ce**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Allah Ya aiko AnnabinSa –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- don yin kira zuwa ga Halaye na gari; Annabi -Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- ya ce: «**Ni an aiko ni ne kawai domin na cika kyawawan halaye**» [Ahmad ya ruwaito shi].

Kuma Manzanni -Aminci ya tabbata a garesu- sun siffantu da Halaye Maɗaukaka; Annabi Nuh -Aminci ya tabbata a gare shi- ya kira Mutanensa tsawon shekara Ɗari Tara da Hamsin yana ta Haƙuri dasu, kuma Ibrahim -Aminci ya tabbata a gare shi- ya kasance Mutum mai Karamci; Baƙi sun sauka gidansa, sai yaje zuwa ga Iyalinsa yazo musu da ɗan Maraƙi mai Kitse kuma gasashshe, haka kuma Isma'el -Aminci ya tabbata a gare shi ya ksance- Mai gaskiyar Alƙawari, kuma Yusuf - Aminci ya tabbata a gare shi- yace ga waɗanda suka yi sanadiyar baƙuntarsa a wani gari da shigarsa gidan yari, yace dasu:

﴿لَا تَثْرِيبَ عَلَيْكُمُ ٱلْيَوْمَ﴾

((**Yau babu wani zargi akanku**)) [Suratu Yusuf: 92].

Kuma Musa Aminci ya tabbata a gare shi «**Ya kasance Mutum mai yawan jin Kunya, mai yawan Suturcewa; ba'a ganin wani abu daga fatar jikinsa;**

**saboda Kunyarsa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma Isah -Aminci ya tabbata a gare shi- ya kasance Mai biyayya ga Mahaifiyarsa.

Kuma Annabin mu Muhammad –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- shine mafi cikar Mutane kamalar Halaye, Allah Ya siffanta shi da faɗinSa:

﴿ وَإِنَّكَ لَعَلَىٰ خُلُقٍ عَظِيمٍ ﴾

((**Kuma lallai kai kana akan Halaye masu girma**)) [Suratul Ƙalam: 4].

Ya taso kuma ya rayu yana mai ƙawa da duk wani halin Karamci, yana mai nisantar duk wata sifa abin zargi, wani Mutum yace masa: «Ya mafi Alkhairin halittu! Sai Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- a cikin Tawalu'u- yace: **Wannan Ibrahim -Aminci ya tabbata a gare shi- kenan**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma ya kasance shine mafi karamci rai daga cikin Hallitu; bai taɓa Mayar da mai roƙo ba, kuma shine wanda yafi kowa sakin Fuska, Jarir –Allah Ya yarda dashi- yace: «Kuma -Manzon Allah Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- bai taɓa ganina ba face sai yayi Murmushi a Fuskata» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma ya kasance shine wanda yafi su cika Alƙawari; idan wani daga cikin Sahabbansa yayi rashin lafiya sai ya ziyarce shi, idan kuma bai ganshi ba sai yayi tambaya gameda shi, kuma shine wanda yafi su Zuciya mai tausayi; ya kasance yana taƙaita Sallarsa idan yaji kukan Yaro; saboda baya son ya tsanantawa

Mahaifiyarsa, kuma shine wanda yafi su taushin Hali; idan ya shiga gidansa yana kasancewa ne a cikin hidimar iyalinsa, kuma ya kasance wanda yafi su Haƙuri; wata rana ya fita daga gidansa da dutse a cikinsa; saboda Yinwa amma bai kokawa kowa ba, kuma shine wanda yafi su fãɗin Afuwa; Maƙiyansa sun yake shi sun zubar masa da Jini, amma lokacin da ya buɗe Makkah sai yace masu «**Ku tafi; ku ƴantattu ne**» [Baihaƙi ya ruwaito shi]; kuma yafisu yalwar Haƙuri; Mutanensa sun cutar dashi sai Mala'ikan Duwatsu ya neme shi idan yanaso ya jefo musu Manyan duwatsu guda biyu amma sai yaƙi amincewa, kuma yace da Aisha –Allah Ya yarda da ita-: «**Ina umurtarki da bi ahankali, kuma kashedinki da Tsanani da Alfasha**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma bai taɓa dukan «Wani abu da hannunsa ba ko sau ɗaya, koda Mace ce ko Hadimi» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma akan wannan miƙaƙƙar Hanya –ta Imani da Allah da Halaye Maɗaukaka- Sahabbansa –Allah Ya yarda dasu- suka kasance akai; sai suka kasance masu manyan Halaye tareda Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi-, Urwa ɗan Mas'ud –Allah Ya yarda dashi- yana siffanta yanayinsu sai yace: «Kuma idan ya umurce su sai suyi gaggawar bin umurninsa, kuma idan yayi Magana sai su saukar da Muryoyinsu a wurinsa, kuma basa tsura masa ido suna kallonsa; saboda girmama shi da suke yi» [Bukhari ya ruwaito shi]. Kuma Amru ɗan Ãs –Allah Ya yarda dashi- yace: «kuma ba wani wanda nafi ƙauna sama da Manzon Allah Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi, kuma ba wanda yakai Girmansa a Idanuna, kuma na kasance bana iya

cika idona dashi; saboda girmama shi, da za'a neme ni da in siffanta shi da bazan iya ba; saboda ban kasance ina cika idona dashi ba» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma Sahabbai sun kasance abun buga Misali a cikin girmama junansu; Umar –Allah Ya yarda dashi- ya ce: «Abubakar yafi ni Haƙuri da kuma Ƙima», kuma Ali –Allah Ya yarda dashi- ya ce: «Abubakar ya kasance na gaba a cikin kowane alkairi», kuma Mala'iku sun kasance suna jin kunyar Uthman –Allah Ya yarda dashi- saboda jin Kunyarsa.

**Waba'adu Ayyuhal Muslimŭn(1):**

Bawa bai taɓa girmama kansa ba da kamar: Imani da Allah da kyawawan Halaye, kuma Tauhidi shine ginshiƙin Halaye; don haka, duk wanda ya rasa shi ba zai amfana da waninsa ba, Aisha –Allah Ya yarda da ita-tacewa Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi-: «Ya Manzon Allah! Ibn Jud'ãn –wani ne daga cikin manyan Ƙuraishawa- ya ksance a lokacin Jahiliya yana sadar da Zumunta, yana ciyar da Miskinai, shin haka zai amfane shi? Sai yace: **A'a, ba zai amfane shi ba; domin koda da rana ɗaya bai taɓa cewa ba: Ya Ubangiji, Ka gafarta min kurakurai na a ranar Sakamako**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma idan Musulmai suka ƙawata da Halayen Al-ƙur'ani; sai Jama'a ta gyaru, kuma su kasance masu kira na Alkhairi zuwa ga Addini ta hanyar koyi dasu a cikin ɗabi'u masu kyau, da maganganu abun godewa.

(1) Bayan haka, Yaku Musulmi.

## Ina neman tsarin Allah daga Shaiɗan jefaffe

﴿خُذِ ٱلۡعَفۡوَ وَأۡمُرۡ بِٱلۡعُرۡفِ وَأَعۡرِضۡ عَنِ ٱلۡجَٰهِلِينَ﴾

**((Kayi riƙo da Afuwa kuma kayi umurni da abu mai kyau kuma ka kawar da kai daga Jahilai)),** [Suratul A'arãf: 199].

Allah Yayi min albarka tare daku a cikin Al-ƙur'ani mai girma ...

## HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarSa da kuma Ni’imominSa, kuma ina shaida cewa lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya; don girmamawa ga Sha’aninSa, kuma ina shaida lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Yabon Allah ya tabbata a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa tareda Aminci mai yawa.

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Halayen Mumini sune: Tsayuwa akan Addini, sakin fuska cikin taushin hali, yin Afuwa tareda kyautatawa, Karamci a cikin kyauta, wadatar Zuci a lokacin Talauci, tare da yaye damuwa, da Kalma mai daɗi, yaɗa Sallama, biyayya ga Mahaifa da kyautatawa ga Maƙoci, Ibnul Mubarak -Allah Ya jiƙan sa- ya ce: «Halaye sune: Sakin Fuska, da yin aiki na ƙwarai, da kuma kamewa daga cutarwa».

Kuma Allah Ya raba Halaye kamar yadda ya raba arzuka, kuma Alƙur’ani shine matattarar Halaye na ƙwarai da Ayukka masu kyau; An tambayi Aisha –Allah Ya yarda da ita- gameda Halayen Annabi –Tsira da Aminci Allah su tabbata a gare shi- sai ta ce: «Halayensa sun kasance Alƙur’ani» [Ahmad ya ruwaito shi].

Don haka, kuyi koyi da Annabin ku ta hanyar siffantuwa da Halayen Alƙur’ani, kuma ku kasance akan

(1) Yaku Musulmi.

Hanyar Sahabbansa masu Karamci, kuma ku kasance da siffantuwa da Halayen Sahabbai ababen koyi ga waninku; sai ku samu jin daɗi a gidaje biyu (Duniya da Lahira).

Sa’annan kuma kusani lallai Allah Ya umurce ku da yin Salati da Sallama ga AnnabinSa ...

# HAƘURI DA NATSUWA[1]

Godiya ta tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa, kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrorin kawunan mu da miyagun Ayukkan mu, wanda Allah Ya shiryar daShi babu mai ɓatar dashi, kuma wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida lallai Annabi Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi yabo da Aminci mai yawa a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Amma Ba'adu[2] :**

Kuji tsoron Allah -yaku bayin Allah- haƙiƙanin jin tsoro, kuma kuyi riƙo da Musulunci da Igiya mai ƙarfi.

**Ayyuhal Muslimŭn[3] :**

Mutum yana samun ɗaukaka ne da Imani da kyawawan ɗabi'u, kuma matsayinsa yana ɗaukaka a wurin Allah idan ya haɗa tsakanin su, Annabi –Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- ya ce: «**Ni nayi lamunin wani gida a mafi ƙololuwar Aljannah ga wanda ya**

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a Ashirin da Huɗu ga watan Swafar, Shekara ta Dubu Ɗaya da Ɗari Huɗu da Talatin da Biyu bayan Hijira.
(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.
(3) Yaku Musulmi.

**kyautata Halayensa**» [Abu dawud ya ruwaito shi].

Kuma Haƙuri shine ginshiƙin Halaye, kuma Alama ce ta cikar Hankali da kuma mallakar kan Mutum, kuma wanda ya siffantu dashi zai kasance: Mai girman sha'ani, mai matsayi maɗaukaki, mai ƙarshe abun godewa, mai aiki abun yarda, Shaikhul Islam –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Juriya da Haƙuri akan cutarwa, da Afuwa ga Zalunci sune; mafi falalar Halayen mutanen Duniya da Lahira, dasu ne bawa zai kai inda Azumi da tsayuwar dare basu kaishi ba dasu».

Kuma yana daga cikin Halayen da Allah yake so ga baiyinSa, kuma Yayi Alƙawarin Gafara da Aljannah ga wanda ya siffantu dashi; Allah Mai tsalki yace:

﴿ وَٱلۡكَٰظِمِينَ ٱلۡغَيۡظَ ﴾

**((Kuma da masu haɗiye Fushi)) [**Suratu Ãli Imrãn: 134].

Ibn Katheer –Allah Ya jiƙan shi- yace: «Ma'ana: basa saukar da Fushinsu akan Mutane; sai dai, suna kame Sharrinsu daga gare su, kuma suna neman Ladar hakan daga wurin Allah».

Kuma mafi cancantar siffantuwa dashi [Yafiya] sune: Manzanni, Fuɗhail –Allah Ya jiƙan sa- ya ce: «Daga cikin Halayen Annabawa akwai: Yafiya da Natsuwa da kuma Tsayuwar dare», kuma Allah Yayi yabo ga Ibrahim –Aminci ya tabbata a gare shi- akan juriyarsa; Allah ya ce:

﴿ إِنَّ إِبۡرَٰهِيمَ لَحَلِيمٌ أَوَّٰهٞ مُّنِيبٞ ﴾

**((Lallai Ibrahim Mai Haƙuri ne, mai yawan Kuka, mai saurin komawa ga Allah)) [**Suratu Hũd: 75]. Kuma Akayi masa Bushara da yaro mai siffar Haƙuri:

﴿فَبَشَّرۡنَٰهُ بِغُلَٰمٍ حَلِيمٖ﴾

**((Sai Muka yi masa Bushara da yaro mai Haƙuri)).** [suratus sãffãt: 101].

Kuma Nuhu -Aminci ya tabbata a gare shi- ya kira Mutanensa zuwa ga bautar Allah; sai suka saka ƴan yatsunsu a cikin kunnuwansu; saboda girman kai a gare shi kuma suka kira shi da:

﴿مَجۡنُونٞ وَٱزۡدُجِرَ﴾

((**Mahaukaci ne kuma aka Gargaɗe shi**)) [Suratl Qamar: 9].

Kuma duk da haka yayi Haƙuri dasu tsawon shekaru Dubu ba Hamsin, kuma Mutanen Musa -Aminci ya tabbata a gare shi- sun jefe shi da Hauka kuma akayi masa Ƙalu-bale da Sihiri, kuma suka haɗe masa kai; don su kashe shi amma kuma yayi Haƙuri dasu:

﴿فَبَرَّأَهُ ٱللَّهُ مِمَّا قَالُواْۚ وَكَانَ عِندَ ٱللَّهِ وَجِيهٗا﴾

**((Sai Allah Ya kuɓutar dashi daga abunda suka faɗa, kuma ya kasance mai matsayi a wurin Allah)).** [Ahzãb: 69].

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya hakaito daga wani Annabi cikin Annabwa

wanda Mutanensa suka masa Duka har suka zubar masa da Jini; kuma ya kasance yana shafe Jini daga Fuskarsa yana cewa: «**Ya Ubangijina, Ka gafartawa Mutanena; domin su basu sani ba**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Annabin mu Muhammad –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya hadu da cutarwa da Izgili daga Mutanensa, kuma ya kasance yana cewa da Aisha –Allah Ya yarda da ita- «**Haƙiƙa na haɗu da abunda na haɗu dashi da Mutanenki**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]. Kuma Mala'ikan Duwatsu yazo wurin sa yace masa: «Idan kaso sai na rifto akansu Manyan Duwatsu biyu dake tsakanin Makkah? Sai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: **A'a, ina fatan Allah Ya fitar daga tsatsonsu waɗanda zasu bautawa Allah Shi kaɗai basa haɗa Shi da wani abu**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]. Kuma wani Balaraben Ƙauye ya ganshi sai ya jawo shi ta Mayafinsa da ƙarfi har sai da Mayafin ya bar Alama a Wuyansa kuma yace: «Ya Muhammad! Kayi umurni abani daga Dukiyar Allah datake wurinka, sai Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya juyo gare shi, yayi Dariya, Sa'annan kuma ya bada umurnin abashi kyauta» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]. Kuma Haƙurinsa ya kai har ga Hadimai, Anasa –Allah Ya yarda da shi- yace: «Nayiwa Manzon Allah -Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- Hidima tsawon Shekaru Goma, na rantse da Allah bai taɓa cemin: Uffan ba, da ɗai» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Annabi -Tsira da Amincin Allah su tabbatta a

gare shi- yayi yabo ga wanda ya siffantu da Haƙuri daga cikin Sahabbansa; sai yace da Ashajju Abdulqais: «**Lallai a tare dakai akwai wasu Halaye guda biyu, Allah Yana son su: Haƙuri da Natsuwa**» [Muslim ya ruwaito shi], Kuma Abubakar –Allah Ya yarda da shi- ya wuce waninsa ne da Imani da kuma cikar kamalar sahabbantakar Annabi -Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi-, da kuma abunda ya ƙawata dashi na daga Siffofin Karamci; har Sahabbai suka masa shaida da haka; Umar -Allah Ya yarda da shi- yace: «Abubakar shine wanda yafi mu Haƙuri da ƙima».

Kuma Gwarzantaka tana cikin ƙarfin Zuciya da tabbatarta, Maganar Jahili ko aikin Wawa basa girgizata, Kuma mai tsananin Ƙarfi shine wanda yake Mallakar kansa a lokacin Fushi; sai yayi abunda ya dace dashi, amma wanda ake rinjaya a lokacin Fushinsa lallai wannan mai rauni ne, kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya yabi wanda ya mallaki kansa a lokacin Fushi, yace: «**Mai kada Mutane ƙasa bashine Mai Ƙarfi ba, Mai Ƙarfi kawai shine wanda yake mallakar kansa a lokacin Fushi**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Haƙuri da Wawa yafi Alkhairi kan fitowa a cikin Surar shi, kuma runtse ido daga Jahili yafi Alkhairi kan tarayya dashi -cikin halinsa-, kuma duk wanda ya kame kuma yayi shiru ga Jahili, lallai ya bashi cikakkar Amsa kuma ya masa Horo mai zafi, kuma wani Mutum yace da Dhirãr binul Qa'a'qa –Allah Ya yarda da shi-: «Na rantse da Allah, da zaka min zagi ɗaya, da kaji zagi goma daga gare ni, sai Dhirãr yace masa: Da zakayi Zagi

goma bazakaji koda ɗaya daga gare ni ba», kuma wani Mutum ya zagi Al-Sha'abiy –Allah Ya jiƙansa- sai ya bashi amsa da cewa: «Idan haka nake kamar yadda ka faɗa, Allah Ya gafarta min, idan kuma ba haka nake ba, Allah Ya gafarta maka».

Kuma duk wanda ya yafewa Hallitta; Allah zai masa Afuwa, Ibnul Qayyim –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Ana yiwa Bawa Mu'amala a cikin Zunubansa da irin yadda Bawa yake Mu'amalantar Mutane a cikin Zunubansu ..., kuma sakamako yana kasancewa ne daga kalar Aiki, don haka, duk wanda yayi Afuwa; Allah zai masa Afuwa, kuma wanda ya yafewa ɗan uwansa a wani laifi da yayi masa; Allah zai yafe masa laifukansa, kuma wanda ya runtse ido kuma ya kwar da kai; Allah zai yafe masa, kuma duk wanda yayi bibiyar diddigi; Allah zai masa bibiyar diddigi».

Kuma Fushi: Yana ɓata Halaye, da Ayukka, da Hankali da Mutunci, ancewa Ibnul Mubarak –Allah Ya jiƙansa- «Ka tattara mana kywawan Halaye a cikin Kalma ɗaya, sai yace: Kabar Fushi».

Kuma barin Fushi Wasiyar Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ce; wani Mutum yazo wurin Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- sai yace: «Ka min Wasiya, sai yace: **Kada kayi Fushi**, ya ƙara mai-maitawa, kuma yace: **Kada kayi Fushi**» [Bukhari ya ruwaito shi]. Sai Mutumin yace: «a lokacin da Manzon Allah Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi ya faɗi abunda ya faɗa, Sai nayi tunani, sai na fahimci lallai Fushi ya tattara dukkan Shari baki ɗaya». [Ahmad ya ruwaito shi].

Hankali yana ragewa a lokacin Fushi; sai ya kai ga yin lalatattar Magana da kuma ɓoye gaskiya, kuma daga cikin Addu'ar Annabi -Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- akwai: «**Kuma ina roƙonka** [faɗin] **kalmar Gaskiya a lokacin Yarda da Fushi**». [Nasa'i ya ruwaito shi].

Kuma Fushi yana hana yin Adalci tsakanin Mutane; Annabi -Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Kada Mai Hukunci yayi Hukunci tsakanin Mutane biyu alhali yana cikin Fushi**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Mutum yana iya Hasarar wani abu daga cikin Dukiyarsa; saboda Fushi; Jãbir –Allah Ya yarda da shi- ya ce: «Mun tafi tare da Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- a Yaƙin Baɗnu Buwãɗin ..., sai hawan raƙumi yazo kan wani daga cikin Ansãrawa sai ya kwantar da Raƙumin ya hau kansa, ya tada shi, sai Raƙumin ya ɗan cije masa, sai yace masa: Tashi mana –Allah Ya tsine maka- sai Manzon Allah Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi ya ce: **Waye wannan wanda yake tsinewa Raƙuminsa**? Sai Mutumin yace: ni ne ya Manzon Allah! sai Annabi yace: **Ka sauka daga kansa, bazaka abokance mu da Tsinanne ba, kada kuyiwa kanku muguwar Addu'a, kuma kada kuyiwa Ƴayǹanku Muguwar Addu'a, kuma kada kuyiwa Dukiyarku Muguwar Addu'a, kada ku dace da wani lokaci wanda ake roƙon Allah a cikinsa kuma Ya karɓa maku**». [Muslim ya ruwaito shi].

Ibn Rajab –Allah Ya jiƙan sa- yace: «Duk wannan yana nuni zuwa ga cewa, lallai ana iya karɓar Addu'ar Mai Fushi idan ta dace da lokacin karɓar Addu'a, kuma [yana nuni da cewa] an hanshi yin Muguwar Addu'a akansa da Iyalinsa da Dukiyarsa a cikin Fushi».

Kuma idan Mutum yayi Fushi zai faɗi abunda bai sani ba, kuma yayi Nadama ga abunda zai iya aikatawa –na bijirewa Iyaye, ko yanke Zumunta, ko rabuwa da Matarsa, ko yanke Arzikinsa, ko ƙauracewar Abokanansa gare shi, ko ta'adi ga wasu, ko furta haramtattun maganganu; na Ƙazafi da Zagi da Alfasha da sauran nau'o'an Zalunci da Ta'addanci, kuma hakan zai haifar da Damuwa, Kaɗaici, Baƙin ciki da Zama shi kaɗai, kuma ana iya masa Uƙuba da abunda ya aikata a lokacin Fushi da Haddi ko ladabtarwa ko Uƙuba a Lahira.

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya kasance yana umurtar wanda yayi Fushi da aikata sabubban dake yaye Fushin daga gareshi, sai yayi umurni da neman tsari daga Shaiɗan; saboda shine sababin Fushi da Ta'adi; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yaga wani Mutum yayi Fushi, Fuskarsa tayi launin Ja sai yace masa: «Ni nasan wata kalma da zai faɗeta da abunda yake ji ya tafi; da zai ce: Auzubillahi Mina shaiɗanir rajim; abunda yake ji zai tafi» [da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Annabi ya hana mai tsananin Fushi yin Magana face Neman tsari; sai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yace: «**Kuma idan ɗayanku yayi Fushi; to, yayi Shiru**» [Ahmad ya ruwaito shi].

Kuma idan a kusa dashi akwai Ruwan Alwala; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yace: «**Lallai Fushi daga Shaiɗan ne, kuma lallai Shaiɗan an hallicce shi daga Wuta, kuma ana kashe Wuta ne da Ruwa; don haka, idan ɗayanku yayi Fushi, to, yayi Alwala**» [Ahmad ya ruwaito shi].

Kuma ya umurce shi da ya canza yanayin dayake akai; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Idan ɗayanku yayi Fushi yana a tsaye, to, ya zauna, idan Fushi ya tafi** [shike nan], **idan kuma** [bai tafi ba] **to, ya Kishingiɗa**» [Abu Dawud ya ruwaito shi].

Kuma daga cikin Girman Mutum da ɗaukakar Himmarsa akwai: Kawar da kai daga Zage-Zage, kuma a cikin kawar da kai daga Jahili akwai: Kariya ga Mutunci da Addini, kuma yana daga cikin Siffofin Mumini:

﴿وَإِذَا خَاطَبَهُمُ ٱلْجَٰهِلُونَ قَالُوا۟ سَلَٰمًا﴾

((**Kuma idan Jahilai suka yi masu Magana sai suce: Salãma**)). [Furqãn: 63].

Kuma wajibi ne ga wanda yayi Fushi ya: Tuna Haƙurin Allah akansa, kuma yaji tsoron UƘubarSa; domin Ikon Allah akanka yafi ƙarfin ikonka akan Hallittu, kuma ya tuna abunda Fushi yake kaiwa gare shi na Nadãma da Hasara, kuma ya kiyaye munin ƙarshen da Ƙiyayya da ɗaukar Fansa da kuma Dariyar Maƙiya da zasuyi ga Musibarsa, kuma shi Mumini yana tuna Ladar Afuwa da Yafiya mai kyau, da kuma kasancewar Duniya wulaƙantatta ce wadda bata kai ayi Fushi dominta ba.

Kuma duk wanda bai kasance mai Haƙuri ba; wajibi

ne ya koyawa kansa yin Haƙuri, Al-ahnaf ya ce: «Ni ba mai Haƙuri ne ba, amma ina ƙoƙarin koyawa kaina Haƙurin», kuma idan Mutum ya saɓawa abunda Fushinsa yake umurtarsa da yi, kuma ya yaƙi kansa akan haka; lallai, Sharri da Fushi zai barshi.

**Ina neman Tsarin Allah daga Shaiɗan Jefaffe.**

﴿ خُذِ ٱلۡعَفۡوَ وَأۡمُرۡ بِٱلۡعُرۡفِ وَأَعۡرِضۡ عَنِ ٱلۡجَٰهِلِينَ ﴾

**((Kayi riƙo da Afuwa kuma kayi umurni da abu mai kyau kuma ka kawar da kai daga Jahilai)).** [Suratul A'arãf: 199].

Allah Yayi min Albarka tare daku a cikin Alqur'ani mai Girma ...

## HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarSa da kuma Ni'imominSa, kuma ina shaida cewa lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya; don girmamawa ga Sha'aninSa, kuma ina shaida cewa lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Yabon Allah ya tabbata a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa tareda Aminci mai ƙaruwa.

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Duk wanda ya shuka Huƙuri, lallai zai girbi ƴayan Aminci, kuma ana sanin Haƙuri ne a lokacin Fushi, kuma mafi Alkhairin Mutane shine: wanda baya saurin Fushi, kuma mai saurin sauka daga Fushin, kuma mafi Sharrinsu shine Mai sauri Fushi kuma mai wuyar sauka daga gareshi zuwa ga Yarda.

Kuma daga cikin cikar Hankali akwai: wanda idan yayi Fushi, Fushinsa ba zai shigar dashi cikin Ɓarna ba, kuma wanda idan ya yarda, yardarsa bazata fitar dashi ba daga Gaskiya.

Kuma kashedinka da Gaugawa; domin idan kayi Gaugawa zaka kuskure rabonka, kuma ka kasance mai sauƙin kai, mai laushi ga na kusa dana nesa.

Kuma Mai Hankali yana turewa kansa Fushin Mutane – ta hanyar barin tozartasu, ko yi masu Izgili ko rena

(1) Yaku Musulmi.

Matsayinsu, ko Ta'adi ga Dukiyarsu ko cin Mutuncinsu; ta hanyar: Giba ko Ƙiren Ƙarya ko Ƙazafi.

Sa'annan kusani cewa: Lallai Allah ya umurce ku da yin Salati da Sallama ga AnnabinSa....

# KARAMCI [1]

Godiya ta tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrorin kawunan mu da miyagun Ayukkan mu, wanda Allah Ya shiryar dashi babu mai ɓatar dashi, kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida lallai Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi Salati da Aminci mai yawa a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Amma Ba'adu[2]:**

Kuji tsoron Allah -yaku bayin Allah- haƙiƙanin tsoro, kuma ku kiyaye Shi a ɓoye da lokacin ganawa.

**Ayyuhal Muslimŭn[3]:**

Allah Mai Tsarki Mawadaci ne da ZatinSa daga waninsa, kuma Yana da cikar kamala ta kowace Fuska a cikin ZatinSa da SiffofinSa da Ayukkansa, Sunayensa kyawawa sun kai Matuƙa a cikin Kyau ƙayatarwa, kuma SiffofinSa Maɗaukaka sun kai matuƙa a cikin Ɗaukaka

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a Shida ga watan Rajab, Shekara ta Dubu Ɗaya da Ɗari Huɗu da Talatin da Ɗaya bayan Hijira.

(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

(3) Yaku Musulmi.

da Girma.

Kuma daga cikin Sunayen Allah Mai tsarki akwai: **Alkarimu** [Mai Karamci]; Ya bamu abunda muka roƙe Shi, kuma Yayi mana Ni'imar abunda bamu roƙe Shi ba, kuma Yana jin Kunyar Bawa ya ɗaga Hannayensa zuwa gare shi ya dawo dasu ba komai a ciki a tozarce.

ƘofarSa a buɗe take ga wanda ya roƙe Shi, kuma ArzikinSa da TaskokinSa suna kwarara ga BayinSa basa ragewa saboda Kyauta; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Hannun Allah a cike yake, ciyarwa bata rage shi, Mai yawan kyauta ne Dare da Yini,** kuma yace: **Shin bakwa ganin abunda ya ciyar tun lokacin da ya hallicci Sama da Ƙasa? Lallai abunda yake cikin HannunSa bai taɓa ragewa ba**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Shi Mai Karamci ne Yana kusa da mai roƙon Sa, babu wani Shamaki tsakanin Sa da buƙatocin bawanSa:

﴿ وَإِذَا سَأَلَكَ عِبَادِي عَنِّي فَإِنِّي قَرِيبٌۖ أُجِيبُ دَعْوَةَ ٱلدَّاعِ إِذَا دَعَانِۖ ﴾

**((Kuma idan BayiNa suka tambayeka gameda Ni, lallai Ni ina kusa, Ina karɓar roƙon mai roƙo idan ya kirani)).** [Suratul Baqara: 186].

Kuma Yana bawa BayinSa fiyeda abunda suka yi buri, kuma yazo a cikin Hadisin Qudsiy: «**Ni na tanadawa BayiNa na ƙwarai abunda Ido bai taɓa gani ba, kuma Kunne bai taɓa ji ba, kuma bai taɓa ɗarsuwa ba a Zuciyar wani Mutum**». [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Haƙiƙa Ya hana BawanSa ya ƙaranta roƙon idan ya roƙeShi, sai dai ya yawaita roƙon Allah abunda duk yake so; domin kyautar Allah mai yawa ce, don haka, ka kai buƙatunka wurinSa; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Kada ɗayanku idan zai yi Addu'a yace: Ya Allah Ka gafarta mini idan Kaga dama; sai dai ya ƙarfafa roƙon kuma ya girmama kwaɗayi** –Ma'ana: ya roƙe Shi abunda yake so-; **domin babu abunda yakeda girman da Allah bazai iya badashi ba**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma LittafinSa Mai tsarki Mai karamci ne:

﴿إِنَّهُۥ لَقُرۡءَانٞ كَرِيمٞ﴾

((**Lallai shi Al-Ƙur'ani ne mai Karamci**)) [Suratul Wãqi'ah: 77]. Duk wanda ya karanta shi kuma yayi aiki dashi; Allah zai Karrama shi.

Kuma a cikin bada Lada, Yana bada lada mai yawa ga aiki kaɗan na ƙwarai:

﴿مَن جَآءَ بِٱلۡحَسَنَةِ فَلَهُۥ عَشۡرُ أَمۡثَالِهَاۖ﴾

((**Duk wanda yazo da aiki na ƙwarai yanada kwatan-kwacinsa goma**)) [Suratul An'ãm: 160].

Kuma Yana ninkawa fiye da haka ga wanda Yaso, kuma «**Wanda yayi nufin yin aiki na ƙwarai sai bai yi ba; za'a rubuta mashi aiki na ƙwarai**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma Yana sakawa wanda yayi maSa biyayya a cikin gajerun shekarun Rayuwa da

Ni’ima Madawwamiya a Lahira, kuma Yana basu falalar ganin FuskarSa Mai tsarki.

Kuma Karamci siffar yabo ce ga Mutum, kuma Alama ce ta tsaftar Zuciya da tsaftar abunda yake ɓoye, Shaikhul Islam –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Manyan Falaloli sune: Ilimi, da Addini, da Karamci da kuma Jarumta», kuma yana daga cikin ɗabi’un Alkhairi; baya kasancewa a cikin Mumini face sai Allah Ya ɗaukaka shi dashi, kuma haƙiƙa Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kwaɗaitar akansa farkon zuwansa garin Madinah da faɗarsa: «**Yaku Mutane! ku yaɗa Sallama, ku ciyar da Abinci, kuma kuyi Sallah a cikin dare lokacinda Mutane suke Bacci; sai ku shiga Aljanna da Aminci**» [Tirmizi ya ruwaito shi].

Kuma shi Ibadah ne daga cikin Ibadodi, kuma kyawawan Halaye suna daga cikin mafi nauyin ababe a cikin Ma’auni, Al-Hassanul Basri –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Halaye kywawa sune: Karamci da Kyauta» kuma a Safiyar kowane yini, Mala’iku biyu suna saukowa «**Sai ɗayansu yana cewa: Ya Allah Ka mayewa mai ciyarwa, kuma ɗayan yana cewa: Ya Allah Ka lalatawa mai riƙewa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma Musulmi ana gasarsa akan yin wannan Ibadar; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Babu Hassadda sai a cikin ababe biyu: Mutum wanda Allah Ya bawa Dukiya; sai Allah Ya ɗora shi akan bada ta a cikin Gaskiya, da kuma Mutum wanda Allah Ya bashi Hikima; kuma yana Hukunci da ita yana koyarda ita**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Allah Mai tsarki Mai Ilimi ne Yana son Malamai, kuma Mai Karamci ne Yana son Masu Karamci, Mai kyautatawa ne Yana son Masu kyautatawa, kuma Karamci yana daga cikin ɗabi'un Mazaje, kuma halin Mutanen kirki ne, kuma Annabawan Allah sune mafiya karamcin Mutane; Ibrahim–Aminci ya tabba a gare shi- Manzannin UbangijinSa sunzo masa a cikin siffar Mutane –bai san cewa Mala'iku ne ba-; sai ya Karramasu kuma ya kyautata hakan, ya yanka musu ɗan Maraƙi mai ƙiba, kuma ya gasashi akan Duwatsu masu zafi, kuma ya kawo musu shi cikin gaugawa:

﴿فَمَا لَبِثَ أَن جَآءَ بِعِجۡلٍ حَنِيذٖ﴾

((**Bai jima ba sai gashi yazo da ɗan Maraƙi gasasshe)**) [Suratu Hũd: 69]. Kuma Allah Ya siffanta Musa -Aminci ya tabbatta a gare shi- da cewa lallai shi Mai karamci ne:

﴿وَلَقَدۡ فَتَنَّا قَبۡلَهُمۡ قَوۡمَ فِرۡعَوۡنَ وَجَآءَهُمۡ رَسُولٞ كَرِيمٌ﴾

((**Kuma haƙiƙa kafinsu Mun jarabci Mutanen Fir'auna kuma Manzo Mai karamci yazo masu**)) [Suratul Dukhãn: 17].

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yace gameda Yusuf -Aminci ya tabbatta a gare shi-: «**Mai Girma, ɗan Mai Girma, ɗan Mai Girma, ɗan Mai Girma**» [Bukhari ya ruwaito shi].

Kuma Annabin mu Muhammad ya kasance yafi Mutane kyauta, kuma ya fisu kyawun kyauta, Ransa mai Karamci ne, kuma Hannunsa mai badawa ne, ba'a taɓa

roƙonsa wani abu ba da ɗai yace A'a; Wani Mutum ya roƙe shi dabobbi da zasu cika kware tsakanin Duwatsu biyu kuma ya bashi su, sai Mutunen ya koma zuwa ga Mutanensa yace; «Ya Mutunena! Ku Musulunta; domin Muhammad yana bada wata irin kyauta, da baya tsoron Talauci» [Muslim ya ruwaito shi].

kuma wata rana ya saka wani gwado sai wani Mutum yace: «Ka tufatar dani shi, kai, lallai yana mai ya fishi kyau! –Sai yabasa shi-» [Bukhari ya ruwaito shi], kuma kyautuka suna zuwa masa sai ya rabasu tsakanin Mutane.

A Yaƙin Hunain ya bawa Swafwãn ɗan Umayyah dabbobi Ɗari, ya ƙara masa wasu Ɗari, ya ƙara masa wasu Ɗari. Swafwãn yace: «Na rantse da Allah, haƙiƙa Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya bani abunda yabani alhali shine mafi ƙyamar Mutane a gare ni, amma bai gushe yana bani ba har saida ya zama tabbas shine mafi soyuwar Mutane a gare ni» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma wata dukiya mai girma daga Bahrain tazo masa –kuma wannan dukiyar ita ce mafi yawan dukiya da tazowa Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi-, sai yace: «Ku zubeta a cikin Masallaci, sai ga Abbas yazo masa, sai yace: Ya Manzon Allah! ka bani; domin ni na fanshi kaina da Aqeelu, sai Annabi yace: Ɗiba, sai ya kwamfata akan Tufafinsa, sa'annan yayi yunƙurin tashi amma ya kasa miƙewa da dukiyar, sai wani sashe na dukiyar ya zube daga gareshi, sa'annan sai ya ɗorata akan Kafaɗarsa» [Bukhari ya ruwaito shi].

Da ace yanada abunda yafi haka, da ya bada shi don

neman yardar Allah. Mai tsira da Aminci yace: «Da ace inada kwatan-kwacin Zinari na Dutsen Uhud, ba zanji daɗin kwana uku su wuce ba, alhali akwai wani abu daga cikinsa ba sai abunda zan ajiye don biyan bashi» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Karamcinsa ya kai yana yiwa Mutane Alƙawarin Dukiya kafin tazo masa; yacewa Jãbir: «**Haƙiƙa, da Dukiyar Bahrain zata zo mana; da na baka kamar Haka da Haka da Haka**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], Ibn Rajab –Allah Ya jiƙansa- yace: «Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kasance yana bada wata irin Kyauta wadda take buwayar Sarakuna; kamar su: Kisrã da Qaisar»

Kuma mafi Karamcin Mutane bayan Annabin mu Muhammad –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- sune Sahabbansa waɗanda suka kasance daban daga sauran Mutane; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yayi umurni da yin Sadaka; sai Umar yazo da rabin Dukiyarsa, kuma Abubakar yazo da Dukiyarsa baki ɗaya, kuma Uthman shine wanda ya shirya rundunar nan data yi tafiya lokacin wahala; kuma har Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yana mai yaba masa yace masa: «**Ba wani abunda Uthman zai yi wanda zai cutar dashi bayan yau**» [At-tirmizi ruwaito shi].

Kuma Abu ɗalha –Allah Ya yarda dashi- ya karɓi baƙuncin wani Mutum sai Matarsa tace masa: «Bamuda komai sai abincin Yara, sai yace: ki shirya Abincinki, kuma ki kunna Fitilarki, kuma idan yaranki suka buƙaci

abinci dare, ki sakasu Bacci; sai ta shirya Abincinta, ta kunna Fitilarta, kuma ta saka yaranta Bacci, sai ta tashi kamar tana gyara Fitilarta sai ta kasheta, sai suka nuna masa [baƙon] kamar suna cin Abinci ne, sai sukayi Bacci ba komai a cikin cikinsu, da suka wayi gari sai yayi sammako zuwa wurin Manzon –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- sai yace: **Allah Yayi Dariya wannan Dare** – ko: **Yayi Mamaki- da abunda kuka aikata**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]. Kuma «Ibn Umar ya kasance baya cin abinci har sai anzo masa da wani Miskini wanda zaici tare dashi» [Bukhari ya ruwaito shi].

Kuma Karamci yana da ƙofofi maban-banta; ciyar da kai Kyautatawa ne; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Idan Allah Yabawa ɗayanku Alkhairi; to, ya fara da kansa da Iyalan gidansa**» [Muslim ya ruwaito shi], kuma ciyarda Mata da Ɗa abunda zai biya buƙatarsu yana daga cikin mafi girman fuskoki, Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:«**Dinarin daka ciyar dashi a cikin hanyar Allah** –Jihadi-, **da Dinarin daka ciyar dashi wurin ƴanta Wuya, da Dinarin daka yi Sadaka dashi ga Miskini, da Dinarin daka ciyar ga Iyalinka; duk wanda yafi su girman Lada shine; wanda ka ciyar ga Iyalinka**». [Muslim ya ruwaito shi], kuma yace: «**Kuma lallai Musulmi idan ya ciyar da Iyalinsa, kuma yana neman ladar haka, zai kasance masa Sadaka ne**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma yana daga cikin Karamci da cika Alƙawari: Girmama Abokin Mahaifa, kuma Girmama Maƙoci yana

daga cikin Imani, Annabi Yabo da Aminci su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Wanda ya kasance yayi Imani da Allah da ranar Ƙarshe; to, ya girmama Maƙocinsa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]. Kuma yana daga cikin kyautata Maƙwabtantaka aika musu da Abinci, da kuma basu daga abunda yake ciyar da Iyalinsa, Mai tsira da Aminci ya ce: «**Idan ka girka Romo, ka yawaita Ruwanta, kuma ka tuna da Maƙotanka** –Ka aika masu da ita» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma Karrama baƙo yana daga cikin Mutunci da Halaye masu Karamci; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Kuma wanda ya kasance yayi Imani da Allah da ranar Ƙarshe; ya Karramma Baƙonsa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]

Kuma wanda bashida Dukiya; to, Maganarsa tazama mai Kyau, domin Kalma mai kyau tana daga cikin sakin hanu kuma nau'i ce ta kyauta; Annabi –Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- ya ce: «**Ku nemi kariya daga Wuta koda da tsagin Dabino ne, idan kuma baka samu ba, to kayi da Kalma mai Kyau**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma kyautatawa ga wasu ta hanyar yaye Baƙin ciki da Damuwa yana daga cikin Kyauta; Annabi Mai tsira da Aminci ya ce: «**Duk wani abun Ƙwarai Sadaka ne**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], Aliyyu –Allah Ya yarda dashi- ya ce: «Kada kaji kunyar bada kaɗan, Hanawa yafi shi zama kaɗan, kuma kada kaji tsoron bada mai yawa; domin kai kafi abun yawa».

Kuma mafi Karamcin ayukka shine wanda akayi shi

domin Fuskar Allah, kuma mafi girman Karamci daga cikin Mutane sune mafi yin Biyayya ga Allah; Allah Mai tsaaki yace:

﴿إِنَّ أَكۡرَمَكُمۡ عِندَ ٱللَّهِ أَتۡقَىٰكُمۡۚ﴾

((**Lallai Mafi Girma daga cikinku a wurin Allah sune waɗanda suka fiku Taƙawa**)) [Suratul Hujurãt: 13].

Kuma ancewa Annabi–Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- «Waye mafi Girma daga cikin Mutane? yace: **Mafi girmansu shine wanda yafisu Taƙawa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Don haka, ka ƙawatu da Karamcin Dukiya, kuma ka zama mai Karamci da Kanka da Matsayinka da Dukiyarka, kuma ka kwaɗaitu akan yin Biyayya ga UbangijinKa da BautarSa; sai ka kasance daga cikin Masu jin daɗi.

## Ina neman tsarin Allah daga Shaiɗan jefaffe

﴿وَمَا تُنفِقُواْ مِنۡ خَيۡرٖ يُوَفَّ إِلَيۡكُمۡ وَأَنتُمۡ لَا تُظۡلَمُونَ﴾

((**Kuma duk abunda kuka ciyar na daga Alkhairi za'a saka maku kuma ba za'a zalunceku ba**)) [Suratul Baƙara: 272]

Allah Yayi min Albarka tare daku a cikin Alƙur'ani mai Girma ...

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarSa da kuma Ni'imominSa, kuma ina shaida cewa lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya; don girmamawa ga Sha'aninSa, kuma ina shaida cewa lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Yabon Allah ya tabbata a gare shi da iyalansa da Sahabbansa tareda Aminci mai yawa.

**Ayyuhal Muslimŭn**[1]**:**

Karamci Marufin Aibobi ne, kuma yana daga cikin abubawa kyawawa na Addini, kuma alama ne na kyautata zato ga Allah, kuma ɗabi'a ne dake tsakanin Ɓarna da Rowa; Allah Mai girma da Ɗaukaka ya ce:

﴿وَٱلَّذِينَ إِذَآ أَنفَقُواْ لَمۡ يُسۡرِفُواْ وَلَمۡ يَقۡتُرُواْ وَكَانَ بَيۡنَ ذَٰلِكَ قَوَامٗا﴾

**((Kuma da waɗanda idan suka ciyar basa Ɓarna kuma basa ƙwauro, kuma a tsakanin wannan dai-daito yake))** [Furqãn: 68].

Kuma Mai Karamci shine wanda Allah Ya karramma shi da yin Biyayya koda kuwa Talaka ne, kuma Wulaƙantacce shine wanda Allah Ya Wulaƙanta shi da yin Saɓo koda kuwa Mawadaci ne; kuyi kwaɗayi akan

(1) Yaku Musulmi.

Karamci kuma ku ƙawatu da shi; zaku rabauta, kuma zaku samu Alkhairi daga Ubangijinku.

Sa’annan kuma ku sani lallai Allah Ya umurceku da yin Slati da Sallama ga Annabinmu ...

# CIKA ALƘAWARI [1]

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga Sharrin kawunan mu da munanan ayukkan mu, wanda Allah ya shiryar dashi babu mai ɓatar dashi kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa: lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi Yabo da Aminci mai yawa a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Amma Ba'adu[2]:**

Yaku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro; kuma kuyi riƙo da Musulunci da Igiya mai ƙwari.

**Ayyuhal Muslimŭn[3]:**

Ran Mutum yana cika ne da bautarsa ga Allah da kuma kyakykyawar Mu'amalarsa da Hallittu, sai Allah Ya shar'antawa BayinSa riƙo da ababe Maɗaukaka, kuma Ya hanasu daga Maƙasƙanta, kuma cika Alƙawari

---

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a Ashirin da Biyar ga watan Muharram, Shekara ta Dubu Ɗaya da Ɗari Huɗu da Talatin da Biyu bayan Hijira.

(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

(3) Yaku Musulmi.

yana daga cikin ginshiƙan abunda ake gina Jama'a da kuma samun tsayuwar Rayuwa, kuma yana daga cikin Halaye masu kyau da Siffofi Maɗaukaka.

Kuma ma'anarsa shine: Yarda da Falala, da Sakamako mai kyau ga wanda yayi maka Alkhairi, ko ya maka wani taimako.

Kuma mafi girman Alƙwarin da ya wajaba ayi riƙo da shi kuma a cika shi, shine: Cika Alƙawarin Allah; Na ka bauta maSa Shi kaɗai kada ka haɗa shi da wani abu; kamar yadda

Allah Mai tsarki Yace:

﴿وَأَوۡفُواْ بِعَهۡدِيٓ أُوفِ بِعَهۡدِكُمۡ﴾

((**Kuma ku cika AlƙawariNa in cika muku Alƙawarinku**)). [Suratul Baƙarah: 40].

Kuma mafi girman waɗanda suka cika wannan Alƙawarin daga cikin Hallittu sune Manzannin; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَإِبۡرَٰهِيمَ ٱلَّذِي وَفَّىٰٓ﴾

((**Kuma da Ibrahim wanda ya cika Alƙawari**)). [Suratul Najm: 37].

Ibn Katheer -Allah ya jiƙansa- ya ce: «Ma'ana: ya cika duk abunda aka Shar'anta masa; kuma yayi aiki dashi –Yabon Allah ya tabbata a gare shi».

Kuma daga cikin cika Alƙawari mai girma akwai: Cika Alƙwarin Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- na yi masa Biyayya, da bin

Shiriyarsa, da bibiyar gurabunsa; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿ وَمَآ ءَاتَىٰكُمُ ٱلرَّسُولُ فَخُذُوهُ وَمَا نَهَىٰكُمۡ عَنۡهُ فَٱنتَهُواْۚ ﴾

((**Kuma duk abunda Manzo yazo maku dashi kuyi riƙo dashi, kuma duk abunda ya haneku ku hanu**)). [Suratul Hashr: 7].

Kuma cika Alƙawari yana daga cikin Halayen Mazaje, kuma yana nuni zuwa ga girman Mutum da kyawun Hali, kuma Manzanni sune mafi girman masu cika Alƙawari daga cikin Mutane; Musa yasan haƙƙin ɗan uwansa Haruna –Aminci ya tabbata a gare su-; sai ya roƙi UbangijinSa da Ya haɗa su tare a cikin Manzanci:

﴿وَٱجۡعَل لِّي وَزِيرٗا مِّنۡ أَهۡلِي ۝ هَٰرُونَ أَخِي ۝ ٱشۡدُدۡ بِهِۦٓ أَزۡرِي ۝ وَأَشۡرِكۡهُ فِيٓ أَمۡرِي﴾

**((Kuma Ka sanya min wani Mataimaki daga Mutanena ⁕ Haruna ɗan uwana ⁕ Ka ƙarfafi bayana dashi ⁕ kuma Ka shigar dashi a cikin Al'amarina))** [Suratu Ɗãha: 29-32].

Kuma Annabin mu Muhammad –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya kasance mai cika Alƙawari ga waɗanda suka taimake shi don isar da Manzancin UbangijinSa; Al-Muƭ'im bin Adiy ya hana Mush'rikai cutar da Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- kafin Hijira; sai Annabi ya kiyaye masa wannan kyautatawar dayayi gare shi kuma yace gameda ribatattun Yaƙin Badr: «**Da ace Al-Muƭ'im bin Adiy yana raye sa'annan yayi min magana akan waɗancan Ƙazaman da na sake masa**

**su**» [Bukhari ya ruwaito shi].

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya kasance mai cika Alƙawari ne tareda Sahabbansa; Abubakar –Allah Ya yarda dashi- shine mafi Falalar Sahabbai, ya taimaki Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- da Dukiyarsa da Kansa, kuma ya kasance shine wanda yafi duk sauran Sahabbai abokantakarsa; sai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yace: «**Da zan riƙi badaɗayi a cikin Al'ummata dana riƙi Abubakar, sai dai shi ɗan uwana ne kuma Sahabina ne**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya aika Uthman –Allah Ya yarda dashi- a ranar Hudaibiyah zuwa ga Ƙuraishawa a Makkah, sai ya jinkirta dawowa gare shi; sai Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya umurci Sahabbansa da yin Muba'yi'ah; sai Mutane sukayi Muba'yi'ah sa'annan saboda cika haƙƙin Uthman na abunda yayi na Hidimar Musulunci- sai yace: «**Lallai Uthaman yana a kan Buƙatar Allah da Buƙatar AnnabinSa,** sai ya ɗora ɗayan Hannayensa akan ɗayan –kuma yace: **Wannan** [Hannun] **na Uthman ne**-; sai Hannun Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ga Uthman ya kasance mafi Alkhairi kan Hannayensu ga kawunansu» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma yayi sallah ga shahidan Uhudu bayan shekara takwas da yin shahadarsu, yana kamar mai yi musu bankwana [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]. Kuma

yayi Sallah ga Ƙabarin wata baiwa Baƙa wadda ta kasance tana share Masallaci, kuma da Ansarawa [Mutanen Madinah] suka taimaki Muhãjirai sai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yayi masu Addu'a da kuma zuriyarsu yace: «**Allah Ka gafartawa Ansãru da ƴaƴan Ansãru da ƴaƴan ƴaƴan Ansãru**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma babu wani ɗaya daga cikin Sahabbai dayayi wani Alkhairi ga Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- face ya sakama masa akai, Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Ba wanda yakeda wani Alkhairi da yayi a garemu face tabbas mun saka masa sai Abubakar; lallai shi yanada wani Alkhairi da yayi a garemu Allah ne zai saka masa shi a ranar Ƙiyama**» [At-tirmizi ya ruwaito shi], kuma yayi umurni da a kiyaye ƙaunar Sahabbansa baki ɗaya bayan Mutuwarsa; sai yace: «**Kada ku zagi Sahabbaina, kada ku zagi Sahabbaina; na rantse da Wanda raina yake HannunSa! Da ace ɗayanku zai ciyar da misalin Dutsin Uhud na zinari ba zai kai Mudun ɗayansu ba ko rabinsa**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma cika Alƙawarinsa ya kai har zuwa ga Al'ummarsa, kuma wannan zai kasance a Filin tsayuwa mai girma, sai yace: «**Kowane Annabi yanada Addu'a da aka karɓa masa, sai kowane Annabi ya gaggauta roƙonsa, amma ni na ɓoye roƙona ya zama Ceto ga Al'ummata a ranar Ƙiyama, kuma –cikin yardar Allah- zai samu duk wanda ya mutu daga cikin Al'ummata alhali baya haɗa Allah da komai**»

[Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma akan wannan Halin na cika Alƙawari Sahabbai –Allah Ya yarda dasu- suka kasance; da aka karɓi Rayuwar Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- sai Abubakar yacewa Sahabbai: «Duk wanda yakeda wani Alƙawari ko Bashi akan Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yazo, Jãbir yace: sai na miƙe, nace: lallai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: **Da Dukiyar Bahrain zata zo mana dana baka kamar haka, da kamar haka, da kamar haka**, sai Abubakar ya kwamfato sau ɗaya, sa'annan yace min: Ƙirgata, sai na ƙirgata, takai Dubu ɗari biyar, sai yace: ɗauki irinta sau biyu» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Abubakar –Allah Ya yarda dashi- ya tafiyar da Rundunar Usama bin Zaid tareda ana tsananin buƙatarta bayan Mutuwar Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi-, kuma ya kasance yana cewa: «Ba zan bar wani Al'amari wanda Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya kasance yana aikatawa ba face sai na aikata shi».

Kuma Sahabbai –Allah Ya yarda dasu- sun kiyayewa Abubakar Matsayinsa da kuma gabatarsa a cikin Musulunci; sai suka haɗu akan yi masa Muba'yi'ah a matsayin Khalifan Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi-, kuma Abubakar ya san matsayin Umar wanda Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya bashi, domin Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- yana yawan faɗin «**Nazo ni da Abubakar da Umar, kuma**

**nashiga ni da Abubakar da Umar, kuma na fita ni da Abubakar da Umar**» sai Abubakar yayi Wasici da Khalifanci ga Umar a bayansa.

Kuma cika Alƙawari yana ƙara ƙarfafa idan ya shafi Iyaye; domin sun wahala saboda samun hutunka, kuma sun ƙi Bacci don kasamu yin Bacci, kuma Uba ya wahala don neman ababen Rayuwarka, kuma Mahaifiyarka ta ɗauki cikinka cikin Wahala kuma ta Haifeka a cikin Wahala, kuma farkon Wajibin da Allah Ya farlanta shi daga cikin Haƙƙoƙan Hallittu shine Biyayya ga Mahaifa; Allah Yace:

﴿ وَقَضَىٰ رَبُّكَ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُ وَبِٱلۡوَٰلِدَيۡنِ إِحۡسَٰنًاۚ ﴾

((**Kuma Ubangijinka Ya hukunta kada ku bautawa kowa sai Shi, kuma gameda Mahaifa biyu ku kyautata**)) [Suratul Isrã: 23].

Kuma daga cikin cika Alƙawari a garesu akwai: Yi masu Addu'a:

﴿وَقُل رَّبِّ ٱرۡحَمۡهُمَا كَمَا رَبَّيَانِي صَغِيرٗا﴾

((**Kuma kace, Ubangiji Kayi masu Rahama kamar yadda suka reneni ina ƙarami**)). [Isrã: 24].

Kuma da yi masu biyayya a cikin abunda ba saɓon Allah ba, da kuma aikata abu mai kyau a gare su, da shigar da farin ciki a cikin Ransu, kuma daga cikin Biyayya garesu: suga sakamakon ƙoƙarin dasukayi na tarbiyar ƴaƴansu ta hanyar tsayuwa kan Addini da kuma aikin ƙwarai, kuma daga cikin cika Alƙawari a garesu akwai: Girmama Abokinsu bayan Mutuwarsu.

Wani Balaraben Ƙauye ya wuce ta wurin Ibn Umar –Allah Ya yarda dasu- sai Ibn Umar yace masa: «Ashe ba kai ne wane ɗan wane ba, yace: Eh; sai Ibn Umar ya bashi Jaki, kuma yace: Ka hau wannan; da kuma Rawani, yace: Ka ɗaura wannan akanka, sai wani daga cikin Almajiransa yace masa: Allah Ya gafarta maka! Ka bawa wannan Balaraben Ƙauyen Jakin da kake hutawa akansa, kuma ka bashi Rawanin da ka kasance kana ɗaure kanka dashi, sai yace: Ni naji Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa: **Lallai yana daga cikin mafi girman biyayya: Mutum ya sada zumuntar iyalan masoyan Mahaifinsa a bayan ya bada baya** –wato: bayan Mutuwarsa- kuma Babansa Abokin Umar ne» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma daga cikin riƙon Alƙawari akwai cika Alƙawari tsakanin Ma'aurata; Tabbas, Ƙulli mai ƙarfi ya haɗasu; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿ وَأَخَذْنَ مِنكُم مِّيثَٰقًا غَلِيظًا ﴾

((**Kuma sun riƙi Alƙawari mai kauri daga gare ku**)) [Suratul Nisa'i: 21].

Kuma Khadijah ƴar Khuwailid –Allah Ya yarda da ita- ta taimaki Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- da Dukiyarta, kuma ta kiyaye Alƙawarinsa, kuma an arzuta shi da ƴaƴa daga gareta, kuma ita ce farkon wadda ta gaskata shi kuma tayi Imani dashi daga cikin Mata, kuma itace sababin tabbatuwar zuciyarsa a farkon saukar wahayi, da kuma ƙarfin azamarsa, kuma ta kasance Mafi Alkhairin Mata ga Mijinta a cikin Rayuwarta, Ibn Hajar –Allah Ya jikansa-

ya ce: «Ta kasance mai kwaɗayi akan samun yardarsa da duk abunda take iyawa, kuma bata taɓa yin abunda zai Fusata shi ba ko sau ɗaya».

Sai Manzon –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya mayar da wannan riƙon Alƙawarin nata da wani irin cika Alƙawari mai girma daga gare shi, don haka, ya kasance mai godewa ga kyautatawarta, kuma ya ci-gaba da ambatonta bayan Mutuwarta, kuma yana cewa gameda ita «**Lallai ni an arzuta ni da Ƙaunarta**» [Muslim ya ruwaito shi], «Wani lokaci yakan yanka Akuya, sa'annan ya yayyanka ta gunduwa-gunduwa, sa'annan ya aika da ita ga Abokanan Khadijah, kuma yace: **Lallai ita ta kasance kaza, ta kasance kaza, kuma inada ƴaƴa daga gareta**» [Bukhari ya ruwaito shi].

Al-Nawawee –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «A cikin wannan baki ɗaya akwai nuni zuwa ga kyawon riƙon Alƙawari da kiyaye Ƙauna, kuma da kula da Alfarmar Aboki da zama a cikin rayuwarsa da bayan Mutuwarsa, da kuma karrama Iyalin wannan Abokin».

Kuma daga cikin cika Alƙawari akwai: Son Malamai da girmama su da ƙaddarasu; domin sune suke ɗauke da Addini da kuma gadon Manzanni, Al-Ɗahawi –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Kuma Malaman Magabata daga cikin Magabata dana bayansu –daga Tabi'ai Ma'abota Hadisi da athari, kuma Ma'abotan Fiqhu da nazari- ba'a ambatonsu sai da abu mai Kyau», Imamu Ahmad –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Tun shekaru Talatin dasuka wuce ban taɓa bacci ba, face sai nayiwa Shafi'i Addu'a kuma

na nema masa Gafara».

Kuma Aboki yanada riƙon Alƙawari da yake tabbata ta hanyar godiya ga Ayukkansa da kiyaye Sirrinsa da Ƙaunarsa, da kuma yabo mai kyau a gare shi, da kare isar cuta zuwa gare shi, da kuma yi masa kyauta da ƴaƴansa, kuma duk wanda ya kyautata maka; lallai ka saka masa akai, idan kuma bakada abunda zaka saka masa dashi; to, kayi masa Addu'a, itama tana daga cikin biyan kyauta.

**Ina neman tsarin Allah daga Shaiɗan Jefaffe**

﴿هَلۡ جَزَآءُ ٱلۡإِحۡسَٰنِ إِلَّا ٱلۡإِحۡسَٰنُ﴾

((**Ashe kyautatawa tanada wani sakamako face Kyuatatatawa**!)) [Suratul Rahmãn: 60].

Allah Yayi min Albarka tare daku a cikin Alƙur'ani mai girma ...

## HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarSa da kuma Ni'imominSa, kuma ina shaida cewa lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya; don girmamawa ga Sha'aninSa, kuma ina shaida cewa lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Yabon Allah ya tabbata a gare shi da iyalansa da Sahabbansa tareda Aminci mai ƙaruwa.

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Cika Alƙawari ya ƙunshi Gaskiyar Harshe da Aiki a tare, kuma cika Alƙawari yana haifar da wani abun kwaɗayi da farin ciki acikin Zuciyar Ma'abocinsa wanda bashida iyaka, kuma ya haifar da kwaɗayin biyayya da sakawa a cikin Zuciyar wanda akayiwa, kuma duk wanda yayi Inkarin Alkhairi lallai wannan yana daga cikin wanda Himmarsa ta kasa daga riƙon Alƙawari, kuma Aikin kyauta da waninsa ya kasance don neman Yardar Allah ne, kuma kada kayi baƙin ciki don wani yaƙi mayarda Alkhairin da ka yi masa; domin kai kana neman Ladar Alkhairin ne daga Allah ba daga Mutum ba, kana mai Aiki da Faɗin Allah:

﴿إِنَّمَا نُطْعِمُكُمْ لِوَجْهِ ٱللَّهِ لَا نُرِيدُ مِنكُمْ جَزَآءً وَلَا شُكُورًا﴾

**((Mu kawai Muna ciyar daku ne domin neman**

---

(1) Yaku Musulmi.

**yardar Allah bamu neman wani sakamako daga wurinku ko godiya**)) [Suratul Insãn: 9].

Ku kwaɗaitu akan cika Alƙawari; domin a cikin yin haka akwai samun Amincin Zuciya da kuma ci-gabanta, kuma kuyi ƙoƙari a cikin yin ƙawa da kowane Halin Girma, da kowace Siffa abar godewa; domin hakan shine Adireshin cin Nasara da Rabauta.

Sa’annan kuma kusani, lallai Allah Ya umurceku da yin Salati da Sallama ga Annabin mu...

# RAHAMA[1]

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrin kawunan mu da munanan ayyukkan mu, wanda Allah ya shiryar dashi babu mai ɓatar dashi, kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa: lallai Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi Yabo da Aminci mai yawa a gare shi da iyalansa da Sahabbansa.

**Amma Ba'adu[2]:**

Kuji tsoron Allah -yaku bayin Allah- haƙikanin tsoro; domin Allah baya karɓar abunda ba Taƙawa ba, kuma baya yin Rahama sai ga Ma'abotanta.

**Ayyuhal Muslimŭn[3]:**

Addini ya tsayu ne akan sauke Haƙƙoƙin Allah da Haƙƙoƙin bayinSa; Haƙƙin Allah shine: Mu bauta maSa Shi kaɗai kuma kada mu haɗa Shi da komai, kuma haƙƙin Hallittu shine: Kyautatawa zuwa garesu da

---

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a Ashirin da Tara ga watan Jumãdã Ulã, Shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da talatin da shida bayan Hijira.

(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

(3) Yaku Musulmi.

kyawawan Halaye tare dasu.

Kuma akwai wata Ɗabi'a mai girma wadda Allah Ya saka tsakanin HallittarSa; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi– ya ce gameda ita «**Allah Ya hallicci Rahama ɗari, sai ya sanya ɗaya tsakanin Hallittarsa, kuma Ya ɓoye guda Ɗari ba Ɗaya a wurinsa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Allah Ya gabatar da ita akan Ni'imar Ilimi:

﴿فَوَجَدَا عَبۡدٗا مِّنۡ عِبَادِنَآ ءَاتَيۡنَٰهُ رَحۡمَةٗ مِّنۡ عِندِنَا وَعَلَّمۡنَٰهُ مِن لَّدُنَّا عِلۡمٗا﴾

((**Sai suka samu wani Bawa daga cikin BayinMu wanda Mun bashi wata Rahama daga wuriMu kuma Muka sanar dashi wani Ilimi daga gareMu**)). [Suratul Kahaf: 65].

Kuma Shi Allah Mai tsarki Yana son wanda ya siffantu da ita, kuma Ya yabi bayinSa masu yin Wasici da ita:

﴿ثُمَّ كَانَ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلصَّبۡرِ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلۡمَرۡحَمَةِ﴾

((**Sa'annan kuma ya kasance daga waɗanda sukayi Imani kuma sukayi wasici da Haƙuri kuma sukayi Wasici da Tausayi**)) [Suratul Balad: 17].

Da Rahama ce tushen gina sauke Haƙƙoƙin Bayi na Wajibi yake tsayuwa kamar kamar: Zakkah ko wanda aka kwaɗaitar wanda ba wajibi ba kamar: Afuwa da Sadaka, Shaikhul Islam –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Wajibi ne ga Mutum ya kasance manufarsa ita ce amfanar da Halitta da kuma kyautatawa zuwa gare su a sake, kuma wannan itace Rahamar da aka aiko

Muhammad –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi– da ita».

Kuma ita kyauta ce daga Allah, Yana bawa wanda yaso daga cikin BayinSa; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi– ya ce ga wani balaraben ƙauye da yayi jafa'i kan tausasawa ƴaƴansa: «**Yaya zanyi da kai idan Allah ya cire Rahama daga cikin Zuciyarka**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma duk lokacin da Allah Yayi nufin Alkhairi ga bawansa sai ya saukar da Rahama a cikin Zuciyarsa:

﴿ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ ٱلسَّكِينَةَ ﴾

((**Shine wanda ya saukar da Natsuwa**)) [Suratul Fat'h: 4].

Ibn Abbas –Allah Ya yarda dasu- yace: «Abin nufi: Rahama»,

﴿ فِى قُلُوبِ ٱلْمُؤْمِنِينَ لِيَزْدَادُوٓا۟ إِيمَٰنًا مَّعَ إِيمَٰنِهِمْ ﴾

((**a cikin Zuciyar Muminai domin su ƙara Imani tare da Imaninsu**)). [Suratul Fat'hi: 4].

Kuma rabon kowane Bawa a ciki yana kasancewa ne gwargwadon rabonsa daga Shiriya; don haka mafi kamalar Imani daga cikin Muminai shine wanda yafisu girman Rahama; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿ مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِ ۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلْكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيْنَهُمْ ﴾

((**Muhammad Manzon Allah ne, kuma waɗanda suke tare dashi masu tsanani ne akan Kafirai masu**

**Rahama ne a tsakaninsu**)) [Suratul Fat'hi: 29]. kuma Allah ya Siffanta Muminai da faɗinSa:

﴿ أَذِلَّةٍ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴾

((**Masu ƙanƙan da kai ne ga Muminai**)). [Suratul Mã'idah: 54].

Ibnu Abbas –Allah Ya yarda dasu- yace: «yana nufi da ƙanƙar da kai: Rahama», kuma cikar Zuciya da ita alama ce ta samun jin daɗi, kuma sanadi ce na samun Rahamar Allah; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi– ya ce: «**Masu Rahama Allah yana yi masu Rahama, Kuyi Rahama ga waɗanda suke a cikin Ƙasa sai wanDa yake a Sama Yayi maku Rahama**» [Abu Dawud ya ruwaito shi].

Kuma daga cikin waɗanda zasu shiga Aljannah akwai: wasu Mutane da aka cika Zukatansu da Rahama da kuma taushi tareda Imani; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi– ya ce: «**Yan Aljannah iri uku ne: Mai Mulki mai Adalci mai Sadaka wanda aka datar dashi, da kuma wani Mutum mai Rahama mai taushin Zuciya ga duk wani Makusanci da Musulmi, da kuma Mai kamewa mai ƙoƙarin kamewa mai Iyali**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma ƙeƙashewar Zuciya yana samuwa ne da rashin samun Rahama a cikinta, Allah Ya zargi wasu Mutane sai Yace:

﴿ ثُمَّ قَسَتْ قُلُوبُكُم مِّنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ ﴾

((**Sa'annan sai Zukatanku suka ƙeƙashe bayan wancan**)), [Suratul Baƙara: 74].

Al-Bagawiy –Allah Ya jiƙansa- yace: «Ma'ana: Suka bushe suka ƙeƙashe, kuma ƙeƙashewar Zuciya shine fitar Rahama da Tausayi daga cikinta» kuma wannan Alamar Taɓewa ce: Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi– ya ce: «**Ba'a cire Rahama sai daga wanda ya taɓe**» [Abu dawud ya ruwaito shi].

Kuma duk wanda baya yin Rahama, Allah baYa masa Rahama; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi– ya ce: «**Allah baYa yin Rahama ga wanda baya yin Rahama**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi]. Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi– yayi inkari ga wanda ya ƙyamaci yin abu ɗan kaɗan daga cikin tasirin Rahama; Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi– ya sumbanci Hassan ɗan Aliyu –Allah Ya yarda dasu- a lokacin Al-Aƙra'u bin Hãbis Al-Tamimiy –Allah Ya yarda dashi- yana zaune a wurinsa, sai Al-Aƙra'u yace: «Inada ƴaƴa Goma, ban taɓa Sumbantar ɗaya daga cikinsu ba, sai Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi– yace: **Wanda baya yin Rahama, ba'a masa Rahama**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], Ibn Baɗɗãl Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Tausayin ɗa ƙarami, da rungume shi, da Sumbantarsa, da lallaɓawa dashi; yana daga cikin Ayukkan da Allah Yake yarda dasu kuma yake sakawa akansu, kuma Sumbantar yaro ƙarami da ɗaukan sa da rumgume shi yana daga cikin abunda ya cancanci Rahamar Allah saboda shi».

Kuma mafi cancantar Mutane ga jin ƙai sune: Mahaifa guda biyu; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَٱخۡفِضۡ لَهُمَا جَنَاحَ ٱلذُّلِّ مِنَ ٱلرَّحۡمَةِ﴾

((**Kuma ka saukar a garesu fikafikin tausasawa na Rahama**)) [Suratul Isrã'i: 24].

Kuma mafi Alkhairin ƴaƴa shine wanda yafi kusa ga tausayawa Mahaifansa biyu:

﴿فَأَرَدۡنَآ أَن يُبۡدِلَهُمَا رَبُّهُمَا خَيۡرٗا مِّنۡهُ زَكَوٰةٗ وَأَقۡرَبَ رُحۡمٗا﴾

((**Sai mukayi nufin Ubangijinsu ya musanya musu mafi Alkhairi daga gare shi a tsarkakuwa kuma wanda yafi kusanci ga tausayawa**)) [Suratul Kahafi: 81].

Kuma Rahamar dake tsakanin Muminai tana mayar dasu kamar Jiki ɗaya; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Zakaga Muminai a cikin Rahamarsu da Ƙaunar junansu da Tausayinsu kamar misalin Jiki ɗaya ne, idan wata gaɓa tana ciwo sai hakan ya kai ga sauran Jikin da rashin bacci da kuma rashin Lafiya**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Shari'ah ta kwaɗaitar akan tausayawa ga Dabbobi; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Kuma Akuya idan ka tausaya mata; Allah sai yayi maka Rahama**» [Ahmad ya ruwaito shi].

Kuma Mumini yana tausayin Kafiri; saboda abunda ya same shi na rasa Shiriya, kuma yana ƙinsa; saboda rashin Imaninsa, kuma duk wanda ƙafarsa ta zame a cikin Saɓo lallai ya cancanci a tausaya masa ta hanyar yi masa Nasiha, da roƙa masa Shiriya; Anzowa Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- da wani

Mutum wanda yasha Giya, sai yace: «**Ku buge shi**, Abu Huraira yace: daga cikin mu akwai mai duka da Hannunsa, akwai mai duka da Takalminsa, akwai kuma mai duka da Tufafinsa, bayan ya tafi sai wani sashe daga cikin Mutane yace: Allah Ya kunyatar da kai, sai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: **Kada kuce haka, kada ku taimaki Shaiɗan akan ɗan uwanku, sai kuce: Allah Yayi maka Rahama**» [Ahmad ya ruwaito shi].

Kuma mafi girman tausayi daga cikin Hallittu sune: Manzannin Allah; sunyi ƙoƙari don Shiriyar Hallitta, kuma sun kira Mutanensu ta kowace Hanya domin tseratar dasu daga Halaka, kuma sukayi Haƙuri akan cutarwarsu, basuyi gaugawar neman zuwan Azabarsu ba; Adam –Aminci ya tabbata a gare shi- idan yaga ƴan Wuta daga cikin Zuri'arsa sai yayi Kuka; a cikin Ƙissar Mi'irãji [Tafiya sama da akayi da Annbi] Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Nace da Jibril: Waye wannan? Yace: Wannan Adam ne, kuma wannan duhun Mutane dakake gani a Damansa da Hagunsa Ruhin ƴaƴansa ne, waɗanda suke dama daga cikinsu sune ƴan aljanna, duhun mutane dake hagunsa ƴan wuta ne, idan ya kalli Damansa sai yayi Dariya, idan kuma ya kalli Hagunsa sai yayi Kuka**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Ibrahmin –Aminci ya tabbata a gare shi- ya kasance mai tausayin Mutanensa; yacewa Ubangjinsa:

﴿فَمَن تَبِعَنِي فَإِنَّهُۥ مِنِّيۖ وَمَنۡ عَصَانِي فَإِنَّكَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ﴾

((**Wanda ya bini lallai yana daga gareni, wanda kuma ya saɓa min lallai Kai Mai gafara ne kuma mai Jin ƙai**)) [Suratu Ibrahim: 36].

Kuma saboda taushin Zuciyarsa ne yayi Jayayya da Mala'iku don kada su halaka Mutanen Luɗ koda zasuyi Imani.

Kuma Musa –Aminci ya tabbata a gare shi- yaji tausayin Yan mata biyu, sai ya shayar dasu ruwa –Kuma yana daga cikin Manyan Annabawa ma'abota Azama-, kuma Tausayinsa –Aminci ya tabbata a gare shi- ya kai har zuwa ga wannan Al'ummar; ya kwaɗaitar da Annabin mu Muhammad –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- da ya ƙara nema daga UbangijinSa kan sha'anin rage yawan Sallah ga Al'ummarsa, sai Ubangiji Mai girma da ɗaukaka ya rageta daga Salloli Hamsin zuwa Salloli Biyar, kuma Allah yasa Yahya –Aminci ya tabbata a gare shi- mai tausayi; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَحَنَانًا مِّن لَّدُنَّا وَزَكَوٰةً ۖ وَكَانَ تَقِيًّا﴾

((**Kuma muka saka shi mai tausayi daga wurinmu kuma mai tsarki kuma ya kasance mai Taƙawa**)). [Suratu Maryam: 13]. Ibn Katheer –Allah Ya jiƙansa- yace: «Ma'anar Ayar shine: Kuma Muka bashi Rahama daga wurinMu da kuma tausayi ga Bayi; saboda ya kirasu zuwa ga biyayyar Ubangijinsu, kuma yayi aiki na ƙwarai a cikin Ikhalsi».

Kuma Allah ya sanya Isah –Aminci ya tabbata a gare shi- mai biyayya ga Mahaifiyarsa kuma bai kasance Mai kaushin Zuciya marar tausayi ba:

﴿وَبَرًّا بِوَالِدَتِي وَلَمْ يَجْعَلْنِي جَبَّارًا شَقِيًّا﴾

**((Kuma Mai biyayya ga Mahaifiyata kuma bai sanya ni mai kaushin Zuciya taɓaɓɓe ba)).** [Maryam: 32].

Kuma wani Annabi daga cikin Annabawa Mutanensa sun buge shi har suka zubar masa da jini, sai yana shafe Jinin daga Fuskarsa yana cewa: «**Ya Allah Ka gafartawa Mutanena; domin su basu sani ba**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Annabin mu Muhammad –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- shine; mafi tausayin hallittun Allah, kuma daga cikin sunayensa akwai «**Annabin Rahama**» [Al-nasa’i ya ruwaito shi], kuma lokacin da ake faɗa masa: «Kayiwa Mush’rikai baƙar Addu’a sai yace: **Ni ba an aiko ne ba mai yawan tsinuwa, ni kawai an aiko ni don Rahama**» [Muslim ya ruwaito shi], kuma lokacinda Mutanensa suka cutar dashi sai Mala’ikin Duwatsu ya kirashi yayi masa Sallama kuma yace: «Ya Muhammad! Idan kaso sai na rikito akansu duwatsunan nan guda biyu [dutsin abu ƙubais, da kuma ƙu'aiƙi'an] dake tsakanin Makkah? Sai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yace: **A’a, Ina fatan Allah Ya fitar daga tsatson su waɗanda zasu bautawa Allah Shi kaɗai, basa haɗa Shi da komai**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Allah Ya aiko shi domin Rahama ga Hallittu baki ɗaya; Allah Ya ce:

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا رَحۡمَةٗ لِّلۡعَٰلَمِينَ﴾

((**Kuma bamu aiko ka ba face sai Rahama ga Talikai**)) [Suratul Ambiyã: 107].

Don haka, duk wanda ya karɓi wannan Rahamar, kuma ya godewa wannan Ni'imar; ya tsira a Duniya da Lahira. Kuma duk wanda ya mayar da ita kuma yayi inkarinta; yayi Hasarar gidaje biyu [Duniya da Lahira], Allah Ya aiko shi Rahama ga Muminai ta Musamman; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَرَحۡمَةٞ لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنكُمۡۚ﴾

**((Kuma –**shi**- Rahama ne ga waɗanda sukayi Imani daga cikin ku)).**

Kuma ya kasance mai tausayi ne ga Al'ummarsa; «Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya karanta faɗin Allah Mai Buwaya da ɗaukaka gameda Ibrahim:

﴿رَبِّ إِنَّهُنَّ أَضۡلَلۡنَ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلنَّاسِۖ فَمَن تَبِعَنِي فَإِنَّهُۥ مِنِّيۖ وَمَنۡ عَصَانِي فَإِنَّكَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ﴾

**((Ya Ubangiji lallai su sun ɓatar da dayawa daga cikin Mutane, duk wanda ya bini lallai shi yana daga gareni, kuma duk wanda ya saɓa min lallai Kai mai Gafara ne kuma Mai Jin ƙai)) [Suratu Ibrahim: 36].**

**Kuma Isah –Aminci ya tabbata a gare shi- ya ce:**

﴿إِن تُعَذِّبۡهُمۡ فَإِنَّهُمۡ عِبَادُكَۖ وَإِن تَغۡفِرۡ لَهُمۡ فَإِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ﴾

**((Idan kayi masu Azaba lallai su BayinKa ne**

**kuma idan Ka gafarta masu lallai Kai Kaine Mabuwayi Mai Hikima))** [Mã'idah: 118].

Sai Annabi ya ɗaga Hannayensa kuma yace: **Ya Allah Al'ummata Al'ummata,** kuma ya fashe da Kuka, **sai Allah Mai Buwaya da Ɗaukaka yace: Ya Jibril! Ka tafi wurin Muhammad –kuma UbangijinKa Shi ne Yafi sani- ka tambaye shi, meye yake sakaka Kuka? Sai Jibril –Aminci ya tabbata a gare shi- yaje wurinsa kuma ya tambaye shi, sai Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya bashi labarin abunda yace, -Kuma shine mafi sani- sai Allah Yace: Ya Jibril! Kaje wurin Muhammad, kace: Lallai Mu zaMu yardar da kai a cikin Al'ummarka, kuma bazaMu baƙanta maka ba**» [Muslim ya ruwaito shi], Al-An-Nawawi –Allah Ya jiƙansa- yace: «Wannan yana daga cikin Hadisi mafi girman fata ga wannan Al'ummar koma shine mafi girman fata».

Kuma ya kasance mai tausayi ga Sahabbansa; «Sa'ad ɗan Ubãdah ya kawo masa kukan wani ciwo da yake damunsa, sai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kai masa Ziyara tare da wani sashe na Sahabbansa –Allah Ya yarda dasu- bayan da ya shiga wurinsa sai ya same shi Iyalin shi suna zagaye dashi yana cikin ciwo, sai yace: **ya Rasu ne**? suka ce: A'a ya Manzon Allah! sai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya fashe da Kuka; da Mutane suka ga Kukan Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- sai suma suka fashe da Kuka» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma «an miƙa wani yaro zuwa ga Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare

shi- alhali Ransa yana sautin fita da kai-komo sai Idanuwansa suka zubo da Hawaye, sai Sa'ad yace: Ya Manzon Allah! Meye wannan? Sai yace: **Wannan Rahama ce, Allah ne ya sanyata a cikin Zukatan BayinSa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kasance mai tausayi ga Samari; Mãlik ɗan Huwairith –Allah ya yarda dashi- ya ce: «Munzowa Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- alhali lokacin muna cikin Samartaka sa'annin juna, sai muka zauna a wurinsa kwana Ashirin, sai ya fahimci cewa lallai munyi kwaɗayin komawa ga Iyalanmu, kuma ya tambayemu labarin waɗanda muka baro a cikin Iyalanmu, sai muka bashi labari, kuma ya kasance mai lallaɓawa da kuma tausayi, sai yace: **Ku koma zuwa ga Iyalanku; ku koyar dasu kuma ku umurce su, kuma kuyi Sallah kamar yadda kukaga ina Sallah, kuma idan lokacin Sallah yayi; ɗaya daga cikinku ya yi maku kiran Sallah, sa'annan Babba daga cikinku yayi maku Limanci**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma ya kasance mai tausayi ga Mata, yana taƙaita Sallah don kada ya wahalar da Uwa da Ɗanta; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Ni ina shiga Sallah alhali inada nufin tsawaitata, sai naji Kukan yaro; sai na taƙaita a cikin Sallata; saboda abunda nasani na tsananin abunda Uwa take ji daga kukansa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma ya kasance Mai tausayi ne ga Yara; Anas –Allah Ya yarda dashi- ya ce: «Ban taɓa ganin wani

wanda yakai tausayin Iyali kamar Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ba» [Muslim ya ruwaito shi]. kuma «Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kasance yana Huɗuba, sai Hassan da Husaini suka zo suna tafiya suna faɗuwa; sai Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya sauko daga kan Mimbari, sai ya ɗauke su ya ɗorasu a gabansa, sa'annan kuma yace: **Allah da Manzonsa sunyi gaskiya:**

﴿إِنَّمَآ أَمۡوَٰلُكُمۡ وَأَوۡلَٰدُكُمۡ فِتۡنَةٞۚ﴾

((**Lallai Dukiyarku da Ƴayaƙnku Fitina ne**)). [Suratul Tagãbun: 15]

**Na kalli waɗannan yaran su biyu suna tafiya suna faɗuwa, sai na kasa Haƙuri har saida na yanke Maganata kuma na daukesu**» [Ahmad ya ruwaito shi], Ibnul Qayyim –Allah Ya jiƙansa- yace: «Wannan yana daga cikin cikar Rahamarsa da kuma tausasawarsa ga yara, da tausayinsa a garesu, kuma wannan koyarwa ce daga gare shi ga Al'ummarsa na Rahama da Tausayi da kuma Lallaɓawa da yara».

Kuma mafi girman tausayi a cikin wannan Al'ummar sune: Sahabban Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi-; Allah Mai tsarki yana yabonsu sai yace:

﴿أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلۡكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيۡنَهُمۡۖ﴾

((**Masu tsanani ne akan Kafirai masu Rahama ne a tsakaninsu**)) [Suratul Fat'hi: 29],

Kuma wanda yafi su tausayi shine Abubakar Siddiq –Allah Ya yarda dashi-, Allah Ya hađa masa tsakanin yawan Ilimi da Rahama, kuma Ibnul Qayyim –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Kuma haka Mutum yake, duk lokacinda Iliminsa ya ƙara fađi; Tausayinsa zai ƙara fađi», kuma Ma’abota Ilimi da Nagarta Ma’abotan Rahama ne, suna ƙoƙarin yađa Alkhairi da Shiriya ga Mutane, kuma basa Zaluntar wanda ya saɓa masu kuma basa cutar dashi».

**Waba’adu Ayyuhal Muslimŭn**(1)**:**

Rahamar Shari’ah da Adalcinta ya yalwaci Maƙiyi da Aboki, kuma sakamako yana kasancewa ne daga irin jinsin Aiki, duk wanda yake kwađayin Rahamar Allah, to, yayi Rahama ga HallitarSa; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Lallai Allah Yana Rahama ne ga BayinSa masu yawan Tausayi**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma duk wanda Allah Yayiwa Rahama; jin dađi zai lulluɓe shi, kuma zai samu ƙarshe mai kyau a Duniya da Lahira.

**Ina neman tsarin Allah daga Shaiđan Jefaffe**

﴿هَلۡ جَزَآءُ ٱلۡإِحۡسَٰنِ إِلَّا ٱلۡإِحۡسَٰنُ﴾

((**Ashe kyautatawa tanada wani sakamako face Kyuatatatawa**!)) [Suratul Rahmãn: 60].

Allah Yayi min Albarka tare daku a cikin Alƙur’ani mai girma ...

(1) Bayan haka, Yaku Musulmi.

## HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarsa da kuma Ni'imominSa, kuma ina shaida cewa lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya; don girmamawa ga Sha'aninSa, kuma ina shaida cewa lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Yabon Allah ya tabbata a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa tareda Aminci mai ƙaruwa.

**Ayyuhal Muslimŭn(1):**

Zuciya tana tsarkakuwa ne daga Girman kai da wulaƙanta Mutane ta hanyar tabbatar da Tausayi, kuma tausayi abu ne wanda yake tskanin ƙeƙashewar Zuciya da Jafa'i, da kuma tsakanin Rauni da Karaya, kuma Allah Yana son Tausayi da Rahama idan dai basu kasance masu tozartar da Addini ba; kamar kiraye-kirayen barin yin Haddodi; saboda tausayi ga Bayi, kuma idan Bawa ya kuɓuta daga Fitinar Shubuhohi da Sha'awowi; zai samu Shiriya da kuma Rahama, Allah yana bada labarin Mutanen kogo sai Ya ce:

﴿ فَقَالُوا۟ رَبَّنَآ ءَاتِنَا مِن لَّدُنكَ رَحْمَةً وَهَيِّئْ لَنَا مِنْ أَمْرِنَا رَشَدًا ﴾

**((Sai suka ce Ya Ubangijin mu Kabamu wata Rahama daga gareKa kuma Ka sauƙaƙe mana Shiriya daga Al'amarinmu))** [Suratul Kahaf: 10].

(1) Yaku Musulmi.

Kuma daga cikin sabubban samun Rahama akwai: Biyayya ga Mahaifa biyu, da sadar da Zumunta, da Sadaka, da Kyautatawa ga waɗanda suke a cikin baƙin ciki da rashin lafiya, da Ziyarar Maƙabartu ga Maza, da yawaita karatun Alƙur'ani Mai girma da ambaton Allah.

Sa'annan kuma kusani, lallai Allah Ya umurceku da yin Salati da Sallama ga AnnabinSa ..

# KUNYA ALKHAIRI CE DUKKANTA[1]

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunan mu da miyagun Ayukkan mu, wanda Allah Ya shiryar dashi babu mai ɓatar dashi, kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida lallai Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi yabo da Aminci mai yawa a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Amma Ba'adu[2]:**

Kuji tsoron Allah -yaku bayin Allah- haƙiƙanin tsoro, kuma kuyi riƙo da Musulunci da Igiya mai ƙarfi.

**Ayyuhal Muslimŭn[3]:**

Mabuɗin Bauta ga Allah da Sirrinta shine sanin Sunayen Allah da SiffofinSa, SunayenSa Maɗaukaki kyawawa ne kuma SiffofinSa Maɗaukaka ne, kuma a cikin kowane Suna da Siffa ta Allah Mai tsarki yanada

---

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a Bakwai ga watan Jumãdãl Ãkhir, Shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da talatin da tara bayan Hijira.

(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

(3) Yaku Musulmi.

Ibada ta musamman wadda itace abinda saninta yake gadarwa da nunawa, kuma Allah Yana son SunayenSa da SiffofinSa, kuma Yana son bayyanar tasirinsu a cikin Hallittunsa, don haka ne, Ya umurci BayinSa dasu roƙe shi dasu, sai Yace:

﴿وَلِلَّهِ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰ فَٱدۡعُوهُ بِهَاۖ﴾

((**Lallai Allah Yanada Sunaye kyawawa don haka ku roƙe Shi dasu**)) [Suratul A'arãf: 180].

Kuma mafi soyuwar Hallittu a wurin Allah shine wanda ya siffantu da siffofin dayake So wadɗanda ba keɓantattu ne ba daShi Allah mai tsarki, kuma duk wanda ya bautawa Allah da SiffoffinSa; zai samu kusanci ga RahamarSa.

Kuma duk wanda ya kiyaye SunayenSa, zai saukar dashi a cikin AljannarSa, kuma daga cikin SunayenSa akwai: Mai Kunya, kuma daga cikin SiffofinSa akwai: Mai Kunya, kuma haƙiƙa Allah Ya siffanta kanSa da hakan, sai yace:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَسۡتَحۡيِۦٓ أَن يَضۡرِبَ مَثَلٗا مَّا بَعُوضَةٗ فَمَا فَوۡقَهَاۚ﴾

((**Lallai baya jin kunyar ya buga Misali da Sauro da abunda yake sama dashi**)) [Suratul Baƙarah: 26].

Kuma Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kirashi da hakan, yace: «**Lallai Allah –Mai Buwaya da Ɗaukaka- Mai Kunya ne Mai yawan Suturcewa ne, Yana son Kunya da Suturtawa**» [Abu dawud ya ruwaito shi], kuma Allah Mai tsarki Yana jin Kunyar ya mayar da wanda ya roƙe shi wani

abu; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Lallai Ubangijinku Mai yawan Albarka da ɗaukaka Mai Kunya ne Mai Karamci ne, Yana jin Kunyar Bawansa idan ya ɗaga Hannayensa zuwa gare Shi ya mayar dasu ba komai a ciki**» [Abu dawud ya ruwaito shi], Ibnul Qayyim yace: «Kunyar Ubangiji Maɗaukaki ga BawanSa Fahimta bata iya sanin haƙiƙaninta, kuma Hankula basa iya siffantata; domin ita Kunyar Karamci ce da Bayarwa da Kyauta da Girma».

Kuma ƙololuwar kyawawan ɗabi'u a cikin Hallittu kuma mafi ɗaukaka kuma mafi girman Matsayi kuma mafi yawan Amfani itace: Kunya, kuma Kunya wani hali ne da yake sanya barin Munanan ababe, kuma yake hani daga yin sakaci a cikin Haƙƙin mai Haƙƙi, abunda yake zaburar da ita da asalin kalmar a larabce daga Rayuwa ne, kuma gwar-gwadon Rayuwar Zuciya; Kunya take kasancewa a cikinta, kuma gwar-gwadon Rayuwar Zuciya gwar-gwadon yadda kunaya take kasancewa cikinta, kuma duk yadda zuciya ta kasance tafi rayuwa, cikar Kunya da Ƙarfinta yake kasancewa a cikinta, kuma al'amarin Kunya bai gushe yana tabbace ba kuma aiki da ita bai gushe yana dole ba tun Zamanin Annabtancin Farko, kuma ba wani Annabi face sai ya kwaɗaitar da Al'ummarsa zuwa gareta, kuma face sai an aiko shi akanta, kuma ba'a taɓa shafeta ba daga cikin ababen da aka shafe na Shari'o'i, kuma ba'a canzata ba daga cikin ababen da aka canza daga cikinta, domin al'amari ne wanda ansan dacewarsa, kuma Falalarsa ta bayyana, kuma Hankula sun haɗu akan kyawonsa, kuma duk abunda wannan ne Saiffarsa ba'a Shafe shi kuma ba'a

canza shi; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Lallai yana daga cikin abunda Mutane suka riska na Maganar Annabta: Idan bakada kunya sai ka aikata abunda kaso**». [Bukhari ya ruwaito shi].

Zaɓaɓɓun Hallittu sun siffantu ne da Kunya, kuma Allah Ya yabi Ma'abotanata; Mala'iku sun siffanta da ita, Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Ashe bazanji Kunyar Mutumin da Mala'iku suke jin Kunyarsa ba?**» [Muslim ya ruwaito shi], Kuma an san Annabawa da ita a cikin Mutanensu; «**Ranar Ƙiyama Hallittu zasu nemi ceto daga Adam da Nuhu da Musa –Aminci ya tabbata a garesu-; sai kowane ɗaya daga cikinsu ya ambato Zunubinsa kuma yaji Kunya**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Musa –Aminci ya tabbata a gare shi- Mai yawan Kunya ne, Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Lallai Musa ya kasance Mutum Mai yawan jin Kunya Mai yawan suturcewa, ba'a ganin wani abu daga fatarsa; saboda jin Kunyarsa**» [Bukhari ya ruwaito shi].

Kuma Annabin mu Muhammad –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yana da mafi girman rabo a cikin wannan; domin ana sanin Kunyarsa daga Fuskarsa; Abu Sa'eed Alkhudriy –Allah Ya yarda dashi- ya ce: «Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yafi tsananin Kunya sama da Budurwa dake cikin ɗakinta, kuma ya kasance idan baya son wani abu sai mugane hakan a Fuskarsa» [Bukhari da Muslim suka

ruwaito shi], kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yayi ta kai-komo a daren Mi'irãji tsakanin Musa –Aminci ya tabbata a gare shi- da Ubangijinsa, yana tambayarSa sauƙi a cikin Sallah har yace: «**Tabbas, najin Kunyar Ubangijina**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma «lokacin da Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya tare da Matarsa Zainab bintu Jahash; an kira Mutane saboda hakan kuma suka ci abinci suka fita, sai wasu Mutane su uku suka zauna suna Labari a cikin Gidan, sai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yaji Kunyar yace musu wani abu, sai ya fita yabarsu a cikin gidan; sai Allah Mai girma da ɗaukaka Ya saukar da:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَدۡخُلُواْ بُيُوتَ ٱلنَّبِيِّ إِلَّآ أَن يُؤۡذَنَ لَكُمۡ إِلَىٰ طَعَامٍ غَيۡرَ نَٰظِرِينَ إِنَىٰهُ وَلَٰكِنۡ إِذَا دُعِيتُمۡ فَٱدۡخُلُواْ فَإِذَا طَعِمۡتُمۡ فَٱنتَشِرُواْ وَلَا مُسۡتَـٔۡنِسِينَ لِحَدِيثٍۚ إِنَّ ذَٰلِكُمۡ كَانَ يُؤۡذِي ٱلنَّبِيَّ فَيَسۡتَحۡيِۦ مِنكُمۡۖ وَٱللَّهُ لَا يَسۡتَحۡيِۦ مِنَ ٱلۡحَقِّۚ﴾

**((Yaku waɗanda sukayi Imani, kada ku shiga gidajen Annabi sai idan anyi maku Izini zuwa ga wani abinci, ba kun tsaya jiran nunarsa ba, sai dai kuma idan an kiraku, to, ku shiga, kuma idan kunci Abincin, to ku waste, ba tareda kun tsaya kuna masu labari ba, lallai wannan yana cutar da Annabi, sai yana jin kunyar ku, kuma Allah baya jin kunyar gaskiya))»** [Suratul Ahzãb: 53]. [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Uthman –Allah Ya yarda dashi- abun buga Misaline a cikin Kunya tsakanin Sahabbai; wata rana ya shiga wurin Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata

a gare shi- sai Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya zauna kuma ya gyara tufafinsa, sai aka tambaye shi akan haka, sai yace: «**Lallai Uthman Mutum ne Mai yawan Kunya, kuma ni naji tsoron idan na bashi izini a cikin wancan yanayin ya kasa bayyana Buƙatarsa zuwa gare ni**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma an hallicci Mace akan jin Kunya kuma da itace Adonta da kyawunta, kuma Kunya Katanga ce a gareta da kuma Aminci; Aisha –Allah Ya yarda da ita- ta ce: «Ya Manzon Allah! Lallai Budurwa tana jin Kunya? Sai yace: **Yardarta** –cikin maganar Aure- shine; **Shirunta**» [Bukhari ya ruwaito shi].

Kuma Yar jagoran garin Madayana tazo tana tafiya alhali Hijabin Kunya ya lulluɓeta, kuma ta rufe Fuskarta da Hannayenta da Tufafinta; Allah Mai Tsarki Yace:

﴿فَجَآءَتۡهُ إِحۡدَىٰهُمَا تَمۡشِي عَلَى ٱسۡتِحۡيَآءٖ قَالَتۡ إِنَّ أَبِي يَدۡعُوكَ لِيَجۡزِيَكَ أَجۡرَ مَا سَقَيۡتَ لَنَاۚ﴾

**((Sai ɗayarsu tazo tana tafiya cikin Kunya, tace: Lallai Babana yana kiranka domin ya sakamaka da ladar shayarwa dakayi mana))** [Suratul Ƙasas: 25].

Kuma Kunya ta kai ga Aisha Uwar Muminai –Allah Ya yarda da ita- har tana jin Kunya a cikin ɗakinta; tana jin Kunyar Umar –Allah Ya yarda dashi- bayan an rufe shi, tace –Allah Ya yarda da ita-: «Na kasance ina shiga ɗakina wanda aka rufe Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- da Mahaifina a ciki, sai na cire kayana, sai nace: Ai Mijina da Mahaifina ne kawai,

amma da aka rufe Umar tare dasu; na rantse da Allah! ban taɓa shiga ba face sai na saka kayana; saboda Kunyar Umar» [Ahmad ya ruwaito shi].

Kuma akwai wata mata wacce ta tayi Haƙuri akan Bala'i kuma bata yarda da cire Kunya ba, sai tasamu Aljannah; Ibn Abbas –Allah Ya yarda dasu- yacewa Adã bin Abi Rabãh –Allah Ya jiƙansa- «ko zan nuna maka wata Mace daga cikin Ƴan Aljannah? Sai nace: Eh, sai yace: Wannan Matar Baƙa, tazo wurin Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- sai tace: Ni ina faɗuwa [Farfaɗiya], kuma jikina yana buɗewa, ka roƙa min Allah, sai yace: **Idan kina so kiyi Haƙuri kinada Aljannah, idan kuma kika so sai na roƙi Allah ya baki lafiya,** sai tace: A'a, zanyi Haƙuri, sai tace: Amma jikina yana buɗewa, ka roƙa min Allah kada jikina ya buɗe; sai ya roƙa mata» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Kunya tana daga cikin Halayen Karamci wadda Mutanen Jahiliya suka tabbatta akanta; a lokacin da Hiraƙal ya tambayi Abu Sufyãn –Allah Ya yarda dashi- akan Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi-, alhali lokacin Abu Sufyãn yana akan Kafirci, yace: «Wallahi ba don Kunya ba a wannan ranar, kada Abokanaina su cirato Ƙarya daga gareni da nayi masa Ƙarya a lokacin da ya tambayeni gameda shi, sai dai naji Kunyar su cirato Ƙarya daga gareni sai na faɗa masa gaskiya» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma da Kunya ce ake samun jin daɗi da kuma kaiwa ga Sabubbanta, kuma Alkhairi ce dukkanta; Annabi –

Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Kunya Alkhairi ce dukkanta** –ko yace-: **Kunya dukanta Alkhair ce**» [Muslim ya ruwaito shi]. Kuma Ƙarshen ma'abocinta yana kaiwa ne zuwa ga Alkhairi, kuma Nadama bata biyo bayansahi har abada; Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Kunya bata zuwa sai da Alkhairi**» [Muslim ya ruwaito shi], Ibnul Qayyim Allah Ya jiƙansa- yace: «Kunya itace: sinadarin rayuwa ga zuciya, kuma itace ginshiƙin kowane Alkhairi, kuma tafiyarta tafiyar Alkhairi ne baki ɗayansa».

Kuma yana daga cikin mafi girman Alkhairi a cikinta: Sabo akan ɗabi'u abun godewa, da kuma nisantar halaye abun zargi, kuma idan Kunyar Mutum ta girmama; sai ta Kiyaye Mutuncinsa, ta ture Munanan aikinsa, kuma ta yaɗa kyawawan halayensa.

Kuma yana daga cikin Aƙidar Ahlusunnah Wal Jama'a: lallai Imani Magana ce da Ƙudurcewa da Aiki, kuma Kunya wani yanki ce nashi; Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Imani yanki Saba'in** ko **Sittin da ɗoriya ne, kuma Kunya yanki ce na Imani**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Ibn Hibbãn –Allah Ya jiƙansa- yace: «Kunya tana daga cikin Imani, kuma Mumini ɗan Aljannah ne, kuma ba'a cire kunya daga wani ba sai tareda cire Imaninsa», kuma «Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya wuce wani Mutum alhali yana yiwa ɗan uwansa faɗa akan Kunya, yana cewa: Kai kana jin Kunya har kamar yana cewa: Ta cutar dashi, sai Manzon

Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yace: **Ka ƙyale shi; domin Kunya tana daga cikin Imani**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Allah bai taɓa Azabtar da wata Zuciya ba da abunda yafi tsanani kan ya cire Kunya daga cikinta, Ibn Umar –Allah Ya yarda dasu- ya ce: «Lallai Kunya da Imani an haɗesu tare, idan aka ɗauke ɗayansu, za'a ɗauke ɗayan».

Kunya ɗa'a ce wacce take zaburarwa zuwa ga wasu Ayukkan ɗa'a, kuma tana tuƙewa ne da ma'abocinta zuwa ga tsantseni, kuma duk wanda yayi sakaci da ita zai aikata saɓanin hakan, kuma daga cikin mafi girman abunda yake katangance Mutum daga aikata Saɓo akwai: Kunya, kuma mai Kunya yana yankewa daga Saɓo; saboda Kunya, kamar yadda ake yankewa daga saɓon saboda Imani, don haka, idan aka zare Kunya daga Bawa; ba wani abu dayayi masa saura da zai hana shi aikata Munanan abubuwa da Halayen ƙasƙanci; Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Idan baka jin Kunya; sai ka aikata abunda kaso**» [Bukhari ya ruwaito shi]. Ibnu Abdul Barri –Allah Ya jiƙansa- yace: «Duk wanda bashida Kunya wacce zata katangance shi daga ababen da Allah Ya haramta; a gunsa zai kasance babu banbanci tsakanin yin Ƙananan Zunubai da Manya, kuma a cikin wannan akwai ma'anar tsoratarwa da kuma gargaɗi akan ƙarancin Kunya».

Kuma Zunubai suna raunana Kunya ga Bawa har takan iya fita daga gare shi baki ɗaya, ya kasance baya damuwa da sanin Mutane ga Halinsa, ko ganinsu [ga

abunda yake yi]; har yakan iya bada labarin Halinsa da Munanan Ayukkansa.

Lallai a cikin Kunya akwai ƙawa da kyawo ga Ma'abocinta; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Ba abunda Alfãsha zata kasance a cikinsa face sai ta aibanta shi, kuma ba abunda Kunya zata kasance a cikinsa face sai ta Ƙawata shi**» [at-irmizi ya ruwaito shi], Kuma Kunya sababi ce ga samun ɗaukakar rai da kiyayeta, mai Kunya baya roƙon Mutane wani abu koda ya buƙaci hakan; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Miskini bashi ne wanda za'a bashi Loma ɗaya ko biyu ba ta ishe shi; sai dai haƙiƙanin Miskini shine wanda bashida wadata kuma yana jin Kunya, ko baya iya nacewa gun roƙon Mutane**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Kunya tana jan ma'abocinta zuwa ga Ladabi kyakykyawa; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yayi tambaya akan wata Bishiya wacce take kama da Musulmi, Ibnu Umar –Allah Ya yarda dasu- yace: «Sai yazo a raina cewa icen Dabino ne, amma sai naga Abubakar da Umar basuyi Magana ba, sai na ƙyamaci nayi Magana» a wani lafazin: «Sai naji Kunya» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Sakamako yana kasancewa ne daga irin aiki, kuma daga cikin abunda Kunya take gadarwa da kuma kyakykyawan Sakamakonta akwai: Kunyar Allah ga Ma'abotanta; Annabi –Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- ya ce: «**Amma ɗayansu sai yaji Kunya; sai Allah Mai buwaya da ɗaukaka Yaji Kunyarsa**» [Bukhari da

Muslim suka ruwaito shi].

Kuma ƙololuwar Kunya itace: Kunyar Allah; saboda kada Ya ganka a inda Ya haneka, kuma kada Ya nemeka a inda Ya umurceka, lallai Allah Shine yafi cancantar aji KunyarSa, Annabi –Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- ya ce: «**Kuji Kunyar Allah haƙiƙanin Kunya**» [at-tirmizi ya ruwaito shi].

Kuma Kunyar Allah: Haske ne da yake ɗarsuwa a cikin Zuciya, wannan Hasken zai nunawa Ma'abocinsa cewa lallai yana tsaye a gaban Ubangijinsa Mai buwaya da Ɗaukaka; sai yaji KunyarSa a lokacin da yake shi kaɗai da kuma bayyane, kuma Kunyar Allah tana tabbata da sanin BaiwoyinSa, da girman Ni'imominSa, tareda halarto da Aibin Mutum da kuma gazawarsa, da kuma sanin cewa Shi Allah masani ne ga abunda yake a sirrance da wanda yafi shi ɓoyuwa.

Kuma idan Bawa yasan da ganin Allah Mai tsarki a gare shi, kuma yasan cewa lallai yana a bisa Ganin Allah da JinSa kuma Bawan ya kasance mai Kunya ne; lallai zai ji Kunyar ya bijiro ga abunda yake fusata Shi, kuma tareda Mutum akwai wasu Mala'iku da basa rabuwa dashi, kuma Jin Kunyarsu yana daga cikin girmama su, Allah Mai tsarki ya ce:

﴿وَإِنَّ عَلَيۡكُمۡ لَحَٰفِظِينَ ❁ كِرَامٗا كَٰتِبِينَ ❁ يَعۡلَمُونَ مَا تَفۡعَلُونَ﴾

((**Kuma lallai akanku akwai Matsara ❁ Masu daraja Marubuta ❁ Suna sanin abunda kuke aikatawa**)) [Suratul Infiɗãr: 10-12].

Ibnul Qayyim –Allah Ya jiƙansa- yace: «Ma’ana: Kuji Kunyar waɗannan Matsaran masu girma, kuma ku karrama su kuma ku girmamasu kada su ganku akan abunda zaku ji kunyar irinku yaganku akai».

Kuma Kunyar Mutane yana zaburarwa zuwa ga ayukkan Mutunci, da ace Musulmi bai samu komai ba daga abokin zama na ƙwarai sai dai kawai Kunyarsa tana hana shi faɗawa saɓo da hakan ya ishe shi, kuma ya zama taimako na Alkhairi ga abokinsa wurin Jin Kunyar Allah, kuma wanda baya jin Kunyar Mutane; baya jin Kunyar Allah, kuma wanda ya zauna da masu Kunya; Kunyarsa zata ƙara jaddaduwa, kuma mafi cancantar wanda Mutum zai girmama shine Kansa, kuma duk wanda yayi wani aiki a ɓoye wanda yake jin kunyar yinsa a bayyane; lallai kansa bashida wani matsayi a wurinsa, kuma duk wanda yake jin Kunyar Mutane amma baya jin Kunyar Kansa: lallai Kansa yafi wulaƙanci a wurinsa akan waninsa, kuma wanda yaji Kunyarsu [Kansa da waninsa] amma kuma baya jin Kunyar Allah: lallai bai san Ubangijinsa ba, kuma duk wanda Kunya tayi masa Tufafi; Mutane bazasu ga Aibinsa ba.

**Waba’adu Ayyuhal Muslimŭn(1):**

Musulunci Addinin ababen godiya ne da Halaye na ƙwarai, ya haɗa mafi kyawon Halaye, da mafi ɗaukakar Siffofi, ba wani Alkhairi face sai yayi umurni dashi, kuma ba wani Sharri face ya tsoratar daga gare shi, kuma

(1) Bayan haka, Yaku Musulmi.

wajibi ne riƙo dashi da Alfahari dashi, da kiran Mutane zuwa gare shi, Kuma lizimtar jin Kunyar Allah dole ne akanmu ta hanyar bin umurninSa da nisantar SaɓonSa.

## Ina neman tsarin Allah daga Shaiɗan Jefaffe

﴿وَمَنۡ أَحۡسَنُ دِينٗا مِّمَّنۡ أَسۡلَمَ وَجۡهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحۡسِنٞ وَٱتَّبَعَ مِلَّةَ إِبۡرَٰهِيمَ حَنِيفٗاۗ وَٱتَّخَذَ ٱللَّهُ إِبۡرَٰهِيمَ خَلِيلٗا﴾

((**Waye yafi kyawun Addini sama ga wanda ya miƙa Fuskarsa don Allah kuma yana mai kyautatawa kuma yabi hanyar Ibrahim Miƙaƙƙiya kuma lallai Allah Ya riƙi Ibrahim Badaɗayi**)). [Suratul Nisã'i: 125].

Allah Yayi min Albarka tare daku a cikin Alƙur'ani Mai girma ...

## HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarSa da kuma Ni’imominSa, kuma ina shaida cewa lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya; don girmamawa ga Sha’aninSa, kuma ina shaida cewa lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Yabon Allah ya tabbata a gare shi da iyalansa da Sahabbansa tareda Aminci mai ƙaruwa.

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Kunyar da Annabi –Tsira da Amincin su tabbata a gare shi- yayiwa yabo itace: Halin da yake sanya yin ayukka masu kyau da barin Munana, amma kuma Rauni da Kasawa wanda yake gadar da tawaya a cikin wani abu na haƙƙoƙin Allah ko haƙƙoƙan bayinSa; wannan baya daga cikin Kunya ko kaɗan, kuma idan Kunya ta hana Ma’abocinta daga Alkhairi; wannan ba Kunya ce ba abun yabo, Aisha –Allah Ya yarda da ita- ta ce: «Madalla da irin Matan Ansãru; Kunya bata hanasu suyi tambaya akan Addininsu, kuma su nemi fahimta a cikinsa» [Musulim ya ruwaito shi], kuma babu Kunya a cikin koyon Addini, kuma duk wanda yabar Ilimi saboda Kunya; zai dawwama har Abada a cikin Jahilcinsa kuma

(1) Yaku Musulmi.

abun haramtawa Alkhairai, Mujãhid –Allah Ya jiƙansa-ya ce: «Mai jin Kunya da mai Girma kai basa koyon Ilimi».

Sa'anna kuma kusani lallai Allah Ya umurceku da yin Salati da Sallama ga AnnabinSa .

# HALAYE ABUN SUKA

# GIRMAN KAI[1]

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa, kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunan mu da miyagun Ayukkan mu, wanda Allah Ya shiryar dashi babu mai ɓatar dashi, kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida lallai Annabin mu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi Yabo da Aminci mai yawa a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Amma Ba'adu[2]:**

Kuji tsoron Allah -yaku bayin Allah- haƙiƙanin tsoro, Taƙawa tana cikin saɓawa son Rai, kuma Taɓewa tana a cikin saɓawa Shiriya.

**Ayyuhal Muslimŭn[3]:**

Nagartar ɗan Adam tana cikin Imani da Aiki na ƙwarai, da kuma ƙoƙari a cikin gyaran Zuciya; shine mafi falala kan Ibadu waɗanda ba na dole ba [Nafila],

---

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a Ɗaya ga watan Rajab, Shekara ta Dubu Ɗaya da Ɗari Huɗu da Ashirin da Huɗu bayan Hijira.

(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

(3) Yaku Musulmi.

kuma matsayin Ayukkan Zuciya a cikin Lãda da Uƙuba kamar Ayukkan Gaɓai suke; ana bada Lada akan Soyayya da Ƙiyayya don Allah, da kuma Dogaro ga Allah da Yarda da Niyya akan yin aikin ɗa'a, kuma ana yin Uƙuba akan Girman kai da Hassada da Jiji da kai da Riya, kuma duk lokacinda Bawa ya ƙara Tawalu'u [ƙan-ƙanda kai] da Bauta ga Allah; zai ƙara samun kusanci ga Allah da ɗaukaka.

Kuma Asalin ɗabi'u abun zargi baki ɗayansu shine: Girman kai da ɗagãwa; dashi ne Iblis ya siffantu sai yayi Hassadar Adam kuma yayi Girman kai yaƙi miƙa wuya ga umurnin Ubangijinsa:

﴿وَإِذْ قُلْنَا لِلْمَلَٰٓئِكَةِ ٱسْجُدُوا۟ لِءَادَمَ فَسَجَدُوٓا۟ إِلَّآ إِبْلِيسَ أَبَىٰ وَٱسْتَكْبَرَ وَكَانَ مِنَ ٱلْكَٰفِرِينَ﴾

((**Kuma a lokacinda Muka ce ga Mala'iku kuyi Sujada ga Adam sai sukayi Sujada face Iblis yaƙi kuma yayi Girman kai kuma ya kasance daga cikin Kãfirai**)) [Suratul Baƙara: 34].

Kuma sanadiyarsa ne Yahudawan da suka ga Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- suka ƙi Imani dashi tareda cewa sun san gaskiyar Annabcinsa, kuma Shine ya hana Ibnu Abi Salul miƙa wuya na gaskiya, kuma dashi ne Abu Jahal yaƙi Imani, kuma dashi ne Ƙuraishawa suka zaɓi Makanta daga Shiriya; Allah Mai Tsarki Ya ce:

﴿إِنَّهُمْ كَانُوٓا۟ إِذَا قِيلَ لَهُمْ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ يَسْتَكْبِرُونَ﴾

((**Lallai su sun kasance idan akace masu: Ba abun Bauta da gaskiya sai Allah sai su ɗora Girman kai**)) [Suratus Sãffãt: 35].

Kuma Sulaiman –Aminci ya tabbata a gare shi- ya kira Bilƙisu da Mutanenta zuwa ga barin ɗagãwa da kuma Miƙa wuya:

﴿أَلَّا تَعْلُوا۟ عَلَيَّ وَأْتُونِى مُسْلِمِينَ﴾

((**Kada kuyi Girman kai a gare ni kuma kuzo min kuna masu Sallamawa**)) [Suatul Naml; 31].

Kuma shine sanadiyar Rabuwar kai, da Jayayya, da Saɓani da Ƙiyayya; Allah Mai Tsarki Ya ce gameda Bani Isrãila:

﴿فَمَا ٱخْتَلَفُوٓا۟ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلْعِلْمُ بَغْيًۢا بَيْنَهُمْ﴾

((**Basuyi saɓani ba sai bayan da Ilimi yaje masu; saboda Zalunci a tsakaninsu**)) [Suratul Jãthiya: 17].

Kuma sanadiyarsa ne miyagun Ayukkan Bani Isrãila suka yi yawa ga Annabawansu tsakanin Ƙaryatawa da Kashewa:

﴿أَفَكُلَّمَا جَآءَكُمْ رَسُولٌۢ بِمَا لَا تَهْوَىٰٓ أَنفُسُكُمُ ٱسْتَكْبَرْتُمْ
فَفَرِيقًا كَذَّبْتُمْ وَفَرِيقًا تَقْتُلُونَ﴾

((**Shin ko yaushe wani Manzo yazo maku da abunda Rayukanku basu so ba sai kuyi Girman kai, ku ƙaryata wani sashe kuma ku kashe wani sashe**)) [Suratul Baƙara: 78].

Kuma yana daga cikin Siffofin Munafukai:

﴿وَإِذَا قِيلَ لَهُمْ تَعَالَوْا۟ يَسْتَغْفِرْ لَكُمْ رَسُولُ ٱللَّهِ لَوَّوْا۟ رُءُوسَهُمْ
وَرَأَيْتَهُمْ يَصُدُّونَ وَهُم مُّسْتَكْبِرُونَ﴾

((**Kuma idan akace masu: kuzo Manzon Allah zai nema maku Gafara sai su juyar da kawunansu kuma ka kagansu suna kangewa kuma suna masu Girman kai**)) [Suratul Munãfiƙun: 5].

Kuma an azabtarda Al’ummomi da suka gabata; saboda siffantuwarsu dashi; Allah Maɗaukaki Yace gameda Mutanen Nuhu:

﴿وَٱسۡتَغۡشَوۡاْ ثِيَابَهُمۡ وَأَصَرُّواْ وَٱسۡتَكۡبَرُواْ ٱسۡتِكۡبَارٗا﴾

((**kuma su lulluɓe da tufafinsu, kuma su doge** -kan laifi- **kuma sunyi Girman kai iyakar Girman kai**)) [Suratu Nuh: 7].

Kuma Yace gameda Mutanen Fir’auna:

﴿وَٱسۡتَكۡبَرَ هُوَ وَجُنُودُهُۥ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَظَنُّوٓاْ أَنَّهُمۡ إِلَيۡنَا لَا يُرۡجَعُونَ * فَأَخَذۡنَٰهُ وَجُنُودَهُۥ فَنَبَذۡنَٰهُمۡ فِي ٱلۡيَمِّۖ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلظَّٰلِمِينَ﴾

((**Kuma yayi Girman kai shi da Rundunoninsa a ban ƙasa bada haƙƙi ba kuma suka tabbatar da cewa lallai su baza’a mayar dasu zuwa gareMu ba * sai Muka kama shi da Rundunoninsa sai muka jefasu a cikin Kogi, sai ka dubi yadda ƙarshen Azzalumai ya kasance**)) [Suratul Ƙasas: 39-40].

Kuma Yace gameda Mutanen Hudu:

﴿فَأَمَّا عَادٞ فَٱسۡتَكۡبَرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَقَالُواْ مَنۡ أَشَدُّ مِنَّا قُوَّةًۖ أَوَلَمۡ يَرَوۡاْ أَنَّ ٱللَّهَ ٱلَّذِي خَلَقَهُمۡ هُوَ أَشَدُّ مِنۡهُمۡ قُوَّةٗۖ وَكَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا يَجۡحَدُونَ * فَأَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِمۡ رِيحٗا

صَرْصَرًا فِيٓ أَيَّامٍ نَّحِسَاتٍ لِّنُذِيقَهُمْ عَذَابَ ٱلْخِزْيِ فِي ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ وَلَعَذَابُ ٱلْءَاخِرَةِ أَخْزَىٰ ۖ وَهُمْ لَا يُنصَرُونَ﴾

**((Amma Ãdãwa sai sukayi Girma kai a cikin ƙasa bada wani haƙƙi ba, kuma suka ce, waye yafimu tsananin ƙarfi, Ashe basa ganin cewa lallai Allah wanda Ya hallicce su Yafi su tsananin ƙarfi kuma suka kasance gameda AyoyyinMu masu yin Musu ne ❋ Sai Muka aika akansu da wata Iska mai tsananin Sauti da Sanyi a cikin wasu kwanuka masu Shu'umanci; domin Mu ɗanɗana masu Azabar Wulaƙanci a cikin rayuwar Duniya, kuma Azabar Lahira tafi Wulaƙanci, kuma Su baza'a taimake su ba)). [Suratul Fussillat: 15-16].**

Masu Girman kai sune Maƙiyan Annabawa da Mabiyansu:

﴿قَالَ ٱلْمَلَأُ ٱلَّذِينَ ٱسْتَكْبَرُوا۟ مِن قَوْمِهِۦ لَنُخْرِجَنَّكَ يَٰشُعَيْبُ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مَعَكَ مِن قَرْيَتِنَآ أَوْ لَتَعُودُنَّ فِي مِلَّتِنَا﴾

**((Sai Manyan Mutane dasukayi Girman kai daga cikin Mutanensa suka ce: lallai tabbas zamu fitar da kai Ya Shu'aibu da waɗanda sukayi Imani tare da kai daga Alƙaryarmu; ko kuma lallai ku dawo a cikin Addininmu)) [Suratul A'arãf: 88].**

Kuma Musa –Aminci ya tabbata a gareshi- ya nemi tsarin Allah daga gare su, Allah Mai girma da ɗaukaka Ya ce:

﴿وَقَالَ مُوسَىٰٓ إِنِّي عُذۡتُ بِرَبِّي وَرَبِّكُم مِّن كُلِّ مُتَكَبِّرٖ لَّا يُؤۡمِنُ بِيَوۡمِ ٱلۡحِسَابِ﴾

((**Kuma Musa yace: lallai Ni ina neman tsarin Ubangajina kuma Ubangijinku daga duk Mai girman kai wanda baya Imani da ranar Hisabi**)). [Suratu Gãfir: 27].

Mai Girman kai mai biya ne ga son Ransa, yana kallon kansa da idon Kamãla amma yana kallon waninsa da idon Tawaya, an rufe Zuciyarsa, bata karɓa sai abunda take so:

﴿كَذَٰلِكَ يَطۡبَعُ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ قَلۡبِ مُتَكَبِّرٖ جَبَّارٖ﴾

**((Kamar haka ne Allah yake rufewa akan Zuciyar kowane Mai girman kai mai tsanantawa))** [Suratu Gãfir: 35].

Kuma Allah Maɗaukaki Yana Ƙinsa:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخۡتَالٖ فَخُورٖ﴾

((**Lallai Allah baYa son dukkan Mai Tãƙama Mai Alfahari**)) [Suratu Luqmãn: 18].

Wanda ya siffantu da girman kai abun juyarwa ne daga Izina da Wa’azantuwa da ababen Lura da Ayoyyi:

﴿سَأَصۡرِفُ عَنۡ ءَايَٰتِيَ ٱلَّذِينَ يَتَكَبَّرُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ﴾

((**ZaN karkatar da waɗanda suke yin Girman kai a ban ƙasa bada wani haƙƙi ba daga AyoyiNa**.)) [Suratul A’arãf: 146].

Kuma Mai girman kai daga gaskiya ana jarabtar sa da Miƙa wuya ga Ƙarya, kuma ana iya gaggauta masa

Azaba tun a Duniya; Hannun wani Mutum ya shanye a zamanin Annabi; saboda Girma kai; Salamatu ɗan Al-akwa' –Allah Ya yarda dashi- ya ce: «Lallai wani Mutum yaci da Hannunsa na Hagu a wurin Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- sai Annabi yace masa: **Kaci da Damanka**, sai yace: Bana iyawa, sai Annabi yace: **Bazaka iya ba**, ba abunda ya hanashi face Girma kai –Mai ruwayar Hadisin yace-: Daga nan bai sake kai Hannun zuwa bakinsa ba» [Muslim ya ruwaito shi], kuma haƙiƙa Ƙasa ta rufta da wani Mai girma kai; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Wani Mutum ya kasance yana tafiya a cikin wasu kaya Asin da Asin** –Kala ɗaya- **yana jin mamakin Kansa, ya taje gashin kansa; sai Allah Ya rufta shi a cikin Ƙasa, yanata fagamniya a cikin ƙasar har zuwa a ranar Ƙiyama**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma a ranar Lahira za'a yi masa Mu'amala da saɓanin nufinsa; duk wanda yake yiwa Mutan jiji da kai a Duniya; Mutane zasu tattaka shi da ƙafafunsu a Lahira, Almustapha –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Allah zai tada wasu Mutane a rabar Ƙiyama a cikin siffar Ƙwayar Zarra, Mutane zasu tattakasu da ƙafafunsu, sai ace: Su waye ne waɗancan a cikin siffar Ƙwayar Zarrah? Sai ace: Waɗancan Masu Girma kai ne a Duniya**» [Albazzãr ya ruwaito shi].

Mai Littafin Nawãdirul Usul yace a cikin littafinsa: «Duk wanda yafi tsananin Girman kai; zai kasance mafi gajarta a tsayi a Lahira, kuma haka nan abun yake ga duk

wanda yafi yawan ƙanƙan da kai ga Allah; shine zai fi ɗaukakar tsayi akan Hallittu», kuma duk wanda yake ɗauke da wani abu kaɗan na Girman kai; An haramta masa shiga Aljannah; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Wanda yake da misalin Ƙwayar Zarrah na Girman kai a cikin Zuciyarsa baya shiga Aljannah**» [Muslim ya ruwaito shi], kuma Wuta itace Gidansu:

﴿أَلَيْسَ فِي جَهَنَّمَ مَثْوًى لِّلْمُتَكَبِّرِينَ﴾

((**Ashe babu Mazauni a cikin Jahannama ga masu Girman kai**)) [Suratul Zumar: 60].

Kuma Annabi –Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Ashe bana baku labarin Ƴan Wuta ba? Kowane Mai kaushin Zuciya, Mai tara Dukiya da rowa da jiji da kai, Mai girman kai**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Wuta da Aljannah sunyi Jayya da juna da Hujjoji, sai wannan** –Wuta- **tace: Masu taurin kai da Girman kai ne suke shiga ta, sai wannan** –Aljannah- **tace: Masu rauni da Miskinai ne suke shigata**» [Muslim ya ruwaito shi].

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Girman kai yana daga cikin Abubuwan da Ubangijintakar Allah Ya keɓantu dashi ba'a Yi masa

(1) Yaku Musulmi.

jayayya a ciki, kuma duk wanda ya siffantu dashi daga cikin Hallittu; Allah Zai Azabtar dashi; a cikin Hadisin Ƙudsiy Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Allah Mai girma da ɗaukaka Yana cewa: Buwaya itace GyautoNa, kuma Girma kai shine Mayafi na; duk wanda yayi Jayayya daNi a cikin wani abu nasu Zan Azabtar dashi**» [Muslim ya ruwaito shi], kuma Allah Mai Buwaya da Ɗaukaka Shine Mai Girman kai; Allah Mai tsarki Yace game da KanSa:

﴿ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡجَبَّارُ ٱلۡمُتَكَبِّرُۚ﴾

((**Mabuwayi Mai tilas'tawa Mai Girman kai**)) [Suratul Hashr: 23].

Kuma Musulunci ya kiyaye sashen Girman kai da Ɗaukaka ga Allah, kuma ya haramta duk wata Hanya da take Jayayyar Ubangiji a cikin Girmansa; sai Musulunci ya hana saka Zinari da Hariri ga Namiji; saboda suna sanya Girman kai da Tãƙama, kuma ya gargaɗi Mai jan Izarinsa da Azaba; sai Annabi –Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- yace: «**Mutane Uku Allah baYa yi masu Magana ranar Ƙiyama, kuma baYa dubi zuwa gare su, kuma baYa Tsarkake su kuma sunada Azaba mai raɗaɗi,** yace: sai Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya maimaita wannan Maganar har sau Uku, sai Abu Zarrin yace: Sun tozarta kuma sunyi Hasara, su waye ne ya Manzon Allah? yace: **Mai jan Tufafi, da Mai Gori, da Mai sayar da Hajarsa da Rantsuwar Ƙarya**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma Musulunci ya hana kawar da kai da juyar da

sashen Fuska [Kunci] saboda Girman kai ga wasu, kuma baiyi Izini ga yin tafiyar jiji da kai da Alfahari ba a wurinda bana Yaƙi ba; Allah Mai girma da ɗaukaka yace:

﴿وَلَا تُصَعِّرْ خَدَّكَ لِلنَّاسِ وَلَا تَمْشِ فِي ٱلْأَرْضِ مَرَحًا ۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخْتَالٍ فَخُورٍ﴾

((**Kuma kada ka karkatar da Kuncinka ga Mutane, kuma kada kayi tafiya a cikin Ƙasa kana mai Faɗin rai, lallai Allah baYa son dukkan mai Taƙama, mai Alfahari**)) [Luqmãm: 18].

Kuma yayi hani daga  zurfafawa cikin tsara magana don ji da isa; Annabi –Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- ya ce: «**Kuma lallai daga cikin waɗanda nafi ƙi a cikinku kuma mafi nisanku daga Mazaunina a ranar Ƙiyama sune: Masu yawan Magana don fita daga gaskiya, da masu wuce iyaka wajen tsara magana, da Masu jujjuya Magana da bakinsu suna Alfahari da ita**» [at-irmizi ya ruwaito shi].

Don haka, ka yayewa kanka Mayafin Girman kai da Ƙasaita; domin banaka ne ba; su biyu ɗin na Mahallicci ne, kuma ka saka tufafin Sunkuyar da kai da Ƙanƙan da kai, wani abu na Girman kai ba zai taɓa shiga Zuciyar Mutum ba; face sai Hankalinsa ya rage gwargwadon abunda ya shiga na Girman kan koma fiye da hakan, kuma Asalin wannan shine, Jahiltar Bawa ga Ubangijinsa da kuma Jahiltar kansa, domin da ya san Ubangijinsa da Siffofin kamãla da ɗaukaka, kuma yasan kansa da Tawaya da Cututtuka, da bai yi Ji da kai ba kuma bai yi Girman kai ba; Sufyãn bin Uyainah –Allah Ya jiƙansa- yana cewa: «Duk wanda Saɓonsa na Girman

kai ne, lallai kaji masa tsoro; domin Iblisa ya saɓa ne yana mai Girman kai sai aka Tsine masa».

Kuma Azaba tana aukuwa ga wanda ya nutsa a cikin Zuciyarsa, kuma sauƙin Azabar da tsananinta tana kasancewa ne gwargwdon sauƙin Girman kan da tsananinsa, kuma wanda ya buɗewa kansa ƙofar Girman kai; ya buɗewa kansa ƙofofin Sharrori masu yawa, kuma wanda ya rufeta ga kansa; da Izinin Allah za'a buɗe masa ƙofofin Alkhairi masu Faɗi, kuma Girman kai wanda yake cin karo da Imani, Ma'abocinsa baya shiga Aljannah; kamar yadda yake a cikin faɗin Allah Maɗaukaki:

﴿ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَسۡتَكۡبِرُونَ عَنۡ عِبَادَتِي سَيَدۡخُلُونَ جَهَنَّمَ دَاخِرِينَ ﴾

((**Lallai waɗannan da suke yin Girman kai ga Bauta Min, da sannu zasu shiga Jahannama suna wulaƙantattu**)) [Suratu Gafir: 60].

Kuma daga cikin Girman kai akwai wanda yake cin karo da Imanin Wajibi, har Girman kansa ya haifar masa da inkarin Gaskiya da kuma rena Hallittu; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Duk wanda yakeda kwatankwacin ƙwayar Zarrah na Girman kai a cikin Zuciyarsa baya shiga Allah,** sai wani Mutum yace: Lallai Mutum yana son tufafinsa su kasance masu kyau kuma Takalminsa su kasance masu kyau, sai Annabi yace: **Lallai Allah mai kyau ne kuma yana son Kyau; Girman kai shine; yin watsi da gaskiya da kuma wulaƙanta Mutane**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma kada kayiwa kowa Alfahari; domin Duniyarka mai gushewa ce; Annabi –Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Haƙƙi ne akan Allah cewa, lallai bazai ɗaga wani abu na Dauniya ba face sai ya sauke shi**» [Bukhari ya ruwaito shi].

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

A cikin ƙanƙan da kai akwai samun ɗaukakar Duniya da Lahiral Annabi –Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Kuma ba wani wanda zai ƙanƙan da kansa ga Allah face sai Allah Ya ɗaukaka shi**» [Muslim ya ruwaito shi], kuma ƙanƙan da kai yana daga cikin Halayen Annabawa da kuma ɗabi'un Mutane masu Daraja; Annabi Musa –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ɗage Dutse ga wasu ƴan Mata guda biyu wanda Mahaifinsu tsoho ne sossai, kuma Annabi Dawud –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kasance yana ci daga abunda ya samu na aikin Hannunsa, kuma Annabi Zakariya –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kasance Kafinta ne, kuma Annabi Isah –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

﴿وَبَرًّا بِوَٰلِدَتِي وَلَمْ يَجْعَلْنِي جَبَّارًا شَقِيًّا﴾

**((Kuma Mai biyayya ne ga Mahaifiyata kuma bai sanya ni mai kaushin Zuciya taɓaɓɓe ba)).** [Maryam: 32].

Kuma «**Allah bai taɓa aiko wani Annabi ba face sai**

(1) Yaku Musulmi.

**yayi kiwon Dabbobi**», kuma Annabinmu –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kasance mai taushin Zuciya, mai tausayi mai saukar da fika-fukinsa ga Muminai, mai tausasawa a gare su, yana ɗaukar nauyin Mabuƙata, kuma yana bawa marashi, kuma yana taimako akan Musibobin zamani, ya hau Jãki kuma har ya goya wani akai, kuma yana yin Sallama ga ƙananan yara, kuma yana fara yin Sallama ga wanda ya haɗu dashi, kuma yana amsa kiran wanda ya gayyace shi koda zuwa ga Damtse ko Kofaton ƙafa ne, kuma lokacinda aka tambayi Aisha –Allah Ya yarda da ita- akan «Abunda Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yake yi a cikin Gida sai tace: Yana kasancewa ne a cikin Hidimar Iyalinsa, amma kuma idan lokacin Sallah yazo; sai ya fita zuwa Sallah» [Bukhari ya ruwaito shi].

Kuma ƙanƙan da kai sanadin Adalci ne da samun kusanci da ƙauna a cikin taron Jama'a, Annabi –Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- yana cewa: «**Kuma lallai Allah Yayi Wahayi zuwa gareni cewa ku ƙanƙar da kai har kada ɗaya yayi Alfahari ga ɗaya, kuma kada ɗaya yayi Zalunci ga ɗaya**» [Muslim ya ruwaito shi].

Zuciyar mai ƙanƙan da kai tana kasancewa mai saduda, mai saukar da fikafukin sauƙi da tausayi ga Bayin Allah, baya ganin cewa yanada wani haƙƙi akan wani, sai dai yana ganin cewa Mutane ne da Falala akansa, kuma Allah yana bada wannan Halin ne kawai ga wanda Yake so kuma Ya kusantar dashi kuma Ya karrama shi.

**Waba'adu Ayyuhal Muslimŭn(1):**

Mafi girman ƙanƙan da kai bayan na haƙƙin Allah shine: ƙanƙan da kai ga Iyaye; ta hanyar yi masu biyayya da girmama su, da kuma yi masu biyayya a cikin abunda ba saɓo ne ba, da kuma tausaya masu, da sakin Fuska a garesu, da tausasawa a cikin magana dasu, da girmama su da yawan Addu'a a gare su a rayuwarsu da bayan Mutuwarsu; Allah Mai girma da ɗaukaka Ya ce:

﴿وَٱخۡفِضۡ لَهُمَا جَنَاحَ ٱلذُّلِّ مِنَ ٱلرَّحۡمَةِ وَقُل رَّبِّ ٱرۡحَمۡهُمَا كَمَا رَبَّيَانِي صَغِيرٗا﴾

**((Kuma ka sassauta masu fika-fikan tausayawa na Rahama, kuma kace: Ya Ubangijina! Kayi musu Rahama kamar yadda suka reneni ina ƙarami)). [Isrã: 24].**

Kuma ƙin bin umurninsu da kuma yin kangara a garesu, da kuma ƙosawa da biyan buƙatocinsu; wani nau'i ne na Girman kai da kuma saɓa masu, ma'abocinsa abun yiwa gargaɗi ne da shiga Wuta.

Kuma ka ƙanƙan da kai ga Addini kuma kada kayi cin karo dashi da Ra'ayi ko son rai, kuma kada ka kawar da kai daga koyonsa da aiki dashi, kuma duk wanda yayi maka Nasiha; to, ka karɓa kuma ka godewa wanda yayi maka ita, kuma duk wanda ya umurceka da yin abun mai kyau ko ya haneka daga abun ƙi; lallai ka karɓi shiryarwarsa; lallai riba tana a cikin ƙanƙan da kai tana a cikin biyayya, Fudhail –Allah Ya jiƙansa- yana cewa: «Ƙanƙanda kai shine ka sauko ga Gaskiya kuma ka miƙa

(1) Bayan haka, Yaku Musulmi.

wuya gareta», kuma wani mutumi yacewa Malik bin Migwal: «Kaji tsoron Allah! Sai ya aza kuncinsa a kan ƙasa».

Kuma Malami da Almajiri suna ƙanƙan da kai ga juna tareda girmama Malami, kuma tabbas Shehin malaman Hadinsin nan: Abu Musa Almadeny –Allah Ya jiƙansa- ya kasance yana koyarda yara karatun Alƙur'ani a cikin Alluna tareda girman mastayinsa da matsayinsa maɗaukaki.

Kuma ka ƙanƙan da kai ga marasa lafiya ta hanyar kai musu Ziyara da tsayawa tare dasu da kuma yaye baƙin cikinsu, da kuma tunatar dasu neman Lada da yarda da kuma Haƙuri akan Ƙaddara, kuma ka tausasa sasaninka ga Mabuƙata da Miskinai, kuma ka lura da Fuskokin Faƙirai da Mabuƙata da masu kamewa daga roƙo da kuma jin Kunyar yin roƙon, kuma ka taimakesu daga dukiyarka, kuma ka ƙanƙanda kai a garesu a cikin matsayinka, Bishir bin Hãrith –Allah Ya jiƙansa- yana cewa: «Banga abunda yafi kyawun Mawadaci dayake zaune tsakanin Mabuƙata ba».

## Ina neman tsarin Allah daga Shaiɗan Jefaffe

﴿تِلْكَ ٱلدَّارُ ٱلْأَاخِرَةُ نَجْعَلُهَا لِلَّذِينَ لَا يُرِيدُونَ عُلُوًّا فِى ٱلْأَرْضِ وَلَا فَسَادًا ۚ وَٱلْعَٰقِبَةُ لِلْمُتَّقِينَ﴾

**((Wancan gidan Lahira muna sanya shi ne ga waɗanda basa nufin ɗaukaka a cikin ƙasa ko ɓarna, kuma ƙarshe mai kyau yana ga masu Taƙawa)).** [Suratul Ƙasas: 83].

Allah Yayi min Albarka tare daku a cikin Alƙur'ani mai girma...

## HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarSa da kuma Ni'imominSa, kuma ina shaida cewa lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Yabon Allah ya tabbata a gare shi da iyalansa da Sahabbansa.

**Waba'adu Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Allah Yana son ƙanƙan da kan Bawa ga umurninSa ta hanyar aiki dashi da kuma wurin Abunda ya hana ta hanyar nisantarsa, kuma ana samun ɗaukaka ne da ƙanƙan da kai da kuma saukar da kai ga Allah da kuma ƙanƙan da kai ga Musulmai, da kuma sauƙaƙawa a garesu, da juriya ga cutarwarsu da kuma Haƙuri dasu; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَٱخۡفِضۡ جَنَاحَكَ لِلۡمُؤۡمِنِينَ﴾

**((Kuma ka sassauta fikafikanka ga Muminai)) [**Suratul Hijr: 88].

Kuma tareda abunda ya gabata a haɗa da shagalantuwa da karatun Alƙur'ani da nazari a cikin Haddissai, tare da Halaye kyawawa da kyautatawa da kuma kamewa daga Cuta, da barin Giba da Gulma, kuma ka Mu'amalanci Mutane Mu'amala ta fifita wani akanka ba son kai ba.

---

(1) Bayan haka, Yaku Musulmi.

Kuma Mai ƙanƙanda kai shine wanda idan yaga wani; sai yace: wannan yafi ni Falala, Shafi'i –Allah Ya jiƙansa- Yana cewa: «Wanda yafi Mutane Matsayi shine; wanda baya kallon Matsayinsa, kuma mafi girman Falala daga cikin Mutane shine; wanda baya ganin Falalarsa», kuma idan Allah Yayi maka Baiwa da wata Ni'ima, to, ka fuskance ta da godiya da ƙanƙanda kai, Abdullahi binil Mubarak –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Ƙololuwar ƙanƙan da kai shine ka saukar da kanka wurin wanda yake ƙasa da kai a cikin Ni'imar Duniya, har ka ganar dashi cewa: Duniyar da kake da ita bata baka wata Falala ba akansa».

Sa'annan kuma kusani, lallai Allah Ya umurceku da yin Salati da Sallama ga AnnabinSa ...

# HASSADA[1]

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa, kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunan mu da miyagun Ayukkan mu, wanda Allah Ya shiryar dashi babu mai ɓatar dashi kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida lallai Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi Yabo da Aminci mai yawa a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Amma Ba'adu[2]:**

Kuji tsoron Allah -yaku bayin Allah- haƙiƙanin tsoro, kuma ku kiyaye Allah a cikin Sirrukanku da tattaunawarku.

**Ayyuhal Muslimŭn[3]:**

Kyautatuwar Gaɓɓai yana kasancewa ne da kyautatuwar Zuciya, kuma matsayin Ayukkan Zukata a cikin samun Lada da Uƙuba kamar Ayukkan Gaɓɓai ne,

---

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a Ashirin da biyar ga watan Swafar, Shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da Talatin da huɗu bayan Hijira.

(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

(3) Yaku Musulmi.

ana bada Lada akan Soyayya da Ƙiyayya don Allah, kuma ana yin Uƙuba akan Hassada da Alfahari da Riya.

Kuma gyaran Zuciya yafi Falala akan Ayukkan nafil-fili na Ibãdah, kuma Musulmi ba zai samu kamala ba face sai ta hanyar yaye abunda yake a cikin Zuciyarsa na Hassada da Ƙulli, kuma lafiyar Zuciya yana daga cikin Siffofin Annabawa; Allah Yana yabon BadaɗayinSa – Aminci ya tabbata a gareshi- Yace:

﴿إِذْ جَآءَ رَبَّهُۥ بِقَلْبٍ سَلِيمٍ﴾

**((A lokacin da yazowa Ubangijinsa da Zuciya lafiyayya))** [Suratus Saffãt: 84].

Kuma an tsaga Ƙirjin Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a garesa- har sau biyu; karo na farko a lokacin yarantarsa kuma aka fitar da wani gudan Jini daga gareshi, kuma aka ƙara tsagawa karo na biyu kafin ayi Isrã'i, kuma aka wanke Zuciyarsa a cikin wata Tãsa ta Zinari da ruwan Zamzam.

Kuma daga cikin Addu'ar Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yana mai koyarwa ga Al'ummarsa akwai: «**kuma Allah Ka shiryar da Zuciyata, kuma Ka daidaita Harshena, kuma Ka fitarda Ƙullin dake cikin Zuciyata**» [Abu Dawud ya ruwaito shi].

Kuma Allah Yayi yabo ga Ansãrawa saboda lafiyar Ƙirazansu:

﴿وَٱلَّذِينَ تَبَوَّءُو ٱلدَّارَ وَٱلۡإِيمَٰنَ مِن قَبۡلِهِمۡ يُحِبُّونَ مَنۡ هَاجَرَ إِلَيۡهِمۡ
وَلَا يَجِدُونَ فِي صُدُورِهِمۡ حَاجَةٗ مِّمَّآ أُوتُواْ﴾

**((Da waɗanda suka zaunar da gidajensu** –ga Muhajirai- **da kuma** –suka zaɓi- **Imani a gabanin zuwansu, suna son wanda yayi Hijira zuwa garesu kuma basa jin wata buƙata a cikin ƙirazansu ga abunda aka basu** -Muhajirai**))** [Suratul Hashr: 9].

Ma’na: abunda aka bawa ƴan uwansu Muhãjirai na daga Falala, kuma Ya bada labarin Mutanen kirki bayansu da faɗarsa:

﴿وَٱلَّذِينَ جَآءُو مِنۢ بَعۡدِهِمۡ يَقُولُونَ رَبَّنَا ٱغۡفِرۡ لَنَا وَلِإِخۡوَٰنِنَا ٱلَّذِينَ سَبَقُونَا بِٱلۡإِيمَٰنِ
وَلَا تَجۡعَلۡ فِي قُلُوبِنَا غِلّٗا لِّلَّذِينَ﴾

((**Kuma waɗanda suka zo bayansu suna cewa Ya Ubangijinmu Ka gafarta mana da ƴan uwanmu da suka gabacemu da Imani, kuma kada Ka sanya wani ƙulli a cikin Zukantan mu ga waɗanda sukayi Imani**)) [Suratul Hashr: 10].

Kuma yana daga cikin Sabubban shiga Aljannah; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi- yacema Sahabbansa –Allah Ya yarda dasu- «**Yanzu wani Mutum ɗan Aljannah zai bayyana a gareku**, sai wani Mutum daga cikin Ansãru ya bayyana, -sai suka tambaye shi akan aikinsa- sai yace: Ni bana jin wani ƙulli ga raina akan wani Musulmi, kuma bana Hassadar kowa akan wani Alkhairi da Allah Ya bashi» [Ahmad ya ruwaito shi].

Kuma Magabata sun kasance suna ƙoƙarin samun

lafiyar Zukatansu har aka siffantasu da hakan, Ibn Katheer yana siffanta Ibnul Qayyim –Allah Ya jiƙansu-sai yace: «Ya kasance mai kyawun Karatu da Halaye, mai yawan soyuwa ga Mutane; baya Hassadar kowa kuma baya cutar dashi kuma baya aibata shi kuma baya ƙullatar kowa».

Kuma ba abunda zai yi amfani a ranar Ƙiyama sai lafiyar Zuciya tareda Imani; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿ يَوْمَ لَا يَنفَعُ مَالٌ وَلَا بَنُونَ ۞ إِلَّا مَنْ أَتَى ٱللَّهَ بِقَلْبٍ سَلِيمٍ﴾

((**Ranarda Daukiya da Ƴaƴa basa amfani ⁕ face sai wanda yazowa Allah da Zuciya lafiyayya**)). [Suratul Shu'ara'i: 88-89].

Kuma Allah Mai tsarki ya ɗaukaka sashen BayinSa akan wani sashe a cikin Kyauta; saboda AdalcinSa da Falala; saboda Haƙurinsu ya bayyana da kuma godiyarsu; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَٱللَّهُ فَضَّلَ بَعْضَكُمْ عَلَىٰ بَعْضٍ فِى ٱلرِّزْقِ﴾

((**Kuma Allah Ya fifita sashenku akan sashe a cikin Arziki**)) [Suratul Nahl: 71].

Kuma Hassada Hali ce abun zargi kuma Siffa ce Maƙasƙanciya, wadda Mahassadi yake nufatar Ma'abota Falala da Ni'imomi da ita, Iblis ya siffantu da ita sai yaƙi yin Sujuda ga Adam; saboda Hassada a gare shi:

﴿ قَالَ أَنَا۠ خَيْرٌ مِّنْهُ خَلَقْتَنِى مِن نَّارٍ وَخَلَقْتَهُۥ مِن طِينٍ﴾

((**Yace: Ni nafi Alkhairi daga gare shi; Ka hallicce**

**ni daga Wuta, shi kuma Ka hallicce shi daga Lãka**)). [Suratul A’arãf: 12].

Sai Hassada ta kasance farkon Zunubi da aka fara saɓawa Allah da shi a cikin Sama, kuma tana daga cikin Siffofin Yahudawa da Nasãra; Allah Mai buwaya da ɗaukaka Ya ce:

﴿أَمْ يَحْسُدُونَ ٱلنَّاسَ عَلَىٰ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضْلِهِۦ﴾

((**Shin ko suna Hassadar Mutane ne akan abunda Allah Ya basu daga FalalarSa**)) [Suratun Nisa’i: 54].

Kuma tana daga cikin Maganganun Masu ciwon Zuciya; Allah Mai girma da ɗaukaka yace:

﴿فَسَيَقُولُونَ بَلْ تَحْسُدُونَنَا﴾

((**Kuma da sannu zasuce, A’a, kuna dai Hasadar mu ne**)) [Suratul Fat’hi: 15].

Kuma tana iya kai Ma’abocinta zuwa ga Kafircewa da Allah; Allah Mai buwaya da ɗaukaka Ya ce:

﴿إِلَّآ إِبْلِيسَ أَبَىٰ وَٱسْتَكْبَرَ وَكَانَ مِنَ ٱلْكَٰفِرِينَ﴾

((**Face sai Iblis yaƙi kuma yayi Girman kai kuma ya kasance daga cikin Kafirai**)) [Suratul Baƙarah: 34].

Kuma da itace wanda ba Musulmi ba yake burin fitar Ma’abota Musulunci daga Addininsu; Allah Mai buwaya da ɗaukaka Ya ce:

﴿وَدَّ كَثِيرٌ مِّنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ لَوْ يَرُدُّونَكُم مِّنۢ بَعْدِ إِيمَٰنِكُمْ
كُفَّارًا حَسَدًا مِّنْ عِندِ أَنفُسِهِم﴾

((**Dayawa daga cikin Ma’abota Littafi suna burin da sun mayar daku Kafirai bayan Imaninku; saboda Hassada daga Kawunansu**)). [Suratul Baƙarah: 109].

Kuma takan iya hana shiga cikin Musulunci; Al-Miswar bin Makhramah yacewa Abu Jahal: «Shin kun kasance kuna zargin Muhammad da Ƙarya kafin ya faɗi abunda ya faɗa? Sai yace: Na rantse da Allah, tabbas Muhammad ya kasance a cikinmu ana kiransa da Amini alhali yana saurayi, bamu taɓa kama shi da Ƙarya ba ko da ɗai, sai yace: To meye yasa bazaku binshi ba? Yace: Mu da Banu Hãshim munyi jayayyar Matsayi, sai suka ciyar muka ciyar, suka shayar muka shayar, suka bada Mafaka muka bada Mafaka, har sai bayan mun gurfana dasu akan gwiwowin mu, kuma mukayi kunnen doki da sai suce: Ga Annabi a cikinmu, yaushe ne zamu samu irin wannan? Na rantse da Allah bazamu yi Imani dashi ba, kuma bazamu gaskata shi ba har abada».

Kuma Mahassadi yakan iya kashe wanda yake yiwa Hassada; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَٱتۡلُ عَلَيۡهِمۡ نَبَأَ ٱبۡنَيۡ ءَادَمَ بِٱلۡحَقِّ إِذۡ قَرَّبَا قُرۡبَانٗا فَتُقُبِّلَ مِنۡ أَحَدِهِمَا وَلَمۡ يُتَقَبَّلۡ مِنَ ٱلۡأٓخَرِ قَالَ لَأَقۡتُلَنَّكَۖ﴾

((**Kuma ka karanta musu labarin Yayan Adam su biyu da gaskiya, yayinda suka bayarda Bakance, sai aka karɓa daga ɗayansu kuma ba’a karɓa daga ɗayan ba, yace: Lallai zan kasheka**)). [Suratul Mã’idah: 27].

Kuma Fitina ce ga Zukatan Mutane; Allah Mai buwaya da ɗaukaka Ya ce:

﴿وَكَذَٰلِكَ فَتَنَّا بَعْضَهُم بِبَعْضٍ لِّيَقُولُوٓاْ أَهَٰٓؤُلَآءِ مَنَّ ٱللَّهُ عَلَيْهِم مِّنۢ بَيْنِنَآۗ﴾

((**Kuma kamar haka ne Muka jarabci sashensu da sashe domin suce: Shin waɗancan ne Allah Yayiwa falala a tsakanin mu**)) [Suratul An'ãm: 53].

Ibn Rajab yace: «Hassada tana tabbace a cikin hallittar Mutum, kuma wanda ya rabauta shine wanda ya tunkuɗe ta daga kansa».

Kuma tana hana cikar kamalar Imani; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Kuma abubuwa biyu basa haɗuwa a cikin Zuciyar Bawa: Imani da Hassada**» [An-Nasa'i ya ruwaito shi], kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya tsoratar da Al'ummarsa daga wannan Cutar, sai yace: «**Kada kuyi Hassada da juna, kuma kada kuyi Ƙiyayya da juna, kuma kada ku yanke da juna**». [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Hassada Maɓuɓɓugar Sharri ce, kuma tana sanya yin Zalunci, kuma tana gadar da yankewa da juna, Ibn Aƙil –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Nayi nazari kan Halaye, sai nasamu cewa mafi tsananin matsalarsu itace: Hassada».

Kuma Mai Hassada yanada raunin Ruhi, kuma yana ganin girman kowace Ni'ima ga waninsa, yana ƙin Ni'imomin Allah ga Bayinsa, yana jin ciwon duk wata Falala da zata bayyana, ko wani matsayi da za'a yi godiya akai, idan yaga Ni'imar Allah ga Hallitarsa sai yayi baƙin ciki, kuma idan yaga gushewarta sai yaji daɗi, Mahassadi baya samun hutu; yana Murna da baƙin cikin Mutane, kuma yana baƙin ciki da farin cikinsu, baya ganin abunda Allah ya ƙaddara Adalci ne, kuma baya

ganin Ya cancanta Yayiwa Mutane Ni’ima, kuma Harshensa yana fito da duhun Zuciyarsa; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿أَمۡ حَسِبَ ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ أَن لَّن يُخۡرِجَ ٱللَّهُ أَضۡغَٰنَهُمۡ﴾

((**Ko kuwa waɗanda suke da cuta a cikin Zukatansu, suna zaton cewa Allah ba zai fitar da mugun ƙulle-ƙullensu ba)).** [Suratu Muhammad: 29].

Mu’awuya –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Kashedinka da Hassada! Domin -illarta- tana bayyana a gareka kafin ta bayyana ga Maƙiyinka», tana halakar da Ma’abocinta kuma ta kaishi zuwa ga Ƙasƙanci da Wulaƙanci; kamar yadda ya faru da ƴan uwan Yusuf lokacinda suka nemi Sadaka daga ɗan uwansau wanda sukayiwa Hassada. Suka ce:

﴿قَالُواْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡعَزِيزُ مَسَّنَا وَأَهۡلَنَا ٱلضُّرُّ وَجِئۡنَا بِبِضَٰعَةٖ مُّزۡجَىٰةٖ فَأَوۡفِ لَنَا ٱلۡكَيۡلَ وَتَصَدَّقۡ عَلَيۡنَآۖ﴾

((**Ya kai wannan Sarki, Cuta ta shafe mu da iyalinmu, kuma munzo da wata ƴar Hãja marar Ƙima, ka cika mana Ma’auni kuma kayi Sadaka a garemu**)) [Suratu Yusuf: 88].

Kuma daga cikin miyagun ɗabi’u babu mai Adalci kamar Hassada; Mahassadi yana Cutar da kansa da kansa kafin ya kai ga wanda yake yiwa Hassada, kuma duk wanda yaga yanayin Mahassadi da yake ciki na Damuwa, da Baƙin ciki da tsananin Ƙunci; lallai zai tausaya masa, kuma Mahassadi ya shiga abunda bai dame shi ba sai ya rasa abunda ya dame shi.

Hassada ɗaukaka ce ga wanda ake yiwa ita; domin rayuka basa hasadar kowa sai Mai girma, kuma Ni'ima nawa ce wadda take a ɓoye amma Mahassadi ya bayyanar da ita, kuma Bawa nawa aka yabe shi bayan anyi masa Hassada, Anyiwa Hãbila ɗan Adam Hassada amma sai ambatonsa ya wanzu, ana yabonsa a cikin Littafin Allah.

Kuma gwargwadon Falalar Mutum, da bayyanar Ni'imomin Allah a gareshi, gwargwadon yadda Hasadar Mutane take yawaita a gare shi, kuma mafi girman Ni'imar da za'ayiwa Mutum Hassada akanata itace; Ni'imar Musulunci; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿ وَدُّواْ لَوۡ تَكۡفُرُونَ كَمَا كَفَرُواْ فَتَكُونُونَ سَوَآءٗۖ ﴾

((**Kuma suna burin ace da zaku kafirta kamar yadda suka kafirta sai ku zamo dai-dai**)) [Suratu Nisa'i: 89].

Kuma anyiwa Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- Hassada akan Alƙur'ani:

﴿وَقَالُواْ لَوۡلَا نُزِّلَ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانُ عَلَىٰ رَجُلٖ مِّنَ ٱلۡقَرۡيَتَيۡنِ عَظِيمٍ﴾

((**Kuma suka ce da ace an sauko da wannan Alƙur'anin ne a akan wani Mutum mai girma daga cikin Alƙaryyun nan biyu**)) [Suratul Zukhruf: 31].

Kuma wanda akayiwa Hassada abun zalunta ne, kuma anyi masa umurni da yin Haƙuri da Taƙawa da Afuwa da kawar da kai; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَدَّ كَثِيرٌ مِّنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ لَوْ يَرُدُّونَكُم مِّنۢ بَعْدِ إِيمَٰنِكُمْ كُفَّارًا حَسَدًا مِّنْ عِندِ أَنفُسِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلْحَقُّ ۖ فَٱعْفُوا۟ وَٱصْفَحُوا۟ حَتَّىٰ يَأْتِىَ ٱللَّهُ بِأَمْرِهِۦٓ﴾

((**Dayawa daga cikin Ma'abota Littafi suna gurin da sun mayar daku Kafirai bayan Imaninku; saboda Hassada daga Kawunansu bayan da gaskiya ta bayyana a garesu, to, kuyi Afuwa kuma ku kawar da kai har sai Allah Yazo da Al'amarinsa**)). [Suratul Baƙarah: 109].

Kuma Yusuf –Aminci ya tabbata a gare shi- yacewa Yan uwansa:

﴿قَالَ لَا تَثْرِيبَ عَلَيْكُمُ ٱلْيَوْمَ ۖ﴾

((**Babu zargi akanku a yau**)) [Suratu Yusuf: 92].

Kuma ana kashe Wutar Mahassadi ce da kyautatawa a gare shi, kuma duk lokacin da Sharrin Mahassadi ya ƙaru; to, ka ƙara kyautatawa da kuma Nasiha da Tausayi akan shi, kuma Hassada tana hana cikar kamalar Imani; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Imanin ɗayanku baya cika har sai ya sowa ɗan uwansa abunda yake so ga kansa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Hassada saɓo ne wanda ya wajaba Musulmi ya tuba daga gare shi, kuma ya yarda da Hukuncin Allah, kuma ya miƙa wuya ga abunda aka ƙaddara, kuma kada yayiwa Allah jayyaya a cikin Al'amarinSa, kuma yayi Murna da Karamcin Allah ga BayinSa, kuma ya tunkuɗe

wannan saɓon daga Zuciyarsa; saboda yin biyayya ga Allah da kuma tsoron AzabarSa, kuma da nisantar faɗawa cikin ƙin Ni'imomin Allah ga BayinSa, kuma ya kalli wanda yake ƙasa dashi, kuma ya tuna Ni'imomin Allah a gare shi, kuma ya wadatu da kyautar da Allah ya bashi, kuma dukkanin Mahassadi shima abun Hassada ne, kuma ya nemi tsarin Allah daga Hassada, kuma ya gaggauta yin Addu'a ga wanda yake yiwa Hassada, kuma yayi fatan samun ƙaruwar Alkhairi ga ɗan uwansa Musulmi, kuma Wanda ya bawa ɗan uwanka wata Ni'ima mai iko ne akan ya baka irinta da fiye da ita:

﴿وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ﴾

((**Kuma Allah Mai Falala ne mai girma**)). [Suratu Baƙarah: 105).

Kuma kwaɗayin samun abunda wani yake akansa na Alkhairi da gasakiya yana kasancewa ne a cikin neman kyautar darajojin Lahira.

## Ina neman tsarin Allah daga Shaiɗan Jefaffe

﴿وَلَا تَتَمَنَّوۡاْ مَا فَضَّلَ ٱللَّهُ بِهِۦ بَعۡضَكُمۡ عَلَىٰ بَعۡضٖۚ﴾

((**Kuma kada kuyi burin abunda Allah Ya ɗaukaka sashenku akan sashe dashi**)) [Suratun Ni'sa'i: 32].

Allah Yayi min Albarka tare daku a cikin Alƙur'ani mai girma ...

## HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarSa da kuma Ni'imominSa, kuma ina shaida cewa lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya; don girmamawa ga Sha'aninSa, kuma ina shaida cewa lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Yabon Allah mai yawa ya tabbata a gare shi da iyalansa da Sahabbansa.

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Mafi soyuwar Zukata ga Allah itace: Mafi taushinta kuma mafi tsaftarta, kuma ba wata rayuwa mai daɗi wadda ta kai kamar ta Mumini mai lafiyayyar Zuciya; idan yaga wata Ni'imar da Allah ya bawa ɗan uwansa sai yayi Murna, kuma yaga Falalar Allah a cikin hakan, kuma ya ƙara ganin buƙatuwar BayinSa zuwa ga wannan Ni'imar, kuma ba wanda yayi adawa da Musulim yaci riba, kuma a cikin yarda da abunda Allah Ya raba akwai samun lafiya ga Zuciya, kuma duk lokacinda Bawa ya kasance yafi tsananin yarda; kuma a lokacin ne Zuciyarsa zatafi samun Aminci.

Kuma wajibi ne Mutum ya rinjayi kansa daga Halayenta abun suka, kuma ya katanganceta daga asalin ɗabi'arta mai muni datake da ita, kuma ginshiƙin abubuwan ake kare Zuciya daga gare su: Kwaɗayi, da Sha'awa, Fushi da Hassada.

(1) Yaku Musulmi.

Kuma wanda yake son Allah Yayi masa Ni'ima; to, kada ya juyar da ganinsa zuwa ga yanayin Mutane, kuma ya sanya Zuciyarsa ta kasance lafiyayya, kuma duk wanda yayi dubi zuwa ga Zunubansa; lallai zai girmama yawan abunda yake ciki na Ni'imomi, kuma wani Bawa bai taɓa kiyaye Ni'imar Allah a gare shi ba da iri godiya, kuma bai taɓa bijirota ga gushewa ba da irin saɓawa Allah da ita.

Kuyi tsere zuwa ga godiyar Ni'imominSa a gareku sai Ya ƙara maku daga FalalarSa, kuma ya baku kyauta daga Alkhairi wanda zaku samu jin daɗi dashi a Duniya da Lahira.

Sa'annan kuma ku sani lallai Allah Ya umurceku da yin Salati da Sallama ga AnnabinSa ...

# ZALUNCI[1]

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa, kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrin kawunan mu da munanan ayyukkan mu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa: lallai Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi Yabo da Aminci mai yawa a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Amma Ba'adu[2]:**

Yaku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro, kuma ku kiyaye Shi a cikin Sirrukanku da Tattaunawarku.

**Ayyuhal Muslimŭn[3]:**

Allah Ya hallicci Mutum kuma ya sanya ɗabi'u abun godewa a cikinsa, kuma Ya umurce shi da tafiya da kuma tabbatta akansu:

---

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a Ɗaya ga watan Swafar, Shekara ta Dubu ɗaya da Ɗari huɗu da Ashirin da Tara bayan Hijira.

(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

(3) Yaku Musulmi.

﴿فِطۡرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِي فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيۡهَاۚ﴾

((**Hallittar Allah wadda Ya hallicci Mutane akai**)) [Suratur Rũm: 30].

Kuma acikin Bawa akwai wasu Siffofi abun suka waɗanda Allah Ya umurce shi da yaƙar kansa da son ransa daga garesu, a cikinsu akwai wata ɗabi'a wadda idan ya miƙa ragamar kansa gareta ya Halaka:

﴿إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَظَلُومٞ كَفَّارٞ﴾

((**Lallai Mutum Mai yawan Zalunci ne kuma Mai yawan Kafircewa ne**)) [Suratu Ibrahim: 34].

Kuma lafiyayyar zuciya tana nisantar Zalunci da wuce iyaka, kuma tana siffantuwa da Adalci da Taƙawa, kuma tabbasa Allah Mahallicci –Mai Girma da Ɗaukaka- Ya tsarkake Kansa daga Zalunci kamar yadda Allah Mai Tsarki Yace:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَظۡلِمُ مِثۡقَالَ ذَرَّةٖۖ﴾

((**Lallai Allah baya Zalunci ko da Misalin ƙwayar Zarraha ce**)) [Suratun Nisa'i: 40].

Kuma ya sanya Zalunci a tsakanin BayinSa abun haramtawa, sai Yace: «**Yaku BayiNa! Ni na harmata Zalunci akaiNa, kuma Na sanya shi a tsakaninku abun haramtawa; kada ku Zalunci Junanku**» [Muslim ya ruwaito shi].

Zalunci yana amshe Haƙƙoƙi, kuma yana lalalata tarayyar Jama'a, yana danne Mai rauni, yana kawo Damuwa, yana halakar da gidaje, kuma dashi ne

Al'ummu da garuruwa suke rushewa, farkon Manzanni Nuhu –Aminci ya tabbata a gare shi- yayi Addu'a akan Azzalumai yace:

﴿وَلَا تَزِدِ ٱلظَّٰلِمِينَ إِلَّا تَبَارًۢا﴾

((**Kuma kada Ka ƙarawa Azzalumai komai sai halaka**)) [suratu Nuh: 28].

Kuma Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gares shi- ya kasance idan ya fita daga gidansa yana neman tsarin Allah daga Zalunci da faɗarsa: «**Da sunan Allah, Ya Ubangiji ina neman tsarinka kada na Zame, ko na ɓatar da wani, ko nayi Zalunci ko a Zalunceni, ko nayi aikin Jahilci ko ayi aikin Jahilci akaina**» [Ahmad ya ruwaito shi] kuma ya umurci ɗaya-ɗayan Al'ummarsa dasu nemi tsari da Allah daga gare shi, sai yace: «**Ku nemi tsarin Allah daga Talauci, da ƙarancin abun hanu, da Ƙasaƙanci da kuma kada kayi Zalunci kuma kada a Zalunceka**» [An-Nasa'i ya ruwaito shi], kuma ya hana Musulmai daga zaluntar Junansu sai yace: «**Musulmi ɗan uwan Musulmi ne; baya Zaluntar sa kuma baya Miƙa shi** –ga Maƙiya-» [Bukhari ya ruwaito shi].

Zalunci Shu'umin abu ne; domin ba'a zalunta sai mai rauni, Ibnul Jauziy –Allah Ya jiƙansa- yace: «Saɓon Zalunci yafi tsanani daga waninsa; domin mafi yawanci baya faɗawa sai akan mai rauni wanda baya iya neman Taimako», kuma Zalunci hali ne abun suka, yana hana Arziki ga Bayi:

﴿فَبِظُلۡمٖ مِّنَ ٱلَّذِينَ هَادُواْ حَرَّمۡنَا عَلَيۡهِمۡ طَيِّبَٰتٍ أُحِلَّتۡ لَهُمۡ﴾

((**Saboda Zalunci daga waɗanda suka zama Yahudawa Muka haramta akansu ababe daɗaɗa da aka hallatta masu**)) [Suratun Nisa'i: 160].

Kuma Zalunci koda a cikin ƙaramin abu ne, Uƙubarsa tana girmama; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gares shi- ya ce: «**Duk wanda ya ƙwace taƙi ɗaya na Ƙasa akan Zalunci, lallai za'a ɗora masa shi tun daga Ƙasa ta bakwai a ranar Ƙiyama**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma idan har Zaluntar Kyanwa yana shigarwa wuta; to, lallai Zaluntar Musulmi yafi Muni; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gares shi- ya ce: «**Wata Mata ta shiga Wuta sanadiyar wata Kyanwa data ɗaure ta; kuma taƙi ciyarda ita, kuma taƙi bari ta tafi taci daga Ƙwarin Ƙasa**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Al'ummomi suna kasancewa a cikin Aminci daga Azaba idan sukayi Imani kuma basuyi Zalunci ba; idan sukayi Zalunci zasu Halaka:

﴿وَتِلْكَ ٱلْقُرَىٰٓ أَهْلَكْنَٰهُمْ لَمَّا ظَلَمُوا۟﴾

((**Kuma waɗancan Alƙar'yyu Mun halakar dasu dasukayi Zalunci**)) [Suratul Kahaf: 59].

Kuma haƙiƙa Allah Ya gargaɗi Azzalumi kuma Yayi masa gargaɗi da Azaba mai raɗaɗi:

﴿ فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ مِنْ عَذَابِ يَوْمٍ أَلِيمٍ ﴾

((**Boni ya tabbata ga waɗanda sukayi Zalunci daga wata Azaba ta wani yini mai raɗaɗi**)) [Suratul

Zukhruf: 65].

Kuma Allah baya Shiryar da Azzalumi kuma baya Taimakonsa kuma baya Sonsa; Allah Mai buwaya da Ɗaukaka Ya ce:

﴿ وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴾

((**Kuma Allah baya son Azzalumai**)). [Suratu Ãli Imrãn: 57].

Azzalumi mai yankakken baya ne, baya barin ambato mai kyau a bayansa, kuma Ubangijinka yana nan yana jiransa, kuma ƙarshensa zuwa ga Halaka ne, kuma Uƙubarsa tana iya kasancewa a gaggauce –koda wanda aka Zalunta bai yi masa Addu'a ba-, kuma Azabarsa mai girma ce; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gares shi- ya ce: «**Ba wani Zunubi wanda ya cancanci Allah Ya gaggauta Uƙuba ga Ma'abucinsa a Duniya –tareda abunda ya tanada masa a Lahira- kamar Zalunci, da yanke Zumunci**» [at-irmizi ya ruwaito shi], kuma Allah Yana iya ƙyale shi, ba zai masa Uƙuba ba a Duniya; saboda yin Tãlala a gare shi, Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gares shi- ya ce: «**Lallai Allah Yana ƙyale Azzalumi, har idan Ya riƙeshi; ba zai taɓa kuɓuce maSa ba**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma ana lunka masa Zaluncisa a ranar Ƙiyama; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gares shi- ya ce: «**Lallai Zalunci Duhu bayan Duhu ne a ranar Ƙiyama**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Azzalumi bashida mataimaka kuma bashida

masu Ceto, kuma ba’a karɓar Uzurra daga gare shi, kuma zai yi fatan ya ceci kansa da duk abunda yake a cikin Ƙasa da irin abunda yake cikinta tareda shi don yasamu kuɓuta daga Azaba mai raɗaɗi:

﴿وَلَوْ أَنَّ لِلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ مَا فِى ٱلْأَرْضِ جَمِيعًا وَمِثْلَهُۥ مَعَهُۥ لَٱفْتَدَوْا۟ بِهِۦ﴾

((**Kuma da duk abunda yake a cikin Ƙasa da irinsa tareda shi na waɗanda sukayi Zalunci ne, da sun nemi Fansa dashi**)) [Suratul Zumar: 47].

Kuma idan wani Azzalumi ya jiɓinci wani Azzalumin a Duniya; to, ƙarshensu shine rabuwa da jayayya da juna, Allah Mai Buwaya da Ɗaukaka Ya ce:

﴿وَإِنَّ ٱلظَّٰلِمِينَ لَفِى شِقَاقٍۭ بَعِيدٍ﴾

((**Kuma lallai Azzalumai suna cikin rarrabuwa mai nisa**)). [Suratu Hajji: 53].

Shaikhul Islam –Allah Ya jiƙan shi- ya ce: «Mutane biyu bazasu taɓa haɗuwa akan Saɓo ba; face sai sun yi Jayayya», kuma Azzalumi baya taɓa jin daɗi da Zaluncinsa; harma ana Jarabtar sa da wanda yafi shi ƙarfin Zalunci sai ya buwaye shi:

﴿وَكَذَٰلِكَ نُوَلِّى بَعْضَ ٱلظَّٰلِمِينَ بَعْضًۢا بِمَا كَانُوا۟ يَكْسِبُونَ﴾

((**Kuma kamar haka ne Muke ɗora sashen Azzalumai akan sashe; saboda abunda suka kasance suna aikatawa**» [Suratul An’ãm: 129].

Kuma Allah da ƘarfinSa da IkonSa yana taimakon wanda aka Zalunta, kuma Ya sanya Addu’arsa karɓaɓɓiya ce; Annabi –Tsira da Amincin Allah su

tabbata a gare shi- ya ce: «**Addu'o'i guda uku karɓaɓɓu ne babu shakka a cikinsu: Addu'ar wanda aka Zalunta, da Addu'ar Matafiyi, da Addu'ar Mahaifi ga ɗansa**» [at-tirmizi ya ruwaito shi].

Al-Zabidiy –Allah Ya jiƙan shi- yace: «Wanda aka zalunta idan ya kai kukansa zuwa ga Allah; Adalcin Allah yana hukunta kama wanda ya Zalunce shi», kuma Addu'arsa bata da Shamaki a gabanta; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Kuma kaji tsoron Addu'ar wanda aka Zalunta; domin lallai ita batada wani shamaki tsakaninta da Allah**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], Ibnu Aƙeel –Allah Ya jiƙan sa- ya ce: «Ana karɓawa wanda Aka zalunta da wanda yake a cikin tsanani da sauri».

Wata Mata ta tuhumi Sa'ad bin Zaid –Allah Ya yarda dashi- akan Ƙarya, -wanda shi ɗaya ne daga cikin Mutane goma da akayiwa Bushara da gidan Aljannah-, ta tuhume shi cewa lallai shi ya kwace mata Fili sai yace: «Ya Allah idan ta kasance Maƙaryaciya ce; Ka makantar da ganinta, kuma Ka kasheta a cikin Filinta; kuma bata Mutu ba har saida ganinta ya tafi, sa'annan wata rana tana tafiya a cikin Filinta; sai ta faɗa a cikin wani Rame ta mutu» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma Ma'abota Gonan nan waɗanda Allah ya bada Ƙissarsu a cikin Suratul Ƙalam, lokacinda suka hana Mabuƙata haƙƙinsu; sai Allah Ya halakar da amfanin gonarsu:

﴿فَطَافَ عَلَيۡهَا طَآئِفٞ مِّن رَّبِّكَ وَهُمۡ نَآئِمُونَ * فَأَصۡبَحَتۡ كَٱلصَّرِيمِ﴾

((**Sai wani mai zagaye daga wurin Ubangijinka ya zagaya akanta** [ya ƙoneta] **alhali suna Bacci ⁕ Sai ta wayi gari** [baƙa ƙirin] **kamar Dare))** [Suratul Ƙalam: 19- 20].

Kuma duk wanda aka zalunta sai yayi Haƙuri; Allah zai ƙara masa ɗaukaka, Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Mutane guda Uku ina Rantsuwa akansu, kuma zan baku wani Hadisi ku hardace shi: Dukiya bata taɓa ragewa saboda Sadaka, kuma ba'a taɓa zaluntar wani Bawa da wani Zalunci kuma yayi Haƙuri akan haka ba face sai Allah Ya ƙara masa ɗaukaka, kuma Bawa ba zai buɗe ƙofar Roƙo ba face sai Allah Ya buɗe masa Ƙofar Talauci**» [at-irmizi ya ruwaito shi].

kuma Allah Yana yiwa wanda aka Zalunta Husuma a ranar Ƙiyama, kuma duk wanda Allah Yayi Husuma dashi lallai za'a ƙure shi; Annabi –Tsira da Aminci su tabbata a gare shi- ya ce: «**Allah Maɗaukaki Ya ce: Mutane uku Ni ne abokin Husumarsu ranar Ƙiyama: Mutumin da aka bawa** –Amana ko Aminci- **don Ni sai yayi Yaudara, da Mutumin da ya sayarda Mutum ƴantacce kuma ya cinye kuɗin daya sayar dashi, da Mutumin da ya ɗauki mai aiki kuma ya gama masa aikinsa amma kuma yaƙi biyansa Jingarsa**» [Bukhari ya ruwaito shi].

Kuma wanda aka zalunta baya shiga Aljannah har sai an cire masa haƙƙinsa daga wanda ya zalunce shi, kuma har sai Ransa yayi daɗaɗa; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Idan Muminai suka**

**kuɓuta daga Wuta; za'a tsaresu a wata gada dake tsakanin Aljannah da Wuta, sai su biya haƙƙoƙan da suka kasance tsakaninsu na Zalunci a Duniya**» [Bukhari ya ruwaito shi].

Kuma daga cikin Zalunci akwai: Hana Ma'aikata haƙƙoƙinsu, ko tauye haƙƙoƙin ko yin Jinkiri a bayarwa da su, Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Taurin bashin Mawadaci Zalunci ne**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma yana daga cikin Zalunci: Ta'adi akan Dukiyar wasu ko ƙwaceta ko cutar dasu a cikinta; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Duk wanda ya ƙwace taku ɗaya na Ƙasa akan Zalunci; lallai ranar Ƙiyama za'a ɗora masa shi tun daga Ƙasan bakwai**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma cin Dukiyoyin Marayu akan Zalunci yana daga cikin ababen da ke zama sanadin shiga Wuta:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ يَأۡكُلُونَ أَمۡوَٰلَ ٱلۡيَتَٰمَىٰ ظُلۡمًا إِنَّمَا يَأۡكُلُونَ فِي بُطُونِهِمۡ نَارٗاۖ﴾

((**Lallai waɗannan dasuke cin Dukiyoyin Marayu akan Zalunci, lallai kawai suna cin Wuta ce a cikinsu**)) [Suratun Nis'ai: 10].

Kuma tauyewar Mace ga haƙƙin Mijinta da inkarin kyautatawarsa, da kuma kai kuka akan abunda bai yi ba; Zalunci ne daga gareta zuwa gare shi; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Kuma kuna Kafircewa abokin zama**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Zaluncin Miji ga Matarsa, ko Tawayarsa a

gareta a cikin abunda Allah Ya wajabta a gareta na Haƙƙoƙi; Ta'adi a akanta, da kuma ƙin yin Adalci tsakanin Mata, da karkata zuwa ga ɗayarsu a cikin Rabo da Ciyarwa da abunda yayi kama dasu; Zalunci ne wanda akayi alƙawarin Azaba akansa; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Duk wanda yakeda Mata biyu sai ya karkate zuwa ga ɗayarsu, ranar Ƙiyama zai zo alhali sashen jikinsa ɗaya yana a karkace**» [Abu Dawud ya ruwaito shi].

Kuma Fifita sashen Yaƴa akan sashe a cikin Kyauta da waninta, ko Tawaya a cikin kula dasu da tarbiyarsu Zaluncin Uba ne a garesu; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Kuji tsoron Allah, kuma kuyi Adalci tsakanin Yaƴanku**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma daga cikin Zalunci akwai: Mahaifi ya hana Yarsa Aure, ko ya Aurar da ita ga wanda bai cancanceta ba; don kwaɗayin Dukiya ko waninta.

Kuma Malami ya gabatar da wani sashe na ɗalibansa akan wani sashe ba tare da Haƙƙi ba; Karkacewa ne daga Adalci, Shaikhul Islam –Allah Ya jiƙan sa- yace: «Kuma Hadisin «**Alƙalai kashi uku ne**» Malamin Yara yana shiga a cikinsa».

Kuma Cutar da Musulmi yana daga cikin mafi girman wuce iyaka; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Lallai yana daga cikin mafi girman manyan Zunubai: Mutum ya ci Mutuncin Mutum Musulmi batareda Haƙƙi ba**» [Abu Dawud ya ruwaito shi].

Kuma Hoto da nau'ukansa yana daga cikin Zaluntar Bawa ga kansa; Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Allah Mai Buwaya da Ɗaukaka Ya ce: Waye yafi girman Zalunci sama ga wanda ya tafi yana yin Hallita kamar HallitaTa? Suje su Hallicci Ƙwayar Zarrah mana, ko su Hallici Ƙwayar Hatsi, ko su Hallicci ƙwayar Sha'ir**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Mafi girman Zalunci shine Shirka da Allah; Allah Mai Buwayi da Ɗaukaka Ya ce:

﴿ إِنَّ ٱلشِّرۡكَ لَظُلۡمٌ عَظِيمٞ ﴾

((**Lallai Shirka Zalunci ce babba**)) [Suratu Luƙmãn: 13].

Kuma duk wanda ya kira wanin Allah, ko yayi Alwãshi ko Ɗawãfi ko Yanka ga wnin Allah ko Yayi rantsuwa da wanin Allah; lallai shi ya Zalunci kansa, kuma Wajibi ne a gare shi ya Tuba.

Kuma duk wanda ya zalunci waninsa; to, ya tuna Ikon Allah akansa, Allah Mai Buwaya da Ɗaukaka Ya ce:

﴿ وَلَوۡ يَرَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓاْ إِذۡ يَرَوۡنَ ٱلۡعَذَابَ أَنَّ ٱلۡقُوَّةَ لِلَّهِ جَمِيعٗا ﴾

((**kuma da waɗanda sukayi Zalunci zasuga lokacinda zasu ga Azaba kuma** –zasu tabbatar da- **lallai Ƙarfi na Allah ne baki ɗaya**)) [Suratul Baƙara: 165].

Kuma Allah yana karɓar Tubar Azzalumi idan ya Tuba kuma ya mayar da ababen da yayi zalunci akansu zuwa ga Ma'abotansu; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿ فَمَن تَابَ مِنۢ بَعۡدِ ظُلۡمِهِۦ وَأَصۡلَحَ فَإِنَّ ٱللَّهَ يَتُوبُ عَلَيۡهِۚ ﴾

((**Wanda ya Tuba bayan Zaluncinsa kuma ya gyara, to, lallai Allah Yana karɓar Tubarsa**)) [Suratul Mã'idah: 39].

Ibnul Qayyim ya ce: «Allah baya barin wani abu na Zaluncin Bayi sashensu ga sashe, kuma Allah zai fitar da haƙƙin kowa».

Kuma daga cikin Adalcin Allah: Lallai Bãyi ana cire masu haƙƙinsu daga wanda ya Zalunce su, har a tsakanin Dabbobi, Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Za'a bada Haƙƙoƙi zuwa ga ma'abotansu a ranar Ƙiyama har acirewa Akuya Marar Ƙaho haƙƙinta daga Mai Ƙaho**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma haƙiƙa Annabi –Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya umurci Azzalumi daya wanke kansa daga wanda ya Zalunta a Duniya kafin Hisabin Lahira; sai yace: «**Duk wanda yake da wani zalunci da yayiwa ɗan uwansa na Mutuncinsa ko wani Abu, lallai ya wanke kansa daga gare shi a yau; kafin** –ranar da- **babu Dinãri ko Dirhami; idan yanada aiki na ƙwarai sai a ɗauka daga ciki gwargwadon Zaluncinsa, idan kuma bashida aikin mai kyau sai a ɗauko daga Miyagun Ayyukan abokinsa** –wanda ya zalunta- **a ɗora masa akansa**» [Bukhari ya ruwaito shi].

Kuma ba'a gafarta Zaluncin Shirka sai da Tauhidi, kuma Wajibi ne a taimaki Azzalumi ta hanyar yi masa Nasiha; domin ya kame daga Zaluncinsa; Allah Yacewa Musa da Hãrun –Aminci ya tabbatta a gare su-:

﴿ٱذۡهَبَآ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ إِنَّهُۥ طَغَىٰ ۞ فَقُولَا لَهُۥ قَوۡلٗا لَّيِّنٗا لَّعَلَّهُۥ يَتَذَكَّرُ أَوۡ يَخۡشَىٰ﴾

((**Kuje zuwa ga Fir'auna lallai shi ya wuce iyaka ⁕ ku faɗa masa Magana mai taushi kila shi ya tunata ko yaji tsoro**)) [Suratu Ɗãha: 43-44].

Kuma hana Azzalumi daga Zaluncinsa taimakonsa ne; saboda kada Azaba ta kewaye shi, Annabi –Tsira da Aminci su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Ka taimaki ɗan uwanka yana Azzalumi ko wanda aka zalunta,** sai suka ce: Ya Manzon Allah! wannan muna taimakonsa idan yana wanda aka zalunta, yaya zamu taimake shi idan yana Azzalumi? Yace: **Ka kame Hannayensa**» [Bukhari ya ruwaito shi].

Kuji tsoron Allah, kuma ku kasance masu tsayuwa akan daidato da Adalci, ku nisanci Zalunci, kuma ku girmama Alfarmar Musulmai, ku mayarda abubuwan da kukayi zaluncinsu zuwa ga Ma'abotansu kafin ranar Hisãbi.

**Ina neman tsarin Allah daga Shaiɗan Jefaffe**

﴿وَمَن يَظۡلِم مِّنكُمۡ نُذِقۡهُ عَذَابٗا كَبِيرٗا﴾

((**Kuma duk wanda yayi Zalunci daga cikinku zamu ɗanɗana masa Azaba mai girma**)). [Suratul Furƙãn: 19].

Allah Yayi min Albarka tare daku a cikin Alƙur'ani mai Girma ...

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan Kyautatawarsa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarSa da kuma Ni'imominSa, kuma ina shaida cewa lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya; don girmamawa ga Sha'aninSa, kuma ina shaida cewa lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Yabon Allah da Aminci mai yawa ya tabbata a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Ayyuhal Muslimŭn[1]:**

Asalin kowane Alkhairi shine: Ilimi da Adalci, kuma Asalin kowane Sharri shine: Jahilci da Zalunci; kuma mafi Hankalin Mutane shine wanda yayiwa Hankalinsa Adalci daga son ransa, kuma daga cikin abunda yake taimakawa akan nisantar Zalunci akwai: Wadatar Zuci, da kiyaye Allah, da yawan Addu'a, kuma duk wanda yayi Adalci kuma ya kiyaye Ubangijinsa kuma yayi maSa biyayya; zai rayu yana Amintacce Mai natsuwa, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَمۡ يَلۡبِسُوٓاْ إِيمَٰنَهُم بِظُلۡمٍ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلۡأَمۡنُ وَهُم مُّهۡتَدُونَ﴾

((**waɗanda sukayi Imani kuma basu cakuɗa Imaninsu da Zalunci ba, waɗancan suna Aminci kuma sune Shiryayyu**)). [Suratul An'ãm: 82].

(1) Yaku Musulmi.

Kuma idan Bayi suka nisanci Zalunci kuma suka koma zuwa ga Allah da Tuba da Addu’a; Arziki da kyauta zai samesu.

Sa’annan kuma ku sani lallai Allah Ya umurceku da yin Salati da Sallama ga Annabin mu ...

# UƘUBAR AZZALUMI[1]

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa, kuma muna neman GafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrin kawunan mu da munanan ayyukkan mu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi kuma duk wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa: lallai Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah Yayi Yabo da Aminci mai yawa a gare shi da Iyalansa da Sahabbansa.

**Amma Ba'adu[2]:**

kuji tsoron Allah -Yaku bayin Allah-, haƙiƙanin tsoro; domin tsoron Allah shine hanyar Shiriya, kuma Saɓa mata shine hanyar Taɓewa.

**Ayyuhal Muslimŭn[3]:**

Allah Ya fifita Mutum kuma Ya Karrama shi, kuma Ya tanada masa sabubban samun Natsuwa; domin ya bautawa Allah Mai tsarki kamar yadda Ya umurta, kuma rayuwar Mutane bata tsayuwa sai da Addini, kuma dashi ne jin daɗinsu yake a Lahira, kuma daga cikin Addu'ar

---

(1) Anyi wannan Huɗubar ne a Masallacin Annabi, ranar Juma'a Talatin ga watan Rabi'ul Akir, Shekara ta Dubu ɗaya da Ɗari huɗu da Talatin da uku bayan Hijira.

(2) Bayan haka; kalma ce wadda ake amfani da ita domin ɗora zance bayan gabatar da Shimfiɗa.

(3) Yaku Musulmi.

Annabi –Tsira da Amincin Allah- akwai: «**Ya Allah ka kyautata min Addinina wanda shine yake Mallakar Al'amarina, kuma Ka kyautata min Duniyata wadda a cikinta Rayuwata take, kuma Ka kyautata min Lahirata wadda Makomata take a cikinta**» [Muslim ya ruwaito shi].

Kuma Ginshiƙin Addini shine: Adalci a cikin abunda yake tsakanin Bayi da Mahallicinsu ta hanyar kaɗaita shi da Ibadah, da kuma abunda yake tsakaninsu da Hallittu ta barin Zaluntar sashensu akan sashe; domin Zalunci shine Asalin kowane Sharri da Lalalcewar Addini da Duniya, kuma Allah Ya tsarkake kansa daga Zalunci kuma Ya sanya shi a tsakanin Bayi Haramtacce; sai yace: «**Yaku BayiNa! Ni na harmata Zalunci ga kaiNa, kuma Na sanya shi a tsakaninku abun haramtawa; kada ku Zalunci Junanku**» [Muslim ya ruwaito shi]. Kuma Abu Idris Alkhaulãni –Allah Ya jiƙansa-, -wanda shine ya ruwaito wannan Hadisin- ya kasance idan ya bada wannan Hadisin sai ya gurfana akan Gwiwoyinsa.

Kuma Allah Ya bada labarin cewa baya son Azzalumi, kuma ya kore samun Rabauta a gare shi, kuma Yayi Alƙawarin yanke bayansa, kuma ba wanda zai dawwamma akan Taimakonsa; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنۡ أَنصَارٖ﴾

((**Kuma Azzalumai basuda Mataimaka**)) [Suratul Ãli Imrãn: 192].

Harma ana ɗora wani Azzalumin da yafi shi ƙarfi akansa; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَكَذَٰلِكَ نُوَلِّي بَعۡضَ ٱلظَّٰلِمِينَ بَعۡضَۢا بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ﴾

((**Kuma kamar haka ne Muke ɗora sashen Azzalumai akan sashe; saboda abunda suka kasance suna aikatawa**)) [Suratul An’ãm: 129].

Ibn Katheer –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Ma’ana: Muna ɗora sashensu akan sashe, kuma muna halakar da sashensu da sashe, kuma muna Azabtar da sashensu da sashe; sakamako ga Zaluncinsu da kuma cutarwarsu».

Kuma Allah Ya kashedi da Makoma mai Muni; sai Yace:

﴿وَسَيَعۡلَمُ ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓاْ أَيَّ مُنقَلَبٖ يَنقَلِبُونَ﴾

((**Kuma da sannu waɗanda sukayi Zalunci zasu san wane irin Makoma ce zasu koma**)) [Suratul Shu’arã’i: 227].

Shuraihu –Allah Ya jiƙan sa- ya ce: «Lallai Azzalumi yana jiran Uƙuba, kuma wanda aka zalunta yana jiran Nasara».

Kuma kwanakinn Azzalumi a Duniya ƙidanyayyu ne, kuma Allah Yana masa Talala; Allah Maɗaukakin Sha’ani Ya ce:

﴿فَلَا تَعۡجَلۡ عَلَيۡهِمۡۖ إِنَّمَا نَعُدُّ لَهُمۡ عَدّٗا﴾

((**Kada kayi masu gaggawa, lallai kawai Muna masu wani tanadi ne Tanadi**)) [Suratu Maryam: 84].

Kuma duk wanda Ta’addancinsa ya tsawaita lallai Ikonsa zai gushe; Allah Mai girma da ɗaukaka Ya ce:

﴿وَكَمۡ قَصَمۡنَا مِن قَرۡيَةٖ كَانَتۡ ظَالِمَةٗ وَأَنشَأۡنَا بَعۡدَهَا قَوۡمًا ءَاخَرِينَ﴾

((**Kuma nawa ne daga cikin Alƙarya muka halakar da ta kasance Azzaluma kuma muka ƙago wasu Mutane na daban a bayanta**)) [Suratul Ambiya'i: 11].

Ibnul Qayyim –Allah Ya jiƙan shi- Yace: «Idan Allah Yayi nufin halakar da MaƙiyanSa da shafe su; sai ya samar masu sabubban dasuke wajabtar da Halakarsu da Shafesu, kuma daga mafi girman su –bayan Kafircinsu- akwai: Zaluncinsu da wuce iyakarsu, da kuma wuce iyaka a cikin cutar da Masoyansa da faɗa dasu da Yaƙarsu da kuma hawa kansu da Zalunci» .

Kuma Allah Ya ambaci Azzalumai a cikin LittafinSa kuma ya ambaci Munnin Ƙarshensu, kuma Ya bada labarin cewa Ya sakasu abun Lura ga waninsu; Fir'auna ya wuce iyaka kuma ya yaɗa ɓarna a cikin Ƙasa, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿إِنَّ فِرۡعَوۡنَ عَلَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَجَعَلَ أَهۡلَهَا شِيَعٗا يَسۡتَضۡعِفُ طَآئِفَةٗ مِّنۡهُمۡ يُذَبِّحُ أَبۡنَآءَهُمۡ وَيَسۡتَحۡيِۦ نِسَآءَهُمۡۚ إِنَّهُۥ كَانَ مِنَ ٱلۡمُفۡسِدِينَ﴾

((**Lallai Fir'auna yayi girman kai a cikin Ƙasa kuma ya sanya Ma'abotanta kashi-kashi, yana raunata wata tawaga daga cikinsu, yana yanke Ƴaƴansu kuma yana rayar da Matansu, lallai shi yankasance daga cikin Maɓarnata**)) [Suratul Ƙasas: 4].

harma ya wuce iyaka ga haƙƙin Ubangiji yayi inkarinsa, yace:

﴿أَنَا۠ رَبُّكُمُ ٱلۡأَعۡلَىٰ﴾

((**Ni ne Ubangijinku mafi ɗaukakaka**)) [Suratul Nãzi'ãt: 24].

Kuma yayi Alfahari da gudanar Ruwa ƙarƙashin Kafafunsa, kuma ya kasance yana cewa:

﴿أَلَيۡسَ لِي مُلۡكُ مِصۡرَ وَهَٰذِهِ ٱلۡأَنۡهَٰرُ تَجۡرِي مِن تَحۡتِيٓۚ﴾

((**Ashe Mulkin Misra ba nawa ne ba, kuma ga waɗannan Ƙoramu suna gudana a ƙarƙashina**)) [Suratul Zukhruf: 51].

Kuma Allah yana nan yana jiransa kuma Ya masa Talala  ne amma bai Manta shi ba; sai Ya gudanar da Ruwa a samansa kuma ya nutsar dashi da Ruwan, kuma a lokacin Halakar dashi Yace masa:

﴿فَٱلۡيَوۡمَ نُنَجِّيكَ بِبَدَنِكَ لِتَكُونَ لِمَنۡ خَلۡفَكَ ءَايَةٗۚ﴾

((**Yau zaMu tseratar da kai da jikinka; domin ka kasance Alama ga waɗanda suke bayanka**)) [Suratu Yunus: 92].

Kuma Allah Ya bada labarin cewa lallai haɗewar kumfan teku akan Fir'auna lokacin halakarsa abu ne mai ban tsoro, Allah Yace:

﴿فَأَخَذَهُ ٱللَّهُ نَكَالَ ٱلۡأٓخِرَةِ وَٱلۡأُولَىٰٓ * إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبۡرَةٗ لِّمَن يَخۡشَىٰٓ﴾

((**Saboda haka, sai Allah Ya kamashi: domin Azabar farko data ƙarshe * Lallai a cikin wannan akwai abun lura ga wanda yake tsoron Allah**)) [Suratul Nãzi'ãt: 25-26].

Kuma Shu'aib –Aminci ya tabbata a gare shi- ya kira Mutanensa zuwa ga Musulunci kuma ya hanasu daga zaluntar Mutane, kuma yace musu:

﴿ أَوۡفُواْ ٱلۡمِكۡيَالَ وَٱلۡمِيزَانَ بِٱلۡقِسۡطِۖ وَلَا تَبۡخَسُواْ ٱلنَّاسَ أَشۡيَآءَهُمۡ وَلَا تَعۡثَوۡاْ فِي ٱلۡأَرۡضِ مُفۡسِدِينَ ﴾

((**Ku cika Sikeli da Ma'auni da gaskiya kuma kada ku tawayewa Mutane abubuwansu kuma kada kuyi ɓarna a cikin ƙasa kuna masu Fasadi)) [**Suratu Hud: 85]. Sai sukayi Izgili dashi kuma suka ce masa:

﴿ أَصَلَوٰتُكَ تَأۡمُرُكَ أَن نَّتۡرُكَ مَا يَعۡبُدُ ءَابَآؤُنَآ أَوۡ أَن نَّفۡعَلَ فِيٓ أَمۡوَٰلِنَا مَا نَشَٰٓؤُاْۖ إِنَّكَ لَأَنتَ ٱلۡحَلِيمُ ٱلرَّشِيدُ ﴾

((**Shin Sallarka take umurtarka da cewa mubar abunda iayayenmu suke bautawa ko mubar aikata abunda kake so a cikin Dukiyarmu, lallai kai mai Haƙuri ne Shiryayye**)) [Suratu Hud: 87].

Sai Allah Ya aike musu da Wuta wadda ta ƙonesu kuma ta ƙone Dukiyoyinsu wadda suka samu da Zalunci; Allah Mai Tsarki Ya ce:

﴿ فَأَخَذَهُمۡ عَذَابُ يَوۡمِ ٱلظُّلَّةِۚ ﴾

((**Sai Azaba ta kamasu a ranar Girgije**)) [Suratul Shu'arã'i: 189]. Ma'ana: Wata irin Wuta mai ƙonewa wadda ta sauko akansu daga Sama:

﴿ إِنَّهُۥ كَانَ عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٍ ﴾ [الشعراء: **189**].

((**Lallai ta kasance Azabar yini mai girma**)).

[Suratul Shu'arã'i: 189].

Kuma Samudawa Zunubinsu tare da Shirka da suke yi ya kasance ne: Soke Dabbar da Allah ya saka masu ita a matsayin Mu'ujizah; sai Allah Ya aiko musu da wata irin Tsawa wadda ta tsits-tsinke Zukatansu, Shaikhul Islam – Allah Ya jiƙan sa- Ya ce: «Kuma duk wanda ya keta Hurumin Allah kuma ya rena ababen da Yayi Umurni, da ababen da Yayi hani, kuma ya soke BayinSa kuma ya zubar da Jininsu; lallai zai kasance ya fisu Tsananin Azaba».

Kuma idan Tsanani, da Bala'i, da Baƙin ciki, da Wahala suka auka ga Muminai; to, lallai Allah Mai Tausayi ne a cikin ƘaddarawarSa, Mai Hikima a cikin gudanarwarSa ga Al'ammura kuma Mai iko ne akan Taimakon BayinSa; sai dai Yana Jarabtarsu saboda HikimarSa; Allah Mai girma da Ɗaukaka Ya ce:

﴿ذَٰلِكَۖ وَلَوۡ يَشَآءُ ٱللَّهُ لَٱنتَصَرَ مِنۡهُمۡ وَلَٰكِن لِّيَبۡلُوَاْ بَعۡضَكُم بِبَعۡضٖۗ﴾

((**Wancan, da Allah Ya so da Ya bada Nasara akansu sai dai domin Ya jarabta sashenku ga sashe**)). [Suratu Muhammad: 4].

Kuma Shi Allah Mai Tsarki Mai Ƙarfi ne a cikin kariyarSa ga BayinSa; Allah Mai girma da Ɗaukaka Ya ce:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ يُدَٰفِعُ عَنِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْۗ﴾

**((Lallai Allah Yana bada kariya ga waɗanda sukayi Imani))** [Suratul Hajj: 38].

Ibn Katheer -Allah ya jiƙansa- ya ce: «Yana kariya ga

BayinSa –waɗanda suka Dogara gare Shi kuma suka koma zuwa gare Shi- Sharrin Masharranta da Kaidin Fãjirai, kuma Yana kiyeyesu kuma Yana kula dasu kuma Yana taimakonsu», kuma wannan Kariya tana kasancewa ne gwargwadon Imanin Bawa ga MasoyinSa; duk wanda Imaninsa ya ƙaru, to, Kariyar Allah a gare shi zata ƙara Ƙarfi; Ƙatãdah –Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Na rantse da Allah! Allah baya taɓa tozartar da Mutumin da ya kiyaye AddininSa».

Kuma Musulmi yana yin riƙo da Sabubban samun Nasara da ture Zalunci da Danniya da kyautata Zato ga Allah cewa lallai Allah zai taimake shi, da kuma Ƙudurce abunda SunayenSa da SiffofinSa suke nuni zuwa gare shi –Na Ƙarfi da Iko da Girma da Buwaya-, kuma da yin Imani da abunda yazo a cikin Alƙur'ani na Alƙawarin Allah na taimkon Muminai:

﴿وَكَانَ حَقًّا عَلَيۡنَا نَصۡرُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ﴾

((**Kuma taimakon Muminai ya kasance Wajibi ne akanMu**)) [Suratur Rŭm: 47].

Da Kuma yawaita Ibadah da Neman Gafara da komawa zuwa ga Allah; Allah Mai Tsarki Ya ce:

﴿إِن تَنصُرُواْ ٱللَّهَ يَنصُرۡكُمۡ وَيُثَبِّتۡ أَقۡدَامَكُمۡ﴾

((**Idan kuka Taimaki Allah** –AddininSa-, **Zai taimake ku kuma Ya tabbatar da Dugadiginku**)) [Suratu Muhammad: 7].

Da kuma samun natsuwa da tabbacin kusancin lokacin samun Mafita:

﴿ أَلَآ إِنَّ نَصۡرَ ٱللَّهِ قَرِيبٞ ﴾

((**Ku saurara, Lallai Taimakon Allah Kusa yake))** [Suratu: 214].

Kuma ya sakankance cewa lallai Dogaro ga Allah shine ginshiƙen Nasara:

﴿إِن يَنصُرۡكُمُ ٱللَّهُ فَلَا غَالِبَ لَكُمۡۖ وَإِن يَخۡذُلۡكُمۡ فَمَن ذَا ٱلَّذِي يَنصُرُكُم مِّنۢ بَعۡدِهِۦۗ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ﴾

((**Idan Allah Ya baku Nasara babu mai rinjayar ku, kuma idan ya wofintar daku, waye zai taimake ku bayanSa, kuma Muminai ga Allah ne suke Dogara**)) [Suratu Ãli Imrãn: 160].

Kuma Haɗuwar kai akan Gaskiya da barin Rarrabuwa; Ƙarfi ne akan Maƙiya; Allah Mai Girma da Ɗaukaka Ya ce:

﴿وَلَا تَنَٰزَعُواْ فَتَفۡشَلُواْ وَتَذۡهَبَ رِيحُكُمۡۖ﴾

((**Kuma kada kuyi Jayayya har ku raunana kuma Ƙarfinku ya tafi**)) [Suratu A’arãf: 46].

Kuma Haƙuri shine Mabuɗin Mafita, kuma buƙatuwarsa tana ƙara ƙarfi a lokacin saukar Jarabawoyi da Musibobi, kuma Addu’a itace mafi ƙarfin Makami akan Maƙiya; Manzon Allah –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce: «**Kuma kaji tsoron Addu’ar wanda aka zalunta; domin lallai ba tada wani Shamaki tskaninta da Allah**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi], Ibn Aƙeel –Allah Ya jiƙanSa- yace: «Ana karɓawa wanda aka zalunta da gaggawa».

Kuma Fata mai kyau Shiriyar Annabin mu –Tsira da Amincin Allah su tabbatta a gare shi- ce; Tabbas an yaƙe shi, an masa Ƙawanya, an masa Rauni, an Cutar dashi, an ƙulla masa Makirci da Kaidi, an fitar dashi, an saka masa Guba, anyi masa Sihiri, kuma ƴaƴansa Shida suka Mutu amma kuma ya kasance yana cewa: «**Kyakyawan Fata yana burgeni,** suka ce: Meye Kyakyawan Fata? Yace: **Kalma mai kyau**» [Bukhari da Muslim suka ruwaito shi].

Kuma Musulmi yana Sakankancewa da taimakon Allah, kuma Haramun ne a gare shi ya karkata zuwa ga Azzalumai; Allah Mai Tsarki Ya ce:

﴿وَلَا تَرْكَنُوٓاْ إِلَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ فَتَمَسَّكُمُ ٱلنَّارُ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِنْ أَوْلِيَآءَ ثُمَّ لَا تُنصَرُونَ﴾

((**kuma kada ku karkata zuwa ga waɗanda sukayi Zalunci sai Wuta ta shafeku kuma bakuda wani koma bayan Allah daga cikin Masoya sa'annan kuma baza'a taimakeku ba**)) [Suratu Hŭd: 113].

Kuma Allah da IkonSa Yana taimakon mai Rauni, ko da tsanani ya dabai-baye shi ko an tozartar da shi; Allah Mai Girma da Ɗaukaka Ya ce:

﴿وَٱللَّهُ غَالِبٌ عَلَىٰٓ أَمْرِهِۦ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعْلَمُونَ﴾

((**Kuma Allah mai rinjaya ne akan Al'amarinSa sai dai mafi yawan Mutane basu sani ba**)) [Suratu Yusuf: 21].

Kuma taimakon Allah ga Muminai yana kasancewa ne

kawai da Imani da Taƙawa, kuma Allah Mai Tsarki mai taimakon BayinSa ne koda Adadinsu da Tanadinsu kaɗan ne; domin Ƙarfi na Allah ne baki ɗaya; Allah Mai Tsarki Ya ce:

﴿كَم مِّن فِئَةٍ قَلِيلَةٍ غَلَبَتْ فِئَةً كَثِيرَةً بِإِذْنِ ٱللَّهِ﴾

((**Sau nawa ne Tawaga ƴar kaɗan ta rinjayi Tawaga mai yawa da Izinin Allah**)). [Suratul Baƙarah: 249].

Kuma Shi Allah Mai Tsarki Yakan taimakon BayinSa ba tareda Yaƙi ba –kamar yadda ya faru a Yaƙin Ahzãb-; Allah Mai Girma da Ɗaukaka Ya ce:

﴿وَرَدَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ بِغَيْظِهِمْ لَمْ يَنَالُوا۟ خَيْرًا ۚ وَكَفَى ٱللَّهُ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٱلْقِتَالَ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ قَوِيًّا عَزِيزًا﴾

((**Kuma Allah Ya mayar da Kafirai da fushinsu basu samu Alkhairi ba, kuma Allah Ya isarwa Muminai Yaƙi, kuma Allah Ya kasance Mai Ƙarfi Mabuwayi**)). [Suratul Ahzãb: 25].

Kuma Allah Yakan iya taimakonsu da jefa Tsoro a cikin Zukatan Maƙiya –Kamar yadda ya faru ga Yahudawan Banin Nadheer-; Allah Maɗaukaki Yace:

﴿مَا ظَنَنتُمْ أَن يَخْرُجُوا۟ ۖ وَظَنُّوٓا۟ أَنَّهُم مَّانِعَتُهُمْ حُصُونُهُم مِّنَ ٱللَّهِ فَأَتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِنْ حَيْثُ لَمْ يَحْتَسِبُوا۟ ۖ وَقَذَفَ فِى قُلُوبِهِمُ ٱلرُّعْبَ ۚ﴾

((**Bakuyi zaton zasu fita ba kuma sun tabbatar da cewa Ganuwowinsu zasu tsare su daga Allah sai Allah Yazo masu ta inda basuyi tsammani ba kuma Ya jefa tsoro a cikin Zukatansu**)) [Suratul Hashr: 2].

Kuma Yakan iya aiko da wasu Rundunoni daga wurinSa; domin su halakar da masu wuce iyaka; Abrahata yazo da Runduna daga Yaman; domin rusa Ka'abah yana tare da mafi ƙarfin Dabbobi –Giwa-; sai Allah ya ɗora akansa mafi Raunin Dabbobi –Tsuntsaye-, kuma ya sanya Makircinsu a cikin Ɓata.

Kuma idan aka samu waɗanda aka kashe da jin Rauni a cikin Musulmi –Kamar yadda ya faru a Uhud-; to, lallai ƙarshe mai Kyau nasu ne, Allah Mai Tsarki Ya ce:

﴿فَٱصۡبِرۡۖ إِنَّ ٱلۡعَٰقِبَةَ لِلۡمُتَّقِينَ﴾

((**Kayi Haƙuri, lallai ƙarshe mai kyau na masu Taƙawa ne**)) [Suratu Hud: 49].

**Wa'ba'adu, ayyuhal Muslimun[1]:**

koda an raunanar da Musulmi lallai sune abun taimako, kuma idan aka yãke su, sune masu Galaba, kuma koda an tarwatsa su, sune abun ƙarfafawa, kuma ba wanda ya dogara ga Allah aka tozarta shi, kuma ba wanda ya laɓe zuwa gare Shi face sai an taimake shi.

**Ina neman tsarin Allah daga Shaiɗan jefaffe**

﴿وَنُرِيدُ أَن نَّمُنَّ عَلَى ٱلَّذِينَ ٱسۡتُضۡعِفُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَنَجۡعَلَهُمۡ أَئِمَّةٗ وَنَجۡعَلَهُمُ ٱلۡوَٰرِثِينَ ۝ وَنُمَكِّنَ لَهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَنُرِيَ فِرۡعَوۡنَ وَهَٰمَٰنَ وَجُنُودَهُمَا مِنۡهُم مَّا كَانُواْ يَحۡذَرُونَ﴾

((**Kuma muna nufin Muyi Ni'ima ga waɗanda aka**

(1) Bayan haka; Yaku Musulmai.

**raunanar a cikin Ƙasa kuma Mu sanyasu Jagorori kuma Mu sanyasu magada ❋ kuma Mu tabbatar dasu a cikin Ƙasa, kuma Mu nunawa Fir'auna da Hãmãna da Rundunoninsu abunda suka kasance suna tsoro daga garesu**)). [Suratul Ƙasas: 5-6].

Allah Ya sanya min Albarka tare daku a cikin Alƙur'ani mai Girma ...

## HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan Kyautatawarsa, kuma godiya ta tabbata a gareShi akan datarwarSa da kuma Ni’imominSa, kuma ina shaida cewa lallai babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake bashida abokin tarayya; don girmamawa ga Sha’aninSa, kuma ina shaida lallai Annabin mu Muhammad BawanSa ne kuma ManzonSa ne, Yabon Allah da Aminci mai ƙaruwa ya tabbata a gare shi da iyalansa da Sahabbansa.

**Ayyuhal Muslimŭn**[1]**:**

Tarihi cike yake da Wa’azozi da ababen Lura, kuma cike yake da ababen dasuka faru da Ƙissoshi, kuma a cikin sanin yanayin Al’ummomi da kuma ƙarshen Azzalumi da Azzalumai akwai abun Lura ga masu Hankali, kuma mai Arziki shine wanda ya wa’azantu da waninsa.

Kuma Tarihin Maɓarnata da kuma ƙarshen Azzalumai da kuma makomar masu laifi; abun Lura ne ga wanda yasan Allah haƙiƙanin sani, kuma yayi Imani da cewa lallai Shi mai Iko ne akan komai; Allah Mai Girma da Ɗaukaka Ya ce:

﴿ فَكُلًّا أَخَذْنَا بِذَنۢبِهِۦ ۖ فَمِنْهُم مَّنْ أَرْسَلْنَا عَلَيْهِ حَاصِبًا وَمِنْهُم مَّنْ أَخَذَتْهُ ٱلصَّيْحَةُ وَمِنْهُم مَّنْ خَسَفْنَا بِهِ ٱلْأَرْضَ وَمِنْهُم مَّنْ أَغْرَقْنَا ۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظْلِمَهُمْ وَلَٰكِن كَانُوٓا۟ أَنفُسَهُمْ يَظْلِمُونَ ﴾

(1) Yaku Musulmi.

((**Saboda haka, Mun riƙi kowanne da Zunubinsa, daga cikinsu akwai wanda Muka aikewa iskar tsakuwa akansa, kuma daga cikinsu akwai wanda Tsawa ta kama shi, kuma daga cikinsu akwai wanda Muka birkice Ƙasa dashi, kuma daga cikinsu akwai wanda Muka nutsar, kuma Allah bai kasance yana zaluntarsu ba sai dai sune suka kasance suna zaluntar kansu**)). [Suratul Alkabut: 40].

Kuma ƙarshen kowane Zalumci komai tsayon lokaci yana tafe, kuma Nasara tana tare da Haƙuri, kuma Mafita tana tare da Baƙin ciki, kuma Sauƙi yana biyowa bayan Tsanani; Allah Mai Tsarki Ya ce:

﴿فَإِنَّ مَعَ ٱلْعُسْرِ يُسْرًا ۞ إِنَّ مَعَ ٱلْعُسْرِ يُسْرًا﴾


((**Lallai tare da Tsanani akwai wani Sauƙi ⁕ Lallai tare da Tsanani akwai wani Sauƙi**)). [Suratul Inshirãh: 5-6].

Sa'annan kuma kusani, lallai Allah Ya umuceku da yin Salati da Sallama ga AnnabinSa ...

# JADAWALIN ABUBUWAN DAKE CIKI

**Gabatarwa**........................................................4
Halaye abun Yabo ................................................6
Kiyaye Harshe ......................................................7
Gaskiya ..............................................................27
Godiya akan Ni’imomi .........................................42
Kyawawan Ɗabi’u ................................................58
Haƙuri da Natsuwa ...............................................68
Karamci ...............................................................90
Cika Alƙawari ......................................................92
Rahama ..............................................................104
Kunya Alkhairi ce dukkanta ...............................121
Halayen Abun Suka ............................................136
Girman kai .........................................................137
Hassada .............................................................155
Zalunci ..............................................................168
Uƙubar Azzalumi ...............................................183
Jadawalin Abubwan dake ciki ...............................199

Mu'assasatu Ɗalibil Ilmi: domin yaɗawa da rabawa,
00966506090448




Littafan da suka fito kasuwa na mawallafin


JERANGIYAR DAGA HUƊUBOBIN MASALLACIN ANNABI



**Rukunnan Musulunci**



**TAUHIDI**



**Rukunnan Imani**



**Annabi ﷺ da sahabbansa**